💫MATAN??? Ko MAZAN???💫

✍🏻M SHAKUR

Chapter 1- FEMINISM

DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAIJINKAI.

Note: Wannan littafin kagaggen labari ne ba rayuwan wata ko wani narubuta ba, is just fiction danai highlighting major issues dake kawo misunderstanding a aure, I hope we all read and learn.
🙏

EPISODE1️⃣
Zaune suke akan kujerun dake cikin garden din yahuza suya na bayan central mosque. Maza hudu ne, dukansu suna sanye da suit but duk sun ciccire jacket din sun makala jikin kujerun dasuke kai da alamun daga wajen aiki suke, gasassun kaji ne agabansu da shayi sunasha suna kallon katon TV dake wajen inda ake buga kwallo tsakanin Manchester da chealsea. Kana ganinsu kasan suna bala'in enjoying match din dan sai gardama suke suna dariya kyakyakya.
Wayan daga daga cikinsu ne yay kara hakan yasa yakai hannunshi yataba aljihun gaban riganshi batare daya janye idanunshi dagakan TV ba yaciro wayan yajanye kanshi daga TV yakalli screen din ganin Madam yasa yadanyi tsaki ya ijiye wayan yacigaba da ringing sauran mazan dayake zaune dasu suka kalleshi dan yake yayi yakai hannunshi yana shafa kirjinshi yace "Madam ce wlh ke kirana tahanani sukuni" dauke kansu duka sukai daga kallonshi kaman hada baki suka cigaba da kallon match din abinsu.

Karfe 11:30 daidai aka gama match din inda Manchester sukaci da 4:2, wanda aka kira dazune yatashi yana daukan wayanshi dake ringing har lokacin da jacket nashi duka ya rike a hannu yace "lemme be on my way, inba hakaba Madam zata kashemini batteryn waya wlh, saida safen ku" daya daga cikin ukun dasuka rage zaune shima yamike dasauri yace "nima gani biye dakai Engineer bazan iya da masifan matan nan this night ba tahanani bacci nima" yana maganan yadauki jacket nashi da car key yabi Engineer dasauri zuwa wajen dasukai parking cars dinsu, sake sallama sukayi kowanne ya shige motarshi suka bar wajen.

Daya daga cikin biyun dasuka rage zaune ne yakalli dayan yace “karfe nawa zaka bar nan Nura?” juyawa wanda aka kira da Nura yayi kaman bashi akama magana ba yadaga hannunshi sama yakira daya daga cikin yaran dake aiki a Yahuzan da gudu gayen dayakira yazo cike da girmamawa yace ”yallabai gani” juyawa Nuran yayi yakalli mutumin dake kusadashi yace “ya akaro dakai ko zaka wucene kaima?” girgizamai kai yayi alamun a’a hakan yasa Nuran yajuyo yakalli yaron yace “karo mana shayin goruba da kaza asaka masa aciki da gizzard, kasa yaji separately bancin yaji sosai" wucewa yaron yayi yatafi Nura yadauki wayanshi zai fara tabama Musa yace “wai har yanzu kaida Hadiza baku shiryaba? Kai to kasauke girman kanka ka nemeta kuyi sulhu mana” tabe baki Nura yayi yace “wlh ko zan mutu bazan lallashi yarinyar nan ba cus nagaji, any little misunderstanding wanda daga wajetane fa yake farawa amman kullum nike neman sulhu akan wani dalili? She keep taking advantage of rashin son hayaniya na, yo bansan ciwon kaina bane aka gayamata?” Dasauri Musa yace “haba abokina kaima kasan mata da fish brain biyemata zakayi” dasauri Nura yace “bazaka gane bane, duk yanda zan suffanta maka Hadiza bazaka ganeba, she’s so bossy, tanada mentality dinnan na feminism, gani take dani da ita daidai muke shoulder to shoulder, she feels irin india kinada kudinki babu shit din da namiji zai kawomiki kidauka, you don’t need him for anything, she don’t care about me one bit billahillazi kaman ba aurenta nake ba” dafashi Musa yayi yace “chill please kodan yaranku ku shirya haba, Aman is just 4,5yrs ina, little Amal kuma 2 please banson yara tun suna kanana su taso suna ganin iyayensu basa shiri kaji Nura” kabar da hannunshi daga kafadanshi Nura yayi yace “enough Man, talking to Hadiza is impossible, barni nima nabita nazama fish din but saidai ni bazan zama sardine irinta ba mara hankali dake karewa a gwangwani ba, dan trust me mentality feminism nata nan is taking her nowhere, wlh saina gwadamata bonu duk randa takaini bango yar durun uwa” ya kifo uban ashar da hausan shi haba Musa ya kwashe da dariya, dan dariya Nura yayi shima yace “kaikuma meya faru kaima kabiye mini dayin dare awaje yau dan is obvious kaima da naka guntun matsalan kaima” dan tsaki Musa yayi yana tsaida dariyan dayake yace “matata, kaga Maman Shatu I don’t even know idan mace ce ita dan at this point cewa nake anya ba namiji bace itaba kuwa” dan dariya Nura yayi daidai lokacin ana kawo musu ordersu yaron ya ijiye yawuce yatafi, tsiyaya musu shayin Musa yayi yadauki kopin yakai baki yadan kurba ya tsaya kaman mai tunani yace “Bro imagine fa duka duka yanzu fa na shiga 45yrs amman this woman na neman maidani tsohon dole, she hates anything tarayya dani, dazaran nazo saita fara ni bansan yakamata yanzu na soma rage kwanciyan aure da itaba nasomas tsufa, menene menene, wai is high time mufara hakura dayi yara sun girma, Shatu is 16 zata shiga university next month let’s just focus on yaranmu, I was like what da hell! An gayamata ni katako ne ko sotake da tsufana nafara sopy”? Bushewa da dariya Nura yayi harsaida ya yarda naman bakinshi kasa yana nema ya kware, Musa yace “kadaina dariya is a serious matter ni da kai munada banbanci, kai daman bakin zuciyanka da girman kanka bazai barka kanemi Hadiza ba I don’t even know yanda kake surviving wlh, niko bazan iyaba kullum da rokon Allah nake hada matan nan kafin tabari indan taba, da girmana da darajata Maman Shatu ta maidani maibara shine fa jiya tamini karatun Alam Nashara matan nan atafaufau tahanani wai munada budurwa mudaina yi” dariyan da Nura keyi saida yan wasu table suka juyo suna kallonsu dasauri yarage sautin dariyan, kwana nawa kenan kullum cikin kunci yake but yau Musa nabashi dariya sosai wlh he’s so funny and hausan shi is just everything, dole ma kai understanding pains nashi sabida kalamomin dayake using to express it, tsagaita dariyan

yayi yadauki nama yakai baki yace “to be honest with you Musa bawai banson nasami natsuwa bane ina so sosai but halinta is making me loose interest and love for her, banmason in tuntubeta da neman kwanciyan aure, itakuma ko oho bata damu dani ba, she no send me fa” cike da takaici Musa yace “I don’t know yaya brain din mata ke aiki imagine fa sun mana laifi but idan sun taru cikinsu they will belike mijina yamin kaza kaza kaza kaga ana kaimu online ana please hide my ID akai karanka amman baza su taba fadin suga kaza kaza da sukema mazajensu ba bunch of hypocrites, masu fuska biyu kawai, banda gayu da nunama kawayensu suna more mazajensu da aurensu babu abinda suka iya, ita kuma dama nafada mata idan bata chanza ba wlh she is on her own, daleliyar kishiya zanyo mata, da kudina da sana’ata wlh bama saina nemi mata ba Gwaggo zan kira a kano asamomin yarinya yar achan achan atoh ni wlh ban tsufaba garau nake, anma kawomin wasu magungunan basir daga Cotonou bazaka sha ba”? Girgixa kai Nura yayi yace “kaidai da shaye shayen magungunan basir din nan” dariya Musa yayi yace “kaima yakamata kasha wlh ya wanke maka mara tastas, fire for fire wlh ka lallasa Hadiza” “inaaa ni bazan biyemaka ba narasa ina zansa kaina, baridai maybe idan komi ya daidaita nazo na amsa”.
Wuraren 1.30AM sukatashi Nura yabiya kudin komi, kowanensu yashiga mota dan tafiya gida, Musa yace “zakazo office kaduba motocin ne gobe sun iso fa” Gyadamai kai Nura yayi yace “inada wani important meeting gobe but zan shigo dazaran nagama” Musa yace “to shikenan nimafa sonake nazo naga site dinnan, terrace dinnan yamin kyau dakukayi” “ba kaki sayaba bakano da son kudi” ckin dariya sosai da barkwanci Musa yace “shikuma bazamfare annubazaranci da kudi, nabiye maka saika karan mini da dan jarin motoci na” dariya dukansu sukai sukai sallama kowa yaja motanshi sukabar wajen.
Kinason magana dani M shakur??? Chat me up by clicking on this link
wa.me/+2347012181461

Parking yayi agaban wani babban gida wajajen 2 nadare. Sauka yayi yana kallon wata sabuwar red 2024 Toyota grand highlander dake pake akofar gidan duka duka last month ya chanza mata mota 2023 Toyota Camry hybrid wato bai mataba shine maybe ta saida tasayo wani, dan murmushi yayi yawuce yana ciro key dinshi yabude kofan yashiga ciki yamaida kofan yarufe yajuyo yakunna wuta lafiyayyen hadadden classic falo ne, ijiye key yayi kan tray dasuke ijiye key yaduka yacire covershoe kafanshi yasake juyowa yabi falon da kallo dayake tsaf tsaf banda motan Aman dake kan kujera hannu yasa yakashe wuta sannan yawuce yahau stairs harya fara tafiya yaji kukan Amal chak ya tsaya cus badaga sama yakejin kukan nan ba and dakin Amal na upstairs, shiru yayi jin magana kasa kasa. “sorry Amalulu, Amalilin Mommy, Amalilin Aman, Amalulu na Amalulu yar lukuta, kiyi bacci zakiji sauki gobe kinji, zazzabi ne saina zane zazzabin nan dake damun mini yarinya na” muryan Amal yaji tafashe da kuka sosai cikin muryan yara tace “Momyyy” dasauri yajuyo yashiga saukowa daga staircase direct hanyar dakin yar aikinsu yayi dake kusada store room na gidan, tsayawa yayi gaban dakin yasa hannu yakunna wutan wajen sannan yayi knocking kofan tareda bude kofa atare dasauri sabida yanda yakejin kukan Amal, wata yar budurwa ce doguwa tsaye tagoya yar yarinya dabazata wuce 2yrs ba abayanta, wata yar karaman katifa ne adakin ta yan boarding sai ganamasgo saikuma kwalayen magunguna da flask na ruwan zafi da gwangwanin cerelac da bowl da spoon duka akasan dakin, adan tsorace yar budurwan ta duka kasa goye da Amal abayanta ganin maigidan

dabai taba zuwa nan ba tace “ina yini” gabanta na faduwa dan yaune rana da farko da Baban su Amal yataba zuwa wajen nan, sosai yake kallonta baima tsaya amsa gaisuwanta ba yace “me Amal keyi anan da daddaren nan”? Tana duke akasan still jijjiga Amal dake kuka take abayanta tace “batada lafiyane Alhaji” “Mamanta fa”? Dasauri tace “Anty tadawo daga aiki tagaji bacci zatayi” ranshi abace yace “ita tace ki kawota nan dakin”? Gyadamai kai tayi batare data kalleshi ba tace “eh” “bani ita nan” batai musa ba tashiga kwanto Amal dasauri, yarinyar was looking so weak sai kuka take ta yarda zanin tadauketa ta taso ta taho har inda yake tsaye agaban dakin takawomai ita, itama Amal tana ganin babanta takara fashewa da kuka tace “Daddy” zafin dayaji ajikinta saida yadan firgita ya rungume yarinyar da sauri ajikinshi yace “my princess” yakalli yar aikin dahar takara dukawa anan gabanshi yace “wani magani tasha”? Dasauri tace “Anty tace nabata wayanchan”? Tanunamai magungunan dake gaban katifar ta, Ibuprofen suspension ne dakuma Tuxil D na mura da tari, jiyayi ranshi na tafasa dan yaranshi are his life, cikeda takaici yace “how many mil ma kika bata? Tun yaushe take wajenki”? Dasauri tace “tun wajajen 9 Anty takawomin ita, cikin marfi Anty tace nababbata zatai bacci” “maisa baki kaita da jikinta yayi zafi haka ba akaita asibiti tun 9 har 2 nadare” kanta na kasa still da zuciya daya tace “Anty tace karna kawota bacci zatayi tagaji ta kwana awajena” kallon yar aikin yayi takaici yasa kawai yajuya yawuce yahau staircase rikeda Amal dake kuka sosai ajikinshi, direct dakin Maman yawuce bude kofan yayi kai tsaye yasa hannu ya kunna wutan dakin, wata kyakkywan faran mata ne kwance kan wani makeken lafiyayyen gado tarufa dawani beautiful bargo AC na aiki dan dakin sanyi tana bacci mai dadi, wucewa yayi gaban gadon ya bubbuga filon da kanta kekai yace “Hadiza, Hadiza” firgigit tabude idanunta dasukai ja cikin bacci tabishi da kallo tana mika tana kallon Amal dake kuka sosai tana miko hannu kaman zata kamata, cikin muryan bacci tace “Nuri lafiya zaka kawomin Amal ina bacci batana wajen Ummi yar aikinmu ba pls kamaidata I need to sleep na bala’in gaji wlh” tai maganan tana hamma zata kara jan bargo azuciye Nura ya fizge bargon ya yaye yace “wai what’s is your problem Hadiza? Kinyi neglecting your responsibilities towards me yanzu ma yarana wulakanta mini su zakiyi, this girl is sick baki kaita asibiti ba, baki kirani kin sanar dani ba, kin barma yar aiki ita da magungunan acika marfin idan tai overdosing yarinyar nan fa”? Hamma Hadiza tasakeyi tarufe bakinta sannan tadan yunkuro kadan takalleshi tace “look Nuri banda lokacin fada dakai yanzu Allah ma yasan I don’t have time, dare mahutan bawa ka maidama Ummi yarinyar nan tasan yanda zata kula da ita, she’s great da yara bakaga duk cikin yan aikin danayi tafi dadewa ba almost a year take nema yanzu agidan nan, and my children loves her sosai” wani kalan kallonta Nura yake yace “da ace bani nakaiki asibiti kika haifi yaran nan ba danace banaki bane Amal is just 2 she’s sick crying for you jibi yanda take kuka take miko hannu ki dauketa kina cewa akaima yar aiki, what kind of woman are you da bakijin tausayin yaranki”? “oooohhhhhhhh! Ohh-ho-hooo!” Hadiza tabuga uban ihu tana daura duka hannayenta saman kanta irin ta shiga uku din nan, cikeda gajiya tace “wai all this while so kake muyi fada naki biyemaka cus am busy da work dina baka gabana what’s the meaning na zuwa tashina tsakar daren nan kana neman bala’i na eh? Nace ka maidama Ummi yar aikina Amal for Godsake this is her job we pay for it ba kyauta take mana ba, idan bazaka maidata ba I can call her da wayana tazo sama ta dauketa sutafi, please pls banson problem Nuri, banso, just get out of my room pls katafi dakinka, haa’a kawai katasheni tsakar daren nan da bala’in ka wannan wani kalan neman rashin zaman lafiya ne iyye? Pls kafitan mini daga dakina nace and nagaji nadawo

daga aiki ka maidama Ummi Amal she's good with kids zatasa yarinyar nan bacci pls go away from here" kawai tsayawa Nura yayi yana kallon Hadiza yanda take magana zaka dauka itane mai gidan nan ko itane take putting food on the plate jibi yanda take cemai yafitan mata daga daki kaman itace ke aurenshi ba shi ke aurenta ba, ganin ya tsaya kallonta yake yana jijjiga Amal dake kuka sosai barinma yanda taga Mommy ta na masifa yasa ta buga tsaki. "Mtswwww, kada Allah yasa kafitan nina barmaka dakin, kajika da ruwa kasha" ta tashi fuuu azuciye tasauka daga gadon tawuce tafita daga dakin tana mita,
yana ji tashiga wani daki ta bugo kofan tarufe tana murza key jiyayi kaman an dauramai dutse a kirji kallon Amal dake ihun kuka yayi tana kokarin sauka daga hannunshi tana kallon kofa tana mika hannu tanaso tabi mamanta Ya jijjigata yace "sorry Amal, Daddy's princess stop crying, muje" wucewa yayi yafita daga dakin dakinshi yaje da ita ya ijiyeta kan gado yawuce bayi yatara ruwa yadawo kayan jikinta yacire mata da pampers yadauketa zuwa bayi wanka yamata tsaf kana ganin yanda yake kasan mutum ne mai tsananin son yara fito da ita yayi daure a towel yawuce yafita yaje dakinta hadadden daki komi pink ga zane komi organize wani shimi yadauko yasamata da pampers yace "zakisha tea Princess"? Girgizamai kai tayi a'a, yace "juice, cheese balls, rice, omelette" gyadamai kai tayi dasauri daya fadi omelette hakan yasa yadauketa sukaje kasa ya kunna wutan falo ya shiga kitchen da ita baimasan ta yanda zai fara mata omelette dinba, tsaki yayi yafito yaje gaban dakin yar aikin yayi knocking bude kofan tayi adan taushashe yace "danzo ki soyama Amal kwai" Amal na ganinta tamika mata hannu dan tadauketa dasauri Nura yace "wait Princess aiki zatayi" dasauri yar aikin Ummi tace "ai na iya aiki ina dauke da ita kawota" dan kallonta yayi sai kawai yabata Amal din ta karbeta tana murmushi ya matsa gefe fitowa tayi tana tafiya tana kallon fuskan Amal tace "namiki omu omu"? Dasauri Amal ta gyada mata kai tace "omu omu" Ummi tace "to muje namiki mai dadi ko"? Amal tasake jinjina mata kai.
💫 MATAN??? Ko MAZAN???💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE2️⃣

Binsu da kallo Nura yayi yadan sauke ijiyan zuciya koba komi tayi shiru yanzu, komawa falo yayi yakunna wuta yazauna kan kujera, yadawo ko chanza kaya baiyiba, bai wanka ba ranshi yabaci, kunna tv yayi yana kallon news dudda hankalinshi bawai yana wajen bane dan damuwa ne cike fal aranshi. Yana zaune awajen Amal tafito da kanta rikeda karamin bowl da aka soya kwai mai kyau aciki tace "Daddyyyy Oumu Oumu" tana nunamai bowl din, dan murmushi yayi tazo kusada shi daukanta yayi yazaunar da ita saman kujera kusadashi tahauci, ruwa Ummi tabiyota dashi a water bottle nata mai kyau ta ijiye agabanta takoma chan nesa dasu wajen dinning tazauna akasa duk atakure take dan batama saba ganin mai gidan ba, kusan 1yr tana aiki agidan itada yaran sukafi zama agidan nan, sai yau ne take ganinshi hakan yasa duk takejinta atakure. Dauke kanshi Nura yayi dagakan tv ya kalleta yanda tazauna akasa kaman

wata mara daraja irin yar maulan nan dukta takure tana wasa da hannunta bini bini tana kallon Amal dakecin kwai abinta da hannu kusada shi yasa yadanji wani iri, he always hate yan aiki to be honest yaune rana ma na farko daya taba kallo fuskan yarinyar nan dake musu aiki agida kuma this is almost 1yr take gidan nan, ba yabo ba fallasa yace “jeki kwanta kiyi bacci” kanta akasa cikeda respect tace “saita gama cin abinci na wanke mata hannu na gyara wajen nasata bacci tukunna zan iya bacci” dan jinjina kai yayi saikuma yayi shiru bai kara cewa komiba, yakai hannunshi yataba wuyan Amal din jikinta yadan rage zafi maybe sabida ruwan daya watsa mata neyamaida idanunshi kan TV, tass Amal tacinye kwan ta cillar da plate kasa tace “akoshi” dasauri Ummi ta taho ta duka tadauki plate din da cokalin adan kunyace dan she’s not comfortable yanda Baban ke wajen tamika mata hannu tace “zo aje a wanke hannu” makemata kafada Amal tayi zata kama Babanta da hannun kwai dasauri ya matsa yace “je princess awanke miki hannu” turo baki tayi takalli Ummi dake kallonta, cikeda dabara da iya wasa da yara tace “zomuje muyi wasa da pampoo akitchen” wani kalan dirkowa Amal tayi abin harsaida yabama Baban mamaki tazo gaban Ummi da dugudu tace “ruwaaa, pampoo” da sauri Ummi taduka ta dauketa tana murmushi tace “yauwa Amalulu na muje, idan Aman yatashi gobe shima mu soyamai Omu Omu ko”? Gyadamata kai Amal tayi sukatafi kitchen, dan ijiyan zuciya yasauke to some extend kam she’s good with kids kawaidai shi bayason yan aiki ne and he don’t trust hygiene dinsu, dan ijiyan zuciya kuma yasauke idan ba yan aikin ba yasan Hadiza ba aikin nan zatayi ba ko sama da kasa zata hade.
Tass ta wanke mata hannu ta share mata baki tare suka wanke plate da spoon din tace “yanzu sai bacci ko, nagoyaki”? Gyadamata kai Amal tayi Ummi ta duka tace “yauwa babuuu Amalily” da gudu tahau bayanta tana murna dariya tayi bataso tasake fitowa daga kitchen din hakan yasa sai kawai tacire dankwalin kanta ta warware ta goyata dashi, wasu manya manyan kitson hannu ne akanta shiku ya tsufa sosai amman tanada bakin gashi mai kyau da santsi, zagaye kitchen din tashigayi da ita tana jijjigata tana mata waka ahankali. “Amal Amal yar gayu, Amal yar kyakkyawa, Amal yar fara saidai tana fitsari agado” dan ihu kadan Amal tayi tana hamma Ummi tai dariya tace “to nadaina Amal bata fitsari agado, Amal jaruma ce gimbiya mai kafafun zinare yi bacci to” haka tadinga jijjigata tana zagaye katon kitchen din nan da ita dantai bacci. Gajiya yayi da zama afalo dan dama jira yake agama wanke mata hannu yadauketa suje sama gashi kusan 30min shiru basu fito daga kitchen ba, baki yabude zai kwalama Yarinyar kira yakasa, shi wlh ya manta sunanta kuma is somehow yakirata yar aiki, dan tsaki yayi yamike tareda kashe tv yatafi wajen kitchen din, kofan abude hangota yayi tana tafiya a kitchen din tana jijjiga Amal data fara bacci abayanta suna zagaye, ko kadan bata luradashi ba dan bekai gaban kitchen dinba, yanda yaga take zagaye take jijjiga Amal abayanta gently tapping her bombom ta saman zanin goyo tana mata wake haka sai kawai hakanan yaji yaji wani iri aranshi, he can’t even understand idan guilt yakeji ko anger, wannan wani kalan rayuwane ace mahaifiyar Yarinyar na bacci anbar yar aiki da yarinya bata runtsaba tsakar dare, tun 9 yanzu kusan 3 idanunta biyu, is she not human being ita? Ko machine ce? Kowa fa deserves this sleep, dare mahutan bawa, koda aikinta ne there’s nothing bad idan Maman yarinyar natare dasu to help her out,  abin is really really somehow azuciyanshi, jiyayi ranshi yamai badadi dauke kai yayi tareda dan gyaran murya batare daya karasa kitchen dinba, dasauri Ummi tajuyo jin gyaran murya, batare daya kalli kitchen dinba yace “kawota taje ta kwanta” dasauri Ummi tace “to” goyon tashiga kwancewa kafin ta sauketa tafara jan dan kwalinta ta jefa akanta sannan ta

dauketa a hannu tariga tai bacci ta taho ahankali har zuwa gabanshi tamikamai ita tace “gata Alaji” dan juyowa yayi yakalleta ahankali yasa hannunshi ya karbeta yace “sannu da kokari, jeki huta kema” “to” ta amsa tana tsaye awajen, wucewa yayi itama tawuce falo takashe wuta sannan takoma dakinta ko 1min bata karaba sai bacci.
**

Wuraren 5 yabude ido sabida zafin jikin Amal data kwana dakinshi, tashi yayi zaune yakai hannunshi yatabata yarinyar nan needs hospital wucewa yayi yashiga bayi ya watsa ruwa yafito daure da alwala yawuce yasauka kasa motsi dayaji a kitchen yasa yawuce kitchen yar aikin yagani tana sharara da goge goge jin knocking kofa yasa ta dago kanta dasauri ganinshi yasa ta duka tace “ina kwana Alhaji” juyawa yayi yace “Ipy lau kibar aikin nan kije ki shirya Amal ina dawowa daga masallaci zamu kaita asibiti” bai tsaya jiran amsanta ba yawuce, wanke hannunta tayi ta tafi sama azuciyanta tace Allah sarki Amal dina, dakinta taje ganin bata ciki yasa ta tafi dakin Aman yana baccin shi shikadai batanan to ko dakin Maman take bude dakin tayi da sallama bata wajen hakan yasa tai tunanin dakin Baban, idan da sabo tasaba shiga dan ita ke gyara dakin ta wanke bayi, bude kofa dakin tayi tadauki Amal dake bacci tawuce dakinta wanka tamata ta shiryata tsaf itama tai salla nan da nan tai parking jaka taje kitchen agurguje tamata air frying chips da sausage tasa mata a cute flask nata da ruwa tahada komi da yaro ke bukata, itama taje ta chanza kaya zuwa wani dan dogon Riga baki ba laifi yanada kyau but irin outdated one din nanne shima Anty tabata ta yana gyalen akai tazauna a falo rikeda Amal da yanzu bamata da karfi, shigowa yayi gidan ganinta zaune akasa afalo rikeda Amal data shiryata tsaf in this short time yasa yace “let’s go” dan kallonshi tayi saikuma ta tashi da sauri, harya zauna agaban mota yaga tafito ta kinkimo Amal da katon jakan a hannu tana tafiya da kyar kaman zata fadi yasa kawai yafito yataho da sauri, tsayawa Ummi tayi gabanta nafaduwa ganin yanda ya dumfarota, hannunshi yamika mata yace “bani jakan” bashi tayi yajuya itama tabishi bude bayan motan yayi ya ijiye jakan ya tsaya yana jiranta tana tahowa tashiga baya rikeda Amal saida tai settling down yamaida kofan yarufe yakoma gaba yashiga yatada motan yaja duk wani motsi da Amal zatayi saita tambayeta menene, ciwo, zafi, me kikeso, zakisha ruwa sannu ko Amal dina abinda baitaba ganin Mamanta tayiba.

Wani babban asibiti suka tafi wannan karan shiya sauko yabude musu baya da kanshi yadauki jakan yabar mata Amal dayaga tai lakur ajikinta suna shiga aka karbesu sukai ciki office na Dr suka shiga, wani baturen Dr ne yace “meke damunta”? Kallon Ummi Nura yayi yace “meke damunta” ahankali tace “zazzabi take tun kwana biyu bata iyacin abinci, but nafada ma Anty tadubata tace chanjin yanayi ne, jiya tanata tari sai zazzabi, kuma idan tashiga flowers na gidanmu jikinta na kaikayi, idanunta namata kaikayi shima, jiya batai bacci ba kagani kuma yanzu batada karfi ko kadan” tanuna Amal dake jikinta kaman zatai kuka, sosai Nura ke kallonta saikuma yadauke kai yama Dr bayani da turenci Dr yace “za’a basu gado cus tana running temprature da yawa kafin a debi jininta aga meke damunta, tashi yayi zai debi jinintа da sabuwan alluran daya bude dasauri Ummi takalli alluran tadan kankame Amal ajikinta, ahankali Nura dake lurada ita yamika mata hannu yace “kawota” batai musu ba bashi Amal tayi Dr

yadebi jininta hawaye taruwa yayi a idanunta yabda Amal ke kuka nan da nan aka kwantar dasu awani private room sai kuka Amal take tana mikama Ummi hannu, kasa zuwa Ummi tayi ganin Babanta natare da ita tashi Nura yayi yakalli Ummi yace “zo ketake nema” kaman jira take dasauri taje rungume Amal Ummi tayi tace “likitan nan ko saimun kaishi wajen police yama Amal allura da zafi”? Gyadamata kai Amal tayi a shagwabe, Ummi tace “sannu ko, zakisha Capri ri”? Dan yatsine fuska Nura yayi irin menene Capri ri kuma, Gyadamata kai Amal tayi, dasauri Ummi tabude jaka tadauko caprisone tace “tadaaaaa” wani kalan murmushi Amal tayi dashi kanshi Nura saida yayi murmushin yadan tabe baki yaciro wayanshi aranshi yace “omelette Omu Omu, Caprisone kuma Capri ri ikon Allah” tana cikin bata juice din wayanta dake pocket din jakan kayan Amal yashiga ringing da sauri tasa hannunta daya taciro wata screen touch Vivo ne dataji jiki sosai ganin Anty yasa ta amsa takai wayan kunnenta cikeda girmamawa tace “Hello Anty ina kwana” daga ta dayan bangaren Hadiza tace “kina ina Aman yatashi”? Cikin kwantacciyan murya tace “Uhmm Anty munzo asibiti da Amal ne, jikinta ya rikice” Hadiza najin haka tasan mijinta ne yakawosu asibitin cikeda masifa tace “to yanzu wazai yima Aman brush da wanka yabashi breakfast eh? Ko nine danake shirin fita aiki yanzu zan tsaya nayi all of this, maza maza ki bar Amal wajen Babanta ki kira bolt yazo ya maidoki gida ai nakoya miki yanda ake yin bolt dan nasan nace kifita kije kibi mota along bacewa zakiyi babu inda kika sani, maza maza kira bolt and come back home kima Aman wanka kibashi breakfast ki shiryashi yatafi school kafin school bus yazo keko school bus yazo idan sun tafi ki kira bolt ki kaishi school din dakanki, kina jina tunda ke mahaukaciya ce dakikiya yar kauye dayace kizo kutafi asibiti bazaki iya gayamai zakiyi aiki ba kika bishi, nabaki 3min karki bari su cika ban ganki agidan nan ba, sabida jakanci da dakikanci irin na yan kauye ina biyanki danki kulamin da yara da gida akanme zaki wani asibiti bayan babanta natare da ita, idan kinsan kin gaji da aikin ne bazaki iyaba ki gayamin na sallameki wata tazo ha’aa nida kudi na ko yan aiki guda dari nakeso zan samesu wlh yau yau din nan, zan koreki wlh kika batamin rai” da sauri Ummi tace “kiyakuri Ant……” dip ta katse wayan tashi Ummi tayi dasauri tace “ina zuwa Amal” tajuya dasauri hada ido tayi da Nura dake kallonta hakan yasa da sauri ta tsugunna daganan wajen gado tace “Alhaji zanje gida Anty tace nabar Amal awajenka zanje in shirya Aman yatafi school” kai tsaye yace “koma ki zauna bazaki ba” dasauri ta kalleshi ganin yacigaba da danna wayanshi yasa takoma ta zauna ahankali but gabanta sai faduwa yake kusan 4min da gama wayan wayanta yahau ruri hannu yamika mata yace “bani wayan” daukan wayan tayi tazo har gabanshi ta duka tabashi wani iri wayan yamai a hannu screen din dukya faffashe wannan ai zai iya yagamai fatan kunne saida wayan yakatse yay dialing number ta da wayanshi yatashi tareda ijiye wayanta kan kujera yawuce yafita dan baiso wani yanajin wayanshi da ita waje yafita wajen parking space daidai ta amsa wayan kafinma yayi magana cikin fushi da ihu tace “sabida kaike biyan salary nata kahanata zuwa ko to daga this month kadaina nizan dinga biyan salary nata lemme be in charge of her nai controlling nata to my satisfaction Alhamdulillah inada kudina, but akan mema zaka hanata dawowa ga Aman ko brush baiyiba bai wanka ba yana kuka yunwa yakeji kuma kasan zan tafi shagona yanzun nan maisa kakemin haka? What kind of man are you? Why do u always look for opportunity to belittle me kanunama kowa banda power over anything in our house eh? What is your problem dani? Bakin ciki kake inada kudi kafison kullum ina kasanka ina rokonka do this for me do that for me”? Shiru Nura yayi saikawai yaciro wayan daga kunnenshi ya katse wayan dan talking to Hadiza is impossible, ita ko kunya bataji ta haifi

yara saidai wasu su tayata kula da yaran, gatada baki kaman reza talking to her is just too impossible dukan motanshi yayi ya jingina da motan yayi shiru is this how life zai cigaba da tafiyan mai? Bayagane gaba balle bayan Hadiza, ance communication is a key in Marraige but communicating da Hadiza is impossible kafin kayi magana daya tal tayi dari da hamsin, babu one single abu datakemai na mata, she doesn't take care for him, karma aje batun girki he can't even remember the last time da Hadiza tadau ruwa ruwan nan dai bottle water tabashi yasha, he can't even remember wen was the last time yaci abinci agidanshi, shi bayacin abincin yan aiki itakuma batayi saidai kullum yaci abinci awaje ko agidan abokai, tun yana korafi yan aiki na shigo mishi daki harya dena dan yagane idan basu gyaraba dakinshi baza'a taba gyaramai ba, he can't remember the last time data gaidashi, is as if he doesn't exit awajenta whenever he tries to talk to her tace yafara fitina da bala'in da korafin da mita shi yabarta tagaji, she's not remorseful akan abubuwan datake she feels itadashi equal right sukedashi sabida tana matanshi he can't step and match her ko control her, sabida tana mace doesn't mean zata kwantarmai dakai that's just her mentality, Hadiza is very stubborn ga baki Ya Allah, wlh yagaji baison mata biyu dan ko daya bakar wahala take bashi aduniya, baison broken home dan yataso Mamanshi bata tare da babanshi he don't want that ma yaranshi, baison neman matan banza abinda baiyiba yana yaro shine yanzu zai fara when he's approaching 50 haba bazai tabayiba but he's just tired yarasa ta ina zaibi ya gyarama Hadiza zama ya gwada zama waje yakai 1-2 nadare amman ko ajikinta yadawo ma tai bacci abinta he's just soo tired of everything he's not happy in his home.

Wajajen 10 aka sallamesu da magunguna a hannu suka dawo tunkafin sukai gate na estate dinsu ya hango Aman dinshi kan kujeran security da pajamas ajikinshi da ledan popcorn idanunshi sunyi jaa, jiyayi zuciyanshi takama da wuta parking yayi yafito dasauri security dayake zaune kusada shi yace "Yallabai barka da dawowa Madam ta ijiyeshi anan gashinan yanata kuka yace yunwa yakeji shine na saya mishi Popcorn yamai jiki"? Sabida yanda ran Nura ke daci gyadamai kai yayi Aman yarike hannunshi yakalli fuskan Baban kaman zaiyi kuka gwanin ban tausayi, kaman dan maraya  yace "Daddy where's Anty Ummi am hungry she's the only one that gives me food and play with me, Mommy never gives me food or play with me" suppressing anger dinshi yayi yaduka ahankali ya shafa kan yaron yace "muje Anty Ummi na bayan mota da princess don't cry again okay"murmushi yayi yay bayan mota da gudu yabude yashige shikuma ya tsaya yama security godiya tareda bashi kudi sannan yazo yabude gaban mota yashiga ya zauna yaja mota ta glass na gaba yake kallonsu duka yaran sun kankame Ummi suna hira da ita, sai biye musu take kaman yarinya itama, wlh zaka dauka itane mahaifiyar yaran kawai dan ita black beauty ne yaran kuma fararene tas su kaman turawa amman kana ganinsu kaga strong affection tsakaninsu, sunma manta dashi a motan sai hira suke Aman yarike Ummi gam yanata zuba kaman bashi yayi kaman orphan dazuba, akofar gida yayi parking duk suka sauko tana rikeda Amal, Aman shima yarike mata hannu suka wuce ciki yabisu da kallo direct kitchen suka wuce zaunar dasu Ummi tayi kan kujerunsu dake kitchen din dake gaban island, tashiga yimusu girki agurguje dan Aman yunwa yakeji tana attending to them, ta dafa lafiyayyen taliya na manza fevorite dinsu da kaza ta zuzzuba musu a plate tajuye sauran kuma a kula mai kyau takai dinning ta ijiye sannan takoma kitchen tana bama Amal abaki dantaci da kyau, koda yashigo gidan dan tuntuni yana waya awaje kamshi ne yamai

sallama wani kalan yunwa yaji yanaji dinning yaje yazauna kaman wanda ke tsoron wani abu bude kulan yayi daidai Ummi tafito da tray na ruwa da fresh juice a hannu dantaji zuwanshi ta ijiye kan dinning taduka tace “ko adafa wani abune daban Alhaji” girgixa mata kai yayi yace “a’a wannan yayi” tashi tayi takoma kitchen, kaman mai tsoro yadau fork yasa yadebo kadan yakai bakinshi yatauna dadin dayaji wlh saida kunnenshi yayi siiiii, baisan sanda yadauki plate yadeba ba shi arayuwan shi yanason home made food rashi yasa almost few restaurants ne baisaniba a Abuja ba yaune rana na farko dayaci abincin yar aiki and wlh yamai dadi sosai tass yacinye yatashi ga mamakinshi rawa yaga tanama Amal tana kai abinci bakinta da wayau dantaci, ga magani dayaga ta fito dasu ta zuzzuba a marfi dan an fadamata yanda zata bata asibiti, shima Aman yataso yana tayata rawan sunama Amal rawa dukansu biyun tana dariya sosai fa tana karban abincin tabata maganin ta shanye tass ba gardama ko kakarin amai suna mata waka Aman na tafi kaman suna studio, jinshi kawai yayi yana murmushi ance some yan aiki suna faking love ko sabida parents na yaran but shi all he sees ana is genuine love, kuma yaran loves her suma dearly hakanan samin kanshi yayi yana kallon Ummi sosai, yarinyar black beauty ce tanada tsayi akalla zatai 23 ko 24, yar kauye ce from her dressing but she’s kind and tanason yaran shi kuma her smile is contagious dan gashi shima yanata yi, sannan the way she dance is annoyingly cute, kaman Ummi taji ana kallonta juyowa tayi da fuskanta ta kallo falon karaf suka hada ido da Nura dake kallonta tana rawa ma Amal.

Wanna talk to me about something??? Chat me up anan;
wa.me/+2347012181461
MATAN??? Ko MAZAN???💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE3️⃣

BONUS💃
Sosai kirjinta yabuga da sauri ta sauke hannayenta kasa tadaina rawan tasauke kanta kasa shima daga kallonshi gabanta nafaduwa dumdumdum.
Wucewa Nura yayi dasauri sama zuwa dakinshi yakasa daina ganin fuskan Ummi dana yaranshi how happy all of them were, yanda itada Aman kema Amal rawa, bayi yafada dasauri ya watso ruwa yafito yashiga shiryawa dan yafita meeting din dayake dashi is by 2, cream yadauka zai shafa saikuma ya tsaya maisa ya kalleta haka smiling ya tambayi kanshi? He was lost dayana kallonta, yar aikinsu ce fa but he was finding all abubuwan datakeyima yaranshi super cute, dan ijiyan zuciya yasauke saikuma yacigaba da shafaman.

Ummi daduk takasa natsuwa itama a kitchen ta tambayi kanta maisa yake kallonta, tun yaushe Alhaji yaganota tana rawa haka? Duk wani kalan kunya kunya da nauyi nauyi taji tanaji, IPad din Aman tadauko ta kunnamusu anan kitchen din dan bazata rabu dasu ba tashiga gyaran

gidan duka tanaso tana gamawa tamusu wanka, itama taje tayi saita daura abincin dare.

Shiryawa yashigayi cikin suit dan dawasu representative na China company zai hadu dasu yanaso yabasu contract nayin titin cikin estate dayakeyi, yana cikin daura agogo wayanshi yahau ringing kallon wayan yayi ganin Sis yasa yakai hannunshi ya danna call din batare daya daga wayanba yacigaba da saka agogo daga ta dayan bangaren akace "Ya Nura ina yini" "how are you Aminatu ya jikin Hajiya kunje asibitin"? Kasa magana tayi sai bakinta yahau rawa, dasauri yasa hannunshi yadauki wayan gabanshi ya mugun fadi yakai wayan kunnenshi dasauri yace "what happen jikin Hajiya ne meya faru?" Cikin kuka tace "dazun nan tafadi abayi yanzu haka muna asibiti" bugawa kirjinshi yahauyi sosai anatse yace "Dr Tanimu ne ke ganinku"? Dasauri tace "eh shine" dan ijiyan zuciya yasauke yace "daina kuka ya isa babu abinda zai sami Hajiya kinji" kaman yana gabanta gyadamai kai tayi, cikin dan taushin murya yace "is okay, zanyi magana da Tanimu I think zan muku booking flight gobe kutaho nan Abuja taje babban asibiti anan don't cry again hankalinta zai tashi, akwai kudi awajenki"? Dasauri tace "eh akwai" ahankali yace "to stop crying bari nai magana da Dr Tanimu" nan da nan ya katse wayan yakira Dr sunyi magana da dadewa sannan ya katse wayan dakanshi yamusu booking first flight na gobe da safe sannan yasake kiran sister nashi yace zasu biyo jirgin safe gobe suzo koya ake ciki tadinga gayamai yatashi ya idasa shiryawa duk mood nashi ya chanza sannan yafito anan falo yaga Aman da Amal suna kallon cartoon a iPad nasu duk an musu wanka sunyi kyau gwanin ban sha'awa kaman ya debesu yafita dasu Amal kaman ba itane mara lafiya ba karasawa yayi inda suke ya duka yamusu peck agoshi yace "Dady zaitafi aiki" dasauri Aman yace "Dady zan bika office" shiru yayi kaman mai tunani yana shafa kansu yace "shikenan zanje daku amman sai ranan Saturday jibi kaga gobe akwai school yau bakuje ba dukanku" Dasauri Aman yace "hadda Anty Ummi zamu itama taje taga Daddy's bigggggg office" ya ware hannunshi biyu yana nuna how big office na babban shi is, dan murmushi yayi yana kallon Aman din kafin ahankali yace "yes Son hadda Anty Ummi" dasauri Aman yace "love you Dady u the best Dad ko Amali? Dadyn mu is the best" dasauri Amal yace "yeeeessssss Dady is the best" murmushi yayi yace "my princess and my Aman are the best nima" harzai tashi yace "ina take?" Aman yace "Anty Ummi"? Gyadamai kai yayi dasauri yace "itama taje tai wanka adakinta" jinjina kai yayi yamike yace "to natafi bye" bye sukamai yawuce yafice.

Wani babban shago ne girmanshi zaiyi wani super market din sama da kasa ne, kasan abayoyi ne irin na yan millions din nan designers dan babu abayan yan 100 ashagon saikuma sama asalin designers bags da shoes ne latest collection ma kuwa, zaune take cikin wani office dake nan sama babban office ne na gaske dawasu mata guda biyu suna hira, daya daga cikin matan biyu ne tadaura tissue kan idanunta tana kuka Hadiza taje tsaki tace "kodai nazo nai magana da mijin nan naki ne Baraka"? Dasauri Baraka tazare tissue dagakan idanunta takalli Hadiza idanunta sunyi jazur tace "so kike ya koreni? Not everyone is as lucky as u are kinada miji kaman Nura mai hakuri da share magana, idan nama Ubale abinda kikema Nura saiya lakadamin duka halan saiya korani gida" wacce ke kusa da itane ta tureta tace "dallachan ai gashinan saisa sai gallaza miki azaba yake waya cemiki anama maza good girl yanzu??" Dasauri Hadiza tace "ahh tohh tell her ooo my dear, tell her Zee cus good girl no dey pay again,

kima miji good girl ya tattakaki yayi using naki do dambu yaje ya watsar a shadda, ai yanzu zaman Auren fire for fire ake yana baki kada kibari yakai kasa give him back gbasgbos kawai saikaga yasha jinin jikinshi yasan keba kanwar lasa bace, kinga Nura ko giyan wake yasha yasan bai isa ya tunkareni da nonsense nashi ba cus bana ma dauka ne kuma gashinan nasama ma kaina lafiya I do duk abinda naga dama duk abinda raina yaso agidana to waima tsaya idan nai aure banyi whatever naga dama agidana ba yo menene fa'idan auren? Menene banbancin gidan mijina da gidan iyayena? Abeg ke waye Ubale yana cemiki kule kicemai chass wlh zakiga kun zauna lafiya" dasauri Zee tace "Allah yasa ta dauka, itane kullum yamata ihu kaman ubanta, fita saiyaga dama yake barinta, yahanata business ya kulleta agida kullum ciki yake duramata won't you speak up kinuna mishi kefa duk lokacin dakikaga dama fita zakiyi ki kwatarma kanki yancinki, ki nunamai kedashi are equal sabida yana namiji baya nufin zai dinga juyaki, munafa zamanin feminism ke duk inda namiji yau yataka aduniya kema zaki iya takawa to akanme zaki maida kanki slave dinsa? Jibemu kawayenki yanda muke more rayuwa muncigaba ke kinachan kina bautama mijin dake hanaki fita sana'a, yakuma miki ihu" tissue takara dauka dan maganganun su nasata jin badadi datasan hakane da da Zee tazo daukanta batabita ba, tace "nidai kubarni duk randa nazo wajenku saikun sani ina feeling bad inajin kaina kaman banda sa'a aduniya, kaman I'm the unlucky one, Ubale na sona ina sonshi kuma ya isa yace nayi nayi karnayi karnayi ya is……." Mtswwwww Hadiza taja tsaki dayasa Baraka tai shiru takalleta Hadiza tace "takuraki dai baya bari kiyi yanda kikaga dama, imagine yaranki uku har yanzu kece ke komi agidanki, girki, kula da yara uku fa da sauransu ke jakace Baraka? In nice ai sai na mutu, Idan yana sonki bazai sama miki yar aiki ba haba akan mene zaki dinga shiga kitchen kina girki awan nan zamanin da masu kudi ke hiring intercontinental chef yana musu girki agida that's my next plan ma ni nadauko professional Chef daman na share zancen ne bayan na sami wannan current yar aikin nawa Ummi but still zan dauko" dan murmushi Baraka tayi tace "Allah baki sa'a, kowa nada abinda works for him, ninaji naga kuma zan iyane ne, mubar maganan please kona tashi nayi tafiya ta gida daman Zee takawoni, I don't have to be like you ladies, tundadai ba dukana ko wahalar dani mijina keyiba ko neman mata Alhamdulillah" dasauri Hadiza tace "to abar maganan amman wlh sabida kawai ke kawarmuce duk tare muka taso da tuni mun rabu dake danni banga dalilin dazaisa kene ke duka aikin gidanki ba mijinki na miki ihu kaman wata jak……." Karan da wayanta yayi yasa takasa karasa maganan takalli screen din ganin Nuri yasa tai murmushi sosai tajuyo da wayan tace "kun gani" tanuna musu screen din wayanta tace "tsakanina dashi kar tasan kar ne amman jibi yanda yake bibiyana maza fa saida hash treatment kana musu taurinkai ki nuna musu ke fire for fire ce cus sun iya raina mace kai mai sanyi irinsu Baraka" Zee tace "kwarai kuwa Aminiyata".

Tashi Zee tayi takalli Barakan tace "muje mu duba abayoyin to" tashi tayi tabita suka fice ba walwala kan fuskanta, Hadiza na kallon kiran sai murmushi take dake kara fito da kyawun fuskanta saida wayan yayi gab da katsewa ta dauka takai kunne ayangance tace "ka gama nunamin matsayina menene kake kirana kuma yanzu"? Dan shiru Nura yayi yana jinta ba sallama bakomi kafin yamace wani abu tai magana, yana addu'a duk wani namiji dabai Riga yayi aure ba to Allah yarabashi da auren mai baki kaman na Hadiza, saikuma chan yace "Hajiya tafadi abayi yau an kaita asibiti but hankalina bai kwanta ba namusu booking flight na safe gobe

zasu taho nan da ita da Amina zan kaita hospital taga kwararren Dr, specialist" wani abu Hadiza taji ya tsaya mata arai zai cigaba da magana ta tareshi tace "wai Nuri what gives you the right kadinga making decision regarding our family on your own eh? Wai meke damunka ne zakace Hajiya bama ita kadaiba harda kanwanka suzo gidana bazaka fadamin ba kaji me zance kafin nan kai kadaine agidan? Kodon kaga gidanka ne? Koma da gidanka ne ai nima ba zaman banza nake agidan ba aure ne yabani gidan dan haka u have no right to invite koma waye into my home without telling me, without seeking my approval" tunda Nura yake baitabajin urge na yadaga hannu ya mari mace ba sai yau wlh he feels kaman yadaga hannu ya kifama Hadiza marin da saiya maida fuskanta keya, keyanta yadawo fuska, mahaifiyarshi ba lafiya bama ta tambaya yaya jikinta ba or anything sai maganan gida, menene agidan? What is house? Me Hajiya zatayi agidan? Yau shekaransu nawa da aure Hajiya bata taba zuwa Abuja bama ballema gidanshi so menene abinda matan nan ke fadi? What can a sick old woman zata possibly iya miki agida tana fama da kanta fisabilillahi?Yanada mahaifiya mara lafiya da zatazo garin abuja for the first time yaje yakama mata hotel ne sabida matanshi batason wani yazo wajensu???

Daurewa yayi yarike zuciyanshi yana controlling anger yadan sauke ijiyan zuciya Hadiza tabugamai ihu da tsawa tawaya. "Ina maka magana kamin banza are you deaf ne or what Nuri? What gave you the right to invite a third party to my house baka fara sanar dani ba" shi Hadiza ke kira deaf??? Innalillahi, cikin wani irin murya datai sanyi sosai tsabagen bacin rai yace "mahaifiyata ce third party Hadiza? Maman mijin dakike aure uban yaranki, kakan yaranmu itane 3rd party"? "Well u can translate it duk yanda kaga dama is none of my business just listen to wat am about to say" tadan gyaran murya tace "first of all bada yawuni aka kawota ba don't expect anything from me babu abinda ya shafeni da dawainiyan ku, sabida Hajiya bazan fasa fita aiki na ba, kuma bazan shiga kitchen ba, kuma bani acikin tafiyan zuwa asibiti ko rakiya kai infact banda any business with anything dazai faru daga goben nan zuwa harta bar gidan, dan haka kaika sani ni please sai anjima I am busy with work, I don't have time for ur unnecessary demand" ta katse wayan Nura yadade yana kallon wayan kafin ya fuzar da iska kaganshi dole kai saluting nashi dan namiji ne mai hakuri dayay composing kanshi bai duramata zagi ba, dama kiranta yayi yaroketa kada taje aiki gobe sabida su Hajiya sannan kuma ya tambayeta me da me babu agida amman jibi abinda tayi rasa abinda zaiyi yasa yayi dialing number Gardner na gidanshi ruwa ringing daya ya dauka anatse Nura yace "Amadu banda number Ummi danje ka buga kofa ka bata wayan" dasauri Amadun yace "gasuchan inajin muryansu a garden takai yaran suna buga kwallo bari nakai mata" anatse Nura yace "ok".

Bata wayan Amadu yayi yace "gashi Alhaji yakira zai magana dake" sa wayan tayi a kunne kaman yana gabanta ta duka tace "Alhaji ina wuni" baisan what just happen ba amman har cikin zuciyanshi yaji sanyi aranshi na muryanta, dan ijiyan zuciya yasauke ahankali yace "Ummi mahaifiyata da kanwata zasuzo gobe dasafe Mamana bata da lafiya zataga likita agarin nan" da zuciya daya Ummi tace "Subhanallahi Allah yakara sauki, Allah yasa kaffara ne, Allah kuma ya iso dasu lafiya ya tsare hanya" Wallahi he cannot even explain wani kalan dadin addu'an ta da sanyinsu dayaji aranshi, jin yanda yayi shiru yasa Ummi tace "Alhaji kanaso na gyara musu wajen kwanan su ne namata abincin da marasa lafiya keson ci"? Harga Allah ta dauka abinda

takira yafada kenan cus ana bata wayan abinda yafara fada mata kenan mahaifiyarshi ba lafiya kuma gobe zatazo. Yarinyar nan is not just good with kids tanada great sense of humor tanada hankali tasan meyakamata and tanada natsuwa, though abinda yakira was yanaso ya tambaya menene babu agida but tambayanta made hum wanna talk to her more, ahankali yace "menene abincin marasa lafiya Ummi"? Kai tsaye dan babu komi aranta tace "meke damun Mama Alhaji"? Yanda tafadi Mama ba Hajiya ba dan yasan batasan Hajiya ake kiranta ba wani sanyi yaji aranshi baisan lokacin dakaman wani dan karamin yaro yace "ciwon sugar da hawan jini ke damunta" dan shiru Ummi tayi kafin ahankali tace "abincin dayakamata tanaci abinci ne da babu sugar aciki, babu Gishiri kuma dan Gishiri yana kara hawan jini, zan mata tuwon Alkama ko tuwon garin plantain dabai nunaba amman duka biyun bamu dashi agida, da miyan ganye, Gwaggo na a kauye nada hawan jini da ciwon sugar duk nasan irin abincin datake ci dake taimakamata bata cika ciwo sosai ba, idan Mama tazo itama zan dinga dafa mata zakagani zata ji sauki da izinin Allah" dan murmushi kadan yayi a tsane yace "nagode Ummi kituramin sunan abubuwan da zan sayo dakuma abubuwan da babu agida, saiki gyara musu wajen kwanan" Ahankali tace "to" dan shiru yayi itama tai shiru tana jiran taji ko akwai wani abun jin shiru yayi yawa yasa tace "hello" batare daya amsa ba yace "inaso naci tuwon shinkafa da miyan taushe ki dafamin kinji" yanda yayi maganan ataushashe saida taji wani iri dasauri tace "too" yasake shiru itama tai shiru tana sake jiran maganan shi maganan su Aman da Amal dayaji suna Anty Ummi come come let's continue yasa yace "to saina dawo ko" ahankali tace "too Allah dawo dakai lafiya" lumshe idanu yayi tareda zare wayan daga kunne he just wish da matanshi yayi dis dogon magana wlh babu abinda yake craving yanzu aduniya irin kwanciyan hankali, Allah ya azurtashi, yakuma bashi yara, kwanciyan hankali ne kawai yarasa, yesterday yafara magana da yarinyar nan why is he enjoying conversation da ita haka?.

See y'all Saturday 🥰

Let's keep HADIZA in one place, one of the major abu dake kawo matsala agidan miji is shigowan baki, guest ko visitors aturence.

Mata will always say ban isa nakawo baki batare dana sanar dakai wane ko wance zatazo ba.

Maza kuma sai sun gama cema mai zuwa Allah kawoshi lafiya za'a cemiki babe wane ko kaza na hanya fa zaizo ko zatazo tamana kwana biyu hakan na batama Mata dayawa rai.

My question is, is it okay for mijinki ya yarda kowa yazo kafin yazo yafada miki daga baya wane ko kaza zaizo?
Koko yakamata yafara neman yardanki ne kafin wane ko kaza yazo?? Cus I keep wondering gidan aure belongs to waye exactly??
Does it belongs to the wives ne sabida ai cewa ake za'a kaiki gidanki ko it belongs to mijin kadai ne koko gidan aure belongs to the TWO OF YOU???

To idan gidan na dukanku ne biyu maisa ba'a making decision kan wanda zai shigo tare???

Mata ayanzu daku nake ko sabida maza sunsan mun tsani ace wane ko kaza zaizo ne koda an gayamana bazamu yarda ba saisa gwara suyi accepting wane yazo kafin asanar damu cewa wane zaizo rana kaza????

How do you think za'a iya magance yawan issues da ake samu idan za'ayi baki agidan miji??

Let's discuss this👇🏽
💫MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

Novel din nan is FREE bana kudi bane.
Chat me up don saki a group

wa.me/+2347012181461

EPISODE4️⃣
Wuraren 7:30 Hadiza tashigo gidan gabaki daya ranta amugun bace yake, Aman da Amal sai Ummi ne afalo dukansu ukun suna zaune kan dogon kujera suna kallon videos letters sound for Amal dudda Ummi bawani boko tayiba iya kanta JS3 but ta iya all this basic things na school shima sound din dan bata iyabane zamanin su da ABCD sukai karatu ba da sounds ba saisa suke koya tanan youtube yanda Amal ke koya itama haka take koya dan sabida koya musu, jin an bude kofa kai tsaye ba sallama yasa suka jujjuyo dukansu hada idanu Ummi tayi da Hadiza dake mata wani kalan kallo dayasa dasauri tamike tsaye daga kan kujeran ta duka kasa danta gane kallon me take mata cike da girmamawa tace "barka da dawowa Anty, ina yini" Hadiza da dama ta shigo da mugun bacin rai dan tun kiran da Nura yamata ashago ranta yake abace tace "ke ban gayamiki koda wasa kada duwawunki yazauna akan kujerun gidana ba, ke kinada darajan dazaki zauna inda nake zama ne yar aiki dake, ubanwa yagaya miki yan aiki nada matsayin zama akujerun gida" Ummi da kanta ke kasa ahankali tace "kiyakuri Anty mancewa nayi Amal muke koyama karatu" baki Hadiza tabude zatai magana daga Aman da Amal da duk suka tashi suna kallon Maman nasu Aman yace "stop shouting at Anty Ummi Mommy" dasauri takalli yaron ta ballamai harara, turo baki Aman yayi yace "u are always fighting and screaming Mommy our school teacher tace anger causes sickness" hararanshi Hadiza tayi bata tace "nakusan fasa bakin nan naka mara kunya kawai" turo baki yayi dan haushin Mommy shi yakeji sosai sabida yanda koda yaushe fada takema Anty Ummi su, bata sake cewa komiba tun maganan Aman tacire heels din dake kafanta awajen tawuce dinning straight taja kujera ta zauna tana sauke jakanta kan table din tace "idan kinga dama kizo kibani abinci" tashi Ummi

tayi da sauri ta taho dinning din Aman kuma yakoma kan kujera yayi zamanshi yadauki IPad itakuma Amal tayi hanyar dinning din cikeda shagwaba tace “Mummy babuuuu, ki goyani zanyi bacci” cikeda masifa Hadiza ta nunata da yatsa tunkafin takarasa dinning din tace “don’t even come here wuce kitafi wajen Aman kiyi karatu yanzun nan nadawo zaku fara damuna, goyon kaniyanki zan miki, jeki jira yar aikinku tazo tagoyaki, Oya go back” juyawa Amal tayi tafashe da kuka dasauri Ummi takalleta kaman tadaina serving Maman taje ta dauketa, ta tsani taga yaran na kuka wlh har cikin ranta, ahankali tawuce wajen Aman tafada jikinshi rungumeta yayi yace “stop crying Amali Anty Ummi is coming yanzun nan kinji” Gyadamata kai tayi yana share mata fuska yace “let’s play game”.

Tunda Ummi tafara serving tuwo a plate Hadiza ke kallonta zuciyanta na wani kalan tafarfasa kawo tray gabanta Ummi tayi ta ijiye bata idasa jaye hannunta ba Hadiza ta daga tray gabaki daya ta mike tsaye ta kwarama Ummi akai da tuwon dake a leda da miyan taushen da kwanukan da cokulan duka suka bare akanta wani kalan mahaukacin azababben mugun ihu Ummi ta kwala tafashe da kuka dayasa su Aman suka firgita dukansu suka juyo ganin Anty Ummi ta tsugunna a dinning ga miya tundaga saman dan kwalin kanta har goshinta da idanunta ta kullen gam tana ihu sosai jikinta nawani kalan rawa kaman wace ta zare tsabagen azaban zafin datakeji na miyan dakuma yajin miyan a idanunta yasa suka taho wajen da gudu Aman yace “Anty Ummi” cikeda masifa Hadiza tanunata da hannu tace “kina gidana, kinacin abinci na, nabaki makwanci, nabaki kayan sawa, nabaki sabulun wanka dana wanki, sannan ina biyanki kizo bazakimin biyayya ba, sau nawa ina gayamiki ni bancin tuwo sau nawa nake gayamiki? So kike nayi kiba nai katon ciki? Zanje sama nai wanka ki tabbata kin dafamin wani abun kin kawomin dakina kafin nagama wanka inba hakaba wlh saina koraki daga gidan nan this night” ta dauki jakanta tawuce sama fuuuuu, tsugunnawa daga Aman har Amal sukayi agaban Ummi da jikinta har bari yake sabida zafin miyan dan bata dade da gama miyanba ta juye a kulan gidan ga kulan su irin na millions din nan ne masu rike zafi kaman me, dudda Aman yaro ne amman saida yakai hannunshi yacire tuwon daga jikinta yana kuka sosai ya yar akasa yace “Anty Ummi sorry stop crying” Amal tace “Mommy is badddd mommy” sosai Ummi ke kokarin tabude idanunta takasa sai kuka take dudda kukan take na tausayin kanta tariga tai alkawari komenene zatai hakuri tana bukatan albashinta dashi Gwaggo ke zuwa asibiti dakuma shi ake tara kudin auren kanninta, dole ta jure komi itane hanyan cin abincin gidansu, so take ta mike but tama kasa hannunta Aman yakama Amal ma takama dayan yace “let’s go Anty Ummi ki wanke fuskanki” gydamusu kai tayi tana tsayar da kukan datake ta yunkura zata tashi tama kasa saita kara fashewa da kuka daidai lokacin an bude kofa da sauri su Aman suka juyo ganin Baban su shima ya shigo ya tsaya chak yana kallon daga yaranshi har Ummi dake kuka sosai kaman anyi mutuwa agidan ga jikin Ummi duk miya, fuskanta ma haka takasa bude idanu yasa yayi wajensu dasauri baima cire takalmi ba yace “Subhanallahi meya faru faduwa kikayi Ummi” Tsayar da kukan tayi dasauri muryanta na rawan sheshekan kuka tace “eh” tana yunkurawa zata tashi dasauri Aman yace “is Mommy Dady, ita ta kwara mata the whole tray na abinci akai Anty Ummi has been crying” warware handky daya ciro Nura yayi daga aljihunshi baiyi wata wata ba yakai kan fuskanta cikeda damuwa ahankali yace “tsaya” batai musu ba tsayawa tayi kwashe miyan kan idanunwanta yayi tass, miyan yayi fasha fasha awajen harda gashin idanunta, sannan ya kwashe na goshinta dana kumata batare daya taba na wuyanta ba dudda

baka ce but he could see yanda fatan fuskan yayi ja, ijiye handky yayi dasauri kafin ahankali yakai hannuwanshi duka biyun yakama kafadanta dagashi har ita atare duka sukaji wani iri dasauri tayi kokari fizge kanta strictly yace “stop banson gardama, tashi muje” yanda yayi maganan ba wasa hakan yasa bata kara gardama ba, yana rikeda ita haka yayi kitchen da ita su Aman suka bisu bude kofan kitchen din yayi zuwa nan backyard gaban wani tap dasuke dashi awajen, yabude tap din yajuyo yakalli Aman yace “je bayin Anty Ummi kadauko mini sabulun wankanta” “okay Dady” Aman ya amsa yajuya da gudu shikuma yabude tap din yace “tsugunna” ahankali Ummi ta tsugunna, gently yadinga tara ruwan da hannunshi yana watsa mata a fuska har saida miyan ya fiffita duka da wayanda sukenan asaman gashin idanunta daidai Aman yakawo sabulan, ga mamakinshi sabulun vivo yagani ahankali ya karbe yakama hannunta yasa sabulun aciki yace “wanke fuskan mugani da sabulu” shafa sabulun tayi ta dirdirje da kanshi yake zuba mata ruwa tana wankewa tass ta wanke fuskan, igiyan wajen ya kalla ganin wata singlet dinshi wanda yasan itane ta wanke yajawo yabata yace “share fuskanki saiki bude idanun nagani”

Share fuskan tayi ahankali sannan tashiga bude idanun yajin dataji yasa tamaida idanun ahaukace tarufe tafashe da kuka kunsan yanda yaji ke birkita mutum tace “wlh da kwai yaji sosai Alhaji, wayyoo Gwaggo na nashiga uku” shi arayuwanshi yanada tausayi, ya tsani aga ana hurting mutane in general balle kuma yaga mace in pains, da sauri yasa hannunshi ya karbi hanky yamikama Aman yace “hold it nagani“ sabulun yadauka daga kasa yasa a hannunshi ya fara wankewa sannan ya murza sabulun a hannunshi ahankali yadan kalli fuskanta yanda ta kankame idanunta gam jikinta har lokacin rawa yake tana dan kuka, dan ijiyan zuciya yasauke sannan yakai hannunshi gently yashafa sabulun a fuskanta kaman yanda ake wankema yaro karami fuska, fuskanta is sooo soft kaman na dan yaro, almost 30sec yayi yana chuda fuskan sannan ya kunna pampoo yashiga wanke mata fuskan tass kafin yakarbi singlet din ya share fuskan da kyau ya tsane dogayen eyelash nata kafin ahankali yana tsugunne agabanta yaciro wayanshi dudda akwai haske wajen bauuu flash na wayanshi ya kunna yabama Amal yace “princess haskamin fuskanta” dasauri Amal ta karba ta haska fuskan Ummi, shima yana kallon fuskanta dake sheki yaji wanki da sabulu yace “bude idon nagani” gently tashiga bude idanun dake rawa sosai na haggu tabude tass na dama ne tabude kadan dan tanajin yaji sai yarfe hannu take ta rude sosai ganin yanda takeyi yasa ahankali yace “tsaya” tsayawa tayi ijiye singlet din yayi kan jikinshi yakai duka hannunshi ahankali yayi cupping fuskanta dasauri Ummi takalleshi tadade rabon dataji namiji dab da ita haka, ahankali babu komi aranshi yakai hannanyenshi ya ware kwayar idannun nata dake mata yaji kafin gently Ya hura iskan bakinshi ciki wani kamshi Ummi taji da sanyi daya ratsa jikinta feeling inama ace zata sami miji dazai dinga kula da ita haka kaman yanda Alhaji keyi yanz, Alhaji nada kirki gashi kyakkyawa fari dashi kaman wani balarabe ga bakin saje, tsayar da hura idanun yayi ganin tabude su rass tana kallonshi kaman yaune rana na farko datake ganinshi shima zuba mata idanu yayi yana kallon kwayar idanunta yanda suke walkiya sabida hasken flash da Amal ke hasko musu, idanun sunyi ja na kukan dataci da yanda tai looking so helpless dakuma yanda take kallonshi hakanan saiyaji kaman yasata ajikinshi ya lallasheta, there’s something about her da kawai he finds

interesting baisan menene ba. “Anty Ummi yadena yajin”? Maganan Aman yadawo da dukansu daga duniyan tunani atare dukansu kowa ya janye idanunshi, Nura ya mike tsaye da sauri yawuce ciki batare daya kara kallonta ba itakuma ahankali tamike tsaye tana goge wuyanta, gyadama Aman kai tayi tace “yadena” dasauri sukazo kusa da ita suna kallon fuskan hakan yasa ta tsugunna dukansu taba fuskan nata sukayi cikeda so sukace “sorry Anty Ummi” murmushi tayi sosai cikeda kokarin cheering nasu up tawani daga hannunta sama tace “Anty Ummi jaruma ce kaman Amalili, ko Mudi da Kumurci tsorona suke menene yajin miya dashima bazai tsorata dani ba” haba zokaga yanda sukahau dariya, Aman yace “Anty Ummi yaushe zaki kaimu kauyenku muma muga Mudin nan da Kumurci” hannunta takai kan kumatunta kaman mai tunani kafin tace “wata rana zamuje” ihu sukahau yi suna tsalle Nura daya dade yana kallonsu ta window kitchen murmushi yayi yawuce yadauki mop yafice gyara dunning din yayi da kanshi. Shigowa sukayi a kitchen din fita tayi taje dakinta ta chanzo kaya zuwa wani atampa dogon red yamata kyau sosai.

Tana fitowa hada ido sukayi da Nura dake zaune a dinning yanacin tuwo adan kunyace ta sauke kanta kasa tazo wajen ta duka har kasa tace “Nagode Alhaji, kana bukatan wani abune dazan kawo maka”? Sosai yake kallonta red yamata kyau dudda babu wani special abu game da atampan but yamata kyau, jin shiru baice komiba yasa tadago kanta ahankali hada idanu sukayi da sauri yadauke kai itama maida nata kasa tayi dasauri, ahankali yace “bana bukatan komi, thank u” mikewa tayi harta juya tafara tafiya kaman daga sama taji yace “abincin yayi dadi sosai, thank u Ummi” dadan sauri tajuyo ga mamakinta kallonta yake suka sake hada idanu sukayi, faduwa gabanta yayi dasauri tasauke kanta kasa tasake juyawa zata shiga kitchen batare datace komi ba yace “mezakiyi a kitchen”? Ahankali tace “Anty zan daurama wani abinci batacin tuwo” strictly yace “wuce kije ki kwanta kihuta” dudda bataso ba dan batasan mezai biyo bayaba kasa musu tayi tawuce takoma dakinta ta kwanta.

Fess yagama cin abinci yakai komi kitchen dakanshi yafito yaje sama fitowa yayi da paracetamol, bottle water yadauka mara sanyi yaba Aman yace “kaima Anty Ummi kace nace tasha” gyadamai kai tayi yawuce da gudu yatafi dakinta Amal na binshi yakoma falo yazauna yana saka news duk yanda yaso yama gane meke faruwa a news din kasawa yayi yawuce sama fuuu, bude kofan dakin Hadizan yayi ranshi abace tana zaune gaban dressing mirror daure da towel tana shafe shafen ta na night routine batare da tajuyo ba tace “ki ijiye abincin kiwuce kifita dakikiya kawai next time try this nonsense kinbar gidana kenan jaka kawai yar kauy…..” “Hadiza!” Nura yakirata da kakkausan murya saida gabanta yafadi dan baitaba kiranta da zafi haka ba juyowa tayi da sauri ta kalleshi ganinshi tsaye a tsakiyar dakin yana kallonta ranshi abace, haderai itama tayi tace “badai kahana yarinyar nan dafamin abinci ba dan idan kayi haka u will see the other side of me Nura” wani kallo yamata yace “inason naga other side of you din today are you crazy? Ke wace kalan senseless mata ce? Kissan kai kike kokarin yi agidana? Are you trying to kill that girl?” Hannu ta dagamai tace “please lower your tone ni matarka ne ba some yan aiki dazaka dinga dagama murya ba Nuri, I’m your wife not slave so keeep muryanka down by now kasan I don’t take that shit, namiji yazo yana wani mini ihu akai

saikace ubana kuma ma idan na kasheta sai me? Eh? Ba yar aiki bace, yarinya mara galihu duk irinsu ne irin yaran da akauyen su akekai yara maza almajiranci mata kuma akaisu aikatau kota mutu sai me mezai faru? Almajirai nawa suka mutu wani abu yataba faruwa? Ai yara da iyayensu suka nuna basu da gata mutane ma basa gatanta su so bakaina farau ba dan yar aiki ta mutu agidana ehe" Sosai Nura ke kallon Hadiza shi baimasan tayi nisa haka ba sai yau wato tanada answer for anything, at this point baimaso maganan nasu yayi nisa dan kar zuciya ya debe shi yadauketa da mari hakan yasa cikin kakkausan murya yace "duk randa kika sake trying nonsense din nan wlh saikin bar gidane duk wani abu dake gidan nan fara tundaga kan gateman suna karkashina ne, hakki na ne nakare kowa na tsaresu dan haka don't ever try hurting mutanen dakemin aiki inba hakaba u will leave this house!" dudda maganan ya mugun mugun sosama Hadiza rai amman daurewa tayi dan bataso yagane tai wani kalan shewa. "Ahayyeeee nanaye ance dama idan baka mutu ba bakagama sanin halin maza ba, Nuri ni kakema gorin zaka kora daga this rat hole dakake kira gida"? Ta nuna dakinta da ko'ina da hannu, tsaki kawai Nura yayi yajuya yafita tabishi da sauri dan idan bata bashi amsan maganan nan ba hankalinta bazai kwanta ba kai zazzabi ma zai iya kamata, tana biye dashi yana tafiya tace "zan iya gina gidan dayafi nakan nan sau dubu a kyau dakuma girma Nura kada kayi kuskuren yimini gorin gida, duka duka yaushe kayi kudin lokacin dana aureka kagama masters akan architecture kanama wani building agency aiki har kazo kabude naka kampanin na harkan filaye da gine ginen estate anan Abuja, who do you think you are dazaka min gorin gida nixaka kora Nuri, au ina maka magana ka maidani mahaukaciya kayi tafiyan ka wlh wlh yanda ka batamin rai dinnan saina huce akan mahaifiyark……." Chak Nura ya tsayar da tafiyan dayakeyi akan staircase yajuyo ahankali yakalleta itama daidai tana tsayawa dab da shi tana kara rike gaban towel nata da kyau tana kallonshi tace "da ilimina da sana'ata da darajata har ka isa kazo kana gayamin na kara dukan wata yar aiki sainabar maka gidan ka, sabida yar aiki Nuri zakace zaka koreni, what on earth do you take yourself for? Are you God? Sabida kaganni mace kadauka I am weak ne I can't defend myself? Zakace zaka korini daga gidanka u think bazanyi speaking up ba, Listen Nuri, me and you are two equal people! Baka fini da komi ba, duk inda kasa kafa nima zan iya saka kafan, nasan kimata nasan daraja ta and my worth u cannot downgrade me or downgrade my status and for batamin rai din nan dakayi this night wlh saina batama mamank……." Azuciye Nura yadaga hannu zaikai mata mari kaman daga sama sukaji Aman yace "Daddy!" Chak Nura ya tsaya da hannunshi batare dayakai marin ba, he don't ever wants yaranshi to have a memory of him yana dukan mahaifiyar su, dunkule hannunshi yayi tareda saukewa kasa ahankali yajuyo yakalli Aman din,  dasauri Aman yazo ya rungumeshi tsamtsam yana kuka sosai yace "Daddy sorry kayakuri Mommy is sooo baddd but don't slap her okay Dady, beating girls is not good katuna ranan dana daki Amal haka kagayamin" daukan yaron Nura yayi ya rungume ahankali tareda mannamai kiss akai yama kasa magana yashiga tafiya dashi yana sauka, Hadiza dake kallonsu tace "ai naso ka maren wlh danai suining naka for domestic violence, try that next time kagani I will mess you up Nura" sauka yashiga yi kasa yana dauke da Aman a hannunshi gaban dakin Ummi yakaishi yace "shiga" shiga yayi sannan yajuya yawuce yafita daga gidan yashiga motanshi yamabar estate din gabaki daya zuciyanshi daci takemai da gaske idan Allah yabaka mata nagari wlh ka gode kama kara godemai dan shaidanun mata azaba ne, they will so push you to the wall kaji kaman zaka kashesu, yayi tafiya mai nisa sannan yayi parking yakalli wayanshi yadade yana kallo kafin yasauke ijiyan zuciya

yakai hannunshi yadauka yabude yaciro wani lomba yakira wayan na gab da katsewa aka dauka daga dayan bangaren wata yar dattijuwan manyantaccen murya ne tai magana. “Nura barka da dare ya wurinku yasu Amalily?” Ahankali yace “lafiya lau” saikuma yayi shiru all this years baitaba daga waya yakai karan matanshi ba sai yau jin yanda baiyi magana ba yasa tace “lafiya Nura Maiya faru? Ina ganin wayan nasan da wani abu duba da lokacin dakama kirani, what happened?” Ahankali yace “Hadiza bansan menene damuwanta ba, tunda na auri Hadiza Anty Jamila for once bantaba kokarin takata ba ko shut her up, ni mutum ne dana tsani takurama mata ko basu damuwa I have 4 sisters dukansu mata nataso da sanin yanda ake girmama mace kare mace dakuma daraja mace” Anty Jamila tace “kwarai Nura wannan haka yake zan shaideka ako’ina” ahankali yace “the whole idea da concept na feminism ya shiga kanta, I’m not saying feminism is wrong no, ko Allah yasani inaso naga matata tacigaba, banki duk matakin dazan taka aduniyan nan matata ta takashi ba, I empower her nabata jari tafara business nakaita su dubai oman Egypt dasauran kasashe alokacin sabida ta saro abayoyi tafara, bansan gobeba I believe empowering matata will go a long way for yaranmu incase of gobe dabata da tabbas, bantaba ma Hadiza kallon wata baiwa ko yar aiki ba rather I see her as life partner dina wacce nakeson to go through every phase na Rayuwa together mu tsufa together but ita bahaka take ganin komi ba, gani take anything daya kamata tayi agida nima yakamata nayi nida ita we are equal, yimin girki gaidani bani abinci is not her duty duka abubuwan nima nayi we are equal afterall, gaidani akan me zata gaidani nima na gaidata…” dasauri Anty Jamila tace “subhanallahi” dan ijiyan zuciya yasauke yace “Anty Jamila the whole feminism din nata haukane kawai, rashin kunya menene menene babu wanda bata mini nakasa gane kanta balle kafanta, i can’t even talk to her kafin nayi magana daya tayi dari, Anty Jamila I am tireddddd nagaji, I want peace of mind at this my age” yanda yayi maganan saida yabama Anty Jamila tausayi tasan yanda Nura keda hakuri tasan for Nura yadauki waya yakirata takaishi bango anatse tace “Nura kayakuri kayakuri shikenan abinda zan iya fadi kaga wannan halin shine dalilin dayasa maza da yawa basason bama matayensu freedom har subarsu suyi sana’a dan wasu matan dazaran sun soma taba kudi shikenan sai sudinga jin kansu kaman giwaye suma yanzu sun faso, amman kabarni da ita zan kirata zan kira Mama kuma” ahankali yace “please kada ki sanarda Mama tana fama da hawan jini saisa nakiraki ban kirata ba” murmushi tayi tace “to shikenan amman dan Allah kayakuri” ahankali yace “to saida safe agaida yara” yakatse wayan yadade ahaka yau bacin ran yasa he wanna be alone ma inda bahaka ba zai iya kiran abokan shi yaji inda suke yaje yasamesu, yayi kusan 3hrs awajen sannan yatada mota yabar wajen.

Domin magana dani M shakur koso nasaki a group dina chat me up tanan
wa.me/+2347012181461

Yana katse wayan Jamila ta danna mata kira wayan harya katse bata dauka ba akaro nabiyu ne tadauka tace “Hellooo Anty Jamila” cikin fushi Jamila tace “ke wace irin mahaukaciya ce Hadiza? Ni wlh I don’t even need to ask you nasan kene da laifi dan nasan kalan hakurin Nura tunda yau dakanshi yadaga waya yakirani nasan kin mai babban laifi” tsaki Hadiza taja dayasa Anty Jamila tasake baki, cikin fushi Hadiza tace “ohhh kiranki yayi yahada mini munafinci? To wlh zaizo gidan nan yasameni ina jiranshi” jin yanda yake magana kaman tana jiran wani saran wasanta yasa Anty Jamila tace “Hadiza are you okay kuwa? What has gotten into your head?

Nuran kike magana haka akanshi?” Cikin fushi sosai Hadiza tace “Anty Jams bazaki gane bane, Nuri finds every little way to belittle me, nan Abuja ne fa ba kano ba but kullum so yake ina shiga kitchen namai abinci, a Abuja yan aiki ke girki matan gida relaxing take bayinta namata aiki, inada yar aiki ai nama baki labari wacce nace miki su Aman na sonta, ita ke kula dasu I am busy da shigo gida nawa yake so naraba kaina? Sai nasa yar aiki tamin wani abu yahanata yimin sabida shike biyan kudin shine nacemai yadena daga this month nizan cigaba dabiyanta sabida I should be the one in control of her, ina shago dazu yakirani wai Mamanshi zatazo gobe taga Dr kinji fa Anty Jamila sabida ya rainama kanshi wayau danni bai isa ya rainamin wayau ba, gidan nan belongs to two of us baida right dazai kawo koma uban waye into this house without asking permission dina, what did he take me for eh? Wlh wlh jiransu nake suzo goben dagashi harsu saina kuntata musu bakin cikin da bazasu kara marmarin zuwa gidana ba me akeyi da yan uwan miji banda hauka mtswwww” “Innalillahi wa innailaihi raji’un” Anty Jamila tafadi tana tafi da hannunta cike da mamaki tace “Hadiza giyar kudi ko giyar karatun wannan femi ah’ahhh Feminism ko oho dai ke damunki” Hadiza tace “feminism wai? I know my right I can fight for my right duk inda nake aduniya tunda mata suka gano this feminism sun samu yanci sun samu cigaba, a woman can stand aduk inda namiji ya tsaya aduniyan nan” “dalla rufemin baki sai idea bature yasa kin rasa mijinki tukunna zaki dawo hankalin ki” Anty Jamila tamata ihu tace “wannan ba shine tarbiyan da aka baki agida ba, keda mijinki can never be equal ko awajen Allah domin ko aljannanki na karkashin tafin kafanshi, mata dakika ganmu daga rib guda daya na maza aka hallito mu, kada ki mata, Allah yafadi acikin suratul Nisa’i aya na 34, Arrijalu qawwamuna Alan nisa, bari madai naja miki ayan gabaki daya

ٱلرِّجَالُ قَوَّٰمُونَ عَلَى ٱلنِّسَآءِ بِمَا فَضَّلَ ٱللَّهُ بَعْضَهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍۢ وَبِمَآ أَنفَقُوا۟ مِنْ أَمْوَٰلِهِمْ ۚ فَٱلصَّٰلِحَٰتُ قَٰنِتَٰتٌ حَٰفِظَٰتٌۭ لِّلْغَيْبِ بِمَا حَفِظَ ٱللَّهُ ۚ
وَٱلَّٰتِى تَخَافُونَ نُشُوزَهُنَّ فَعِظُوهُنَّ وَٱهْجُرُوهُنَّ فِى ٱلْمَضَاجِعِ وَٱضْرِبُوهُنَّ ۖ فَإِنْ أَطَعْنَكُمْ فَلَا تَبْغُوا۟ عَلَيْهِنَّ سَبِيلًا ۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيًّۭا كَبِيرًۭا ٣٤

Men are the caretakers of women, as men have been provisioned by Allah over women and tasked with supporting them financially. And righteous women are devoutly obedient and, when alone, protective of what Allah has entrusted them with. And if you sense ill-conduct from your women, advise them ˹first˺, ˹if they persist,˺ do not share their beds, ˹but if they still persist,˺ then discipline them ˹gently˺. But if they change their ways, do not be unjust to them. Surely Allah is Most High, All-Great.

Allah ne yafadi da kanshi, idan kuma u are talking about rights da yanci ne tun zamanin Annabinmu ya kwatoma mata yancinsu idan wani yaji kina magana haka idan ba’asan Nura ba zaa dauka wani abu bawan Allahn nan yake miki, kin sami miji nagari bawan Allah shiru shiru mara magana kinamai irin abubuwan nan ke kinada baki kice sai da izinin ki mahaifiyarshi zatazo gidan danda tahaifa, matan da komu nan last week saida muka kirata muka mata yajiki wlh maganan ki yasama ina jin kunyan Nura, Hadiza sau nawa da ni da yarana harda Mama muke zuwa gidan ki every now and then duk wani abu dazai shigo damu Abuja gidanki ne masaukinmu we don’t even ask for permission sabida anzama daya, ace yau mahaifiyarshi zatazo for treatment na rashin lafiyanta kina maganganu haka ina imanin ki? Wani kalan tsantsan son kai ne wannan”? Cikin kunkuni Hadiza tace “ai dama side dinshi zaki dauka nasani mutum yana nema ya maidani yar aiki bazakice komiba ace nine zan shiga dakinshi na gyara namai girki bayan inada yar aiki mai yi” Anty Jamila tayi shiru na kusan 5min sannan tace

“danace basai na sanar da Mama ba but Hadiza kinyi nisa Mama dole ta shigo zancen nan, yar aiki itane ke gyara dakin mijinki tamai girki? How many minute zai daukeki kima mijinki girki? Bawai nace yar aiki is bad bane ai ko ni inada yar aiki tadan taimaka maka da one or two things but that does not mean zaki barmata ragaman gidanki menene haka Hadiza ke kina ganin wayau ne hakan kin cika yar boko ko? Kin waye  kinada kudi kinyi kawaye matan Abuja kema kin dauki sahunsu kirasa wanda zaki mawa sai mutumin da shine yabaki jarin mutumin that made u Hadiza” ihu Hadiza tayi tace “me  aciki Anty Jams ai sai nabiyashi kudin daya kashemin nafara business din harda riba indai hakan zaisa yafita harkata yabarni na Sarara nayi yanda naga dama” dasauri Jamila tace “wai kinsan wane kike aure kuwa? Nura fa kampanin shi shike tashe yanzu ko su cosgrove abayansu suke, ga kyau ga aji ga hakuri baki tunanin yazo yahadu da wata kinamai haukan nan yakaro aure abinshi” har cikin ranta Hadiza taji maganan ya soketa dasauri tace “Nuri baida ra’ayin mata biyu tun kafin muyi aure yamin alkawarin ni kadaice matarshi har abada and Nuri baya taba karya alkawari, he’s a man of his words” dan murmushi Anty Jamila tayi tace “to inhar bakison alkawarin nan ya karye take care of mijinki ki sauke pride din nan youu are under him and u will always be, kidaina mai kallon keda shi are equal kina rainashi, keda mijinki can NEVER BE EQAUL, and Bari nagaya miki ki gaggauta gyarawa kafin Nura ya rufe babinki yabude sabon babi,_ saida safe kuma zan sanar da Mama yanda mukayi” ta katse wayan batare data karabi takanta ba shiru Hadiza tayi tana kallon wayan ranta ya mugun sosu da kalman kishiya. Da Yayanta tayi tsaki tayi ta yarda wayan gefenta tace “shiya isa yama mini kishiya, tsorona bazai ma barshi yayi wannan kuskuren ba, banda hakama mata basa gaban Nuri sai business kuma Nuri baida ma yawan sha’awa kaman nine saimuyi watanni bamubi takan shimfidan juna ba ninama fison haka dan ba haihuwa nakeson nakarayi ba inaso nai maintaining this body da shape shi aina zai taba samun kyakkyawan mata fara hausa fulani komi yaji irina” tayi dan murmushi tanajan bargo takoma bacci abinta.

MAISA WASU MATAN KE GANI SUDA MAZAJENSU ARE EQUAL????

💫MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE5️⃣
Ummi kwata kwata takasa runtsawa koyaya ta kulle ido ganin lokacin da Alhaji ke kallonta take, da yanda ya kula da ita dazun dinnan the same way yake handling su Aman that’s yanda yayi handling nata, abun yaki fita daga zuciyanta, the entire scene ya narkan da zuciyanta sosai dan har yanzu kamshin turarenshi takeji yanda yazo dab da ita, she can still feel dadin kamshin iskan bakinshi lokacin daya hura mata, mirginowa tayi daga dan katifan datake kai zuwa kasan tiles, sanyin tiles din yawani kara tsuma zuciyanta ta bude idanunta tana kallon POP sama fuskan Alhaji take gani wlh Alhaji akwai karisma da haiba dawani irin kyau ahankali tace “inama

ya aureni" dawani kalan sauri tadaura hannunta saman bakinta kaman irin wacce tafadi taboo din nan, tayi aiki agidaje 4 wannan ne na 5 bata tabajin kaman mijin ko Alhajin gidan datake aiki ya aureta ba sai wannan sabida yanada mugun kirki, gashi da sanyin zuciya, sannan yanada natsuwa, yanada daraja mutane sannan yana son yaranshi sama da komi kawai mata ce baiyi sa'a ba wlh inda itace matanshi ko zaiga gata dan miji irin Alhaji da baida matsala hakan nan wlh kula zatayi dashi sama da yanda yake kula dasu Amal ma kula zatayi dashi kaman wani jariri tana bashi duk abinda yakeso aduniya, ahaka bacci yayi awon gaba da ita da tunanin Alhaji aranta.

Wuraren 1 yashigo gidan da kanshi ya kwaso duka kayan daya sayo dazu na cefene yakai kitchen ya ijiye komi sannan yawuce sama dan kwanciya.

As usual biyar yafito sanye da jallabiya tunda yabude kofanshi kamshi ya daki hancinshi ahankali yake sauka daga staircase harya karasa sauka kasa wutan ko'ina akasan akashe wutan kitchen ne kawai akunne ga kofan kitchen din abude wajen dinning yaje ya tsaya yana kallon kitchen din Ummi yagani tana girke girke daban daban ga su lunch bag na Aman da Amali akan island yau zasu school, tana sanye da Riga da skirt yana ganin kayan yagane su kayan Hadiza ne tun tana yammata sun kode sosai amman dudda haka sunma Ummi kyau that means tayi wanka kafin tashigo kitchen folding hannunshi yayi yana kallonta tundaga kan slippers green dake kafanta zuwa kanta dake daure da dan kwalin atampan jikinta, tanada tsayi sannan tanada hips dudda ba sosai ba but sunada curve irin yaran nan ne da suna samin kula zasu cicciko yanzu wahala ne yasa suke looking haka ma, dan lumshe idanu yayi yabude ya tsare fuskanta da kallo ahankali Yatambayi kanshi am I falling for this girl? Dan ijiyan zuciya yasauke yajuya yawuce yafice zuwa mosque yana deep tunani shiba yaro bane yasan when zuciyanshi keson abu.

Wuraren 7 nasafe yashigo gidan Hadiza yagani a dinning taci gayu sosai cikin wani exclusive atampa ta buga dauri tanacin lafiyayyen breakfast chips da pepper soup sai shayi agefe, itakuma Ummi na tsugunne a tsakiyan falo tana feeding Amal a baki Aman na kusa da su daduk ta shiryasu cikin kayan makaranta suna ganin babansu da gudu sukai wajenshi. "Daddyyy Assalamu Alaykum Dady ina kwana" murmushi yayi yadauki kowannensu yamusu peck yashigo dasu falon yace "ku karasa breakfast yanzun nan school bus zaizo" basuyi musu ba suka koma, anatse Ummi da kanta ke kasa tace "ina kwana Alhaji" batare daya kalleta ba yace "fine" sannan yadau remote yana chanza tasha 8 zai fita hakan yasa kawai ya ijiye remote din yawuce sama ko kallon HADIZA baiyiba itama bata kalleshi ba saima karasa cin abincinta datayi tawuce tadauki car key tace "ki dafamin couscous da daddare ke" ahankali Ummi tace "to Anty, saikin dawo Allah bada sa'a" yatsine fuska tayi bata amsaba tawuce tafita tashiga motanta tabar gidan, bata dade da fita ba motan su Amali yazo Ummi takaisu suma suka wuce tafito tana gyara wajen taje dinning ne ta gyara inda Hadiza taci abinci sannan tawuce tana duba girkin datake ma Kakan su Amal dazata zo, tana cikin tuka tuwon Alkaman taji kamshin turare dasauri ta juyo hada ido tayi da Nura daya shigo kitchen din yasa wani blue gizna shadda wlh yayi kyau na bugawa a jarida faduwa gabanta yayi dasauri ta dauke kai ta saki muciyan a tukunya zata duka yace "cigaba da abinda kikeyi" batai musu ba tacigaba saikuma tadan juyo

hada idanu suka sakeyi ahankali bakinta nadan rawa tace “kana bukatan wani abu ne Alhaji”? Dan girgiza kai yayi yaja daya daga cikin kujerun dake gaban island din yazauna yace “me kike tukawa”? Atsanake tajuya takalli tukunyan tace “tuwon Alkama, kace Hajiya da safe zata iso saisa nake mata nasan basuyi kari ba suka shiga hanya, itakuma sister ka zan dafa mata abu daban” yana kallonta yace “nikuma fa” dan kallonshi tayi ga mamakinta murmushi yasakan mata dasauri tace “breakfast dinka nakan dinning amman idan kanason wani abu daban ne zaka iya fadamin namaka yanzun nan” “hmmm!” Yasauke ijiyan zuciyan dashi kanshi baisan karanta yafito ba maganan yatabamai zuciya dan wannan ne abinda matanshi bata tabamai ba just look at yanda yarinyar nan tabashi girma da daraja da kima kome yakeso yafadi zatamai that king treatment shitake mai, kawai saiya dago yakalleta yace “dafamin shayi mai kayan kamshi” dasauri tace “to” zare muciyan tayi daga tuwon tadan diga ruwa ta rufe tarage heat din tawuce ta wanke hannunta tashiga hadamai shayi shikuma yaciro wayanshi yana tabawa dan kawai tasaki jiki amman wlh kusan kome takeyi idanunshi binta suke, nan da nan tahada shayin tadauko wani hadadden flask jug tazubamai tasaka a tray tadauki cup da spoon da sugar kaga yanda take plating zaka dauka taje culinary school ne nan ko tsabagren experience ne a aikatau, tadauko tray din tazo har gabanshi ta ijiye sannan ta duka tace “nazuba maka?” Ahankali yace “yes” mikewa tayi yana kallon hannunta farcenta farare kal dogaye masu kyau tazubamai tace “sugar cubes nawa zansa ko asa zuma?” Kaman wani yaro dan he’s just enjoying the way take neman permission nashi for komi this is luxury da baya samu yace “zuma” dasauri tajuya tafita daga kitchen din taje dinning tadauko zuma takawo ta zubamai sannan tajuya tadauki cup din tadaura kan tray nashi tajuyo tabashi kallon fuskanta yayi sannan yasa hannu ya amsa yace “thank you Ummi” wucewa tayi takoma wajen tuwon tashiga kwashewa kaman daga sama taji yace “waye Mudin kauye?” Juyowa dasauri tayi takalleshi hada ido sukayi yana kurban tea juyawa tayi tacigaba da kwashe tuwon tana mamaki a ina yatabajin takira sunan Mudi saikuma ta sauke ijiyan zuciya tace “tsohon miji na ne” dasauri Nura yakalleta yace “kin taba aure”? Gyadamai kai tayi tace “eh amman an dade tun ina shekara sha uku-sha hudu aduniya” yana kallonta yace “meya rabaku”? Tsayar da kwashe tuwon datakeyi tayi saikuma ta kalleshi yanda ya tsareta da ido yasa ahankali tace “dukana yake, kullum kullum duka, hakanan kaman idan bai dakeni ba bayajin dadi rayuwanshi, shine…..” takasa maganan tai shiru takai hannu ta goge hawayen dasuka zubo mata dasauri tajuya tacigaba da kwashe tuwo Nura yace “shine meya faru”? Ahankali tana kwashe tuwon tace “shine rannan dayamin wani bakin duka saida na haifo bakwaini, inada cikin wata shidda lokacin, amace yafito yaron, saida nayi jinya na kusan shekara daya inata fama da yoyon fitsari, Gwaggo na ta hadashi da mai anguwa akan saiya sakeni kuma abimini hakkina dan ya illata mata jika tun bayan haihuwan dole dayasa nayi ban warkeba, to da kyar yasakeni amman dudda ina rashin lafiyan yakan biyoni har gidanmu yamin duka har suma inayi, ko baizoba kullum cikin fargaba nake zaizo, Maman mu tarasu Gwaggo mu ce kadai garemu kuma batada karfi ta tsufa, ahaka dai na warke but ina cikin tsoro kullum, saisa dataji wata mata dake zuwa kauyenmu kwasan yara aiki taje ta roka da kyar akace za’a daukeni, to aboye aka fitar dani daga kauyen mu kada Mudi yaganni, tundaga nan nazo birni tun ban gane abubuwa harna gane yanzu nima, amman inaso nakoma kauyenmu naga Gwaggo na da kannina Salamatu tai aure harta haihu Maimuna da Ikilima ne za’ayi bikinsu kwanan nan kuma inaso naje amman Gwaggo na bataso nazo tsoro take kada nakoma kauye Mudi ya kasheni, yanzu ance yafi da

zama takadiri ya gagari kowa, tsoron shi ake har mai gari, amman nayi kewan garinmu da gidan mu da Gwaggo na da kannina sosai bansan ya Allah zaiyi dani ba bansan kozan kara sa kafa a kauyenmu ba" tai maganan tana kai hannunta saman fuskanta duka biyun tadanyi sheshekan kuka mara sauti, shiru Nura yayi yana kallonta tabashi tausayi sosai ahankali yace "kinaso nakaiki kauyenku kiga yan uwanki"? Dasauri tazare hannayen ta dagakan fuskanta takalleshi da rinannun idanunta yanda ya tsareta da idanu yasa gently ta gyadamai kai, murmushi yayi yace "I promise zan kaiki kauyen ku, and namiki alkawari ba Mudi ba ko mudari yake bai isa yamiki kallon banza bama balle ya dakeki kinji" gyadamai kai tayi ahankali, murmushi yadan mata yace "kada ki kara kuka bayama fuskanki kyau" akunyace tai murmushi shima murmushi yayi yace "idan Hajiya tazo dazaran nagama kata katan asibitin ta zan kaiki gida ko" gyadamai kai tayi dasauri, tashi yayi yakalli agogon hannunshi yace "bari natafi daukosu nasan jirginsu yatashi yanzu kafin nakai airport sun sauka, kinason nasayo miki wani abu"? Yamata tambayan da saida ta kalleshi da mamaki ganin ya tsaya yakuma tsareta da ido tace "Amali tadameni tun jiya zatasha yoghurt babu yoghurt agida" jinjina kai yayi irin yaji din nan yace "ke me kikeso"? Sunnar da kanta kasa tayi akunyace tace "slippers wannan yakatse dazu na naneshi da wuka mai zafi saisa na iya sawa" yanda takejin kunyanshi na burgeshi sosai, anatse yace "to" yajuya zai wuce dasauri tace "Nagode Alhaji Allah kara girma, saika dawo Allah ya tsare" juyowa yayi yace "Ameen Hajiya Ummi" dasauri takalleshi wucewa yayi yafice yana murmushi mota yashiga, saida yafara tsayawa a super market yayi sayayya harda cream da shower cream mai kyau yasa mata da su turaruka da wasu abaya daya gani a super market din da idanu ya gwada tsayinta haka yabiya kudi yafito, haryakai airport labarin Ummi yake tunani yaushe kauye zasu dainama yara Auren wuri ne haka, yanzu sabida wani katon mugu aka koro yarinyar nan aiki, yayi traumatizing nata tun tana 14, small girl fa, hmmm Allah ya kyauta.

Daidai yana parking awajen parking wayan Amina nashigowa fitowa yayi daga motan yana daukan wayan yace "okay ku jirani a arrival din gani nan zuwa" wucewa yayi tun kafin su ganshi ya hangosu, wata tsohuwa ce fara mai zanen kalangu a fuskanta zaune kan wheelchair dawata budurwa da akalla zatai tsaran Ummi ke gungurawa ga akwatinan su kan cart a gefe tareda mutumin dake turawa, ahankali tsohuwan matan tadago idanunta dan taji alamun danta ajikinta hakan yasa sai waige waige take, ta baya yazo yahada idanu da Amina daya mata alamun kartai magana sannan yataho kawai Hajiya ganinshi tayi agabanta ya tsaya bai damu da airport sukeba tsugunnawa yayi yasa guiwowinshi akasa yana kallon fuskan mahaifiyar tashi data washe baki ganinshi tace "me haka tashi tashi kayanka zasu baci, yanzu kasan banda karfi balle na wanke maka" ahankali yakai duka hannayenshi yatallabo fuskan mahaifiyan nashi yace "bance kada ki kara ciwo ba eh Hajiya?" Cikin barkwanci tace "ai dazai tasomin saida nace kai rashin lafiya ka manta kashedin da Nura yamaka ne kakeso kadawo kuma" dan murmushi yayi duk rashin lafiyan Hajiya bakinta is always there baya fatan tai rashin lafiyan dazai hanata magana har abada In sha Allah. Rungumeta yayi ahankali yace "barka da zuwa Mamana, Allah yabaki lafiya Hajiya, Allah yasa kaffara ne" bayanshi ta shafa tace "Ameen Ameen ai naji sauke Amina ai bata kyautamini ba banso ta tadamaka da hankali ba wlh, tashi daga kasa kaga jama'a sai kallemini d'a suke yasa guiwa akasa" batare daya saketa ba yace "albarkan mahaifiyata nake so" murmushi tayi tace "Allah maka albarka Nura, Allah ya lura dakai kaman yanda kake lurada ni, Allah yasa yaranka sumaka yanda kamini Nura, yanzu tashi mutafi kaji

dan albarka" anatse yace "to Hajiya" sannan yadago yabama mai cart hannu suka gaisa sannan yakalli Amina hannu yabude mata dasauri ta rungumeshi tace "Yaya ina yini" kanta yashafa yace "lafiya lau Autan Hajiya" wheelchair ya karbe yashiga tura Hajiya da kanshi har mota saida ya zaunar da Hajiya tazama comfortable sannan ya sallami mai cart suka shiga mota suka tafi, Hajiya sai kallonshi take ta madubi tanamai hira tace "amman kai rashin lafiya ne ko Nura? Naga kafada sosai"? Dan murmushi yayi yace "aiki ne wlh Hajiya" ijiyan zuciya tasauke tace "to Allah yabaku sa'a kadinga hutawa kanacin abinci akai akai kaji ko" "to Mamana" ya amsa yana murmushi, tace "nataho maka da danderu" baki yabude yadan juyo zai kalleta dasauri tace "kul maida hankali tuki kake" dan dariya yayi yace "Meenah ya akayi akabar Hajiya tawuce da danderu"? Dan dariya tayi tace "ba anga batada lafiya ba babu wanda yayi musu da ita" murmushi kawai yayi yace "inason Mamana Ameena sosai" Hajiya data washe baki tace "nima inason d'ana sosai" Ameena ta turo baki tace "Hajiya nifa" dan dariya Hajiya tayi tace "Inason ku duka akwai wanda ma yasamu soyayyata irinki Auta na" ahaka suna family hira sukakai gida Nura yace "specialist danai consulting yace zai ganmu by 12 yanzu zakici abinci kihuta anjima saimuje asibitin ko" yayi maganan tareda yin Parking yafito da ita sabida dakali da kafanta tayi tafiya tana rikeda shi suna tafiya ahankali Ameena biye dasu tana kallon hadadden gidan, bude kofa sukayi suka shiga ciki wani lafiyayyen kamshi yamusu sallama dasauri Ummi tafito daga kitchen tazo har tsakiyan falon ta duka tace "sannu da zuwa Mama, ya hanya ya jiki, Allah yabaki lafiya Mama, Allah yasa kaffara ne" washe baki Hajiya tayi tana kallon Ummi tace "waye wannan yarinyar mai ladabi ba irin su Auta ba da basu gaida mutane da kyau, ga iya addu'a, waye ita"? Dan murmushi kadan Nura yayi yace "Ummi sunanta" daidai Hajiya na zama, Hajiya tasauke ijiyan zuciya tace "jiki Alhamdulillah Ummi, sannu kinji Allah miki albarka tashi tashi ki zauna, ina Hadiza? Nasan jikoki na ana makaranta ina Hadiza?" Hajiya takara tambayan da zuciya daya tana waige waige neman Hadiza, cikeda hikima Ummi tace "tadanje tadawo wani uzuri yakamata amman tace na kula dake da kyau kome kikeso namiki" sosai Nura ke kallon Ummi yanda yarinyar keda hikima baitaba sanin zata iya fadan magana hakaba, dariya Hajiya tayi tace "ayyooo" kallon Amina data shigo da jaka Ummi tayi gateman biye da ita da kayansu da sauri ta tashi tace "kawo nakai miki daki jeki zauna kihuta kinsha hanya" murmushi Meena tayi tace "thanks" kai kayan sukayi sama sannan Ummi tadawo tashiga kitchen a tray tajera abincin Hajiya da ruwa a bowl mai kyau na wanke hannu tafito takawo har gaban Hajiya, Hajiya tace "Ayyah sannu da aiki Ummi, Allah dai yasa cimata ne dan yanzu bakomi nakeci ba, cuta batayi ba" tai maganan tana bude kulan ganin tuwon Alkama da miyan zogale dayaji ganye yasa Hajiya tace "laaaaaaa Hadiza tamin girkin nan kafin tafice" dasauri Ummi tabude baki zatace eh Nura yace "Ummi ta dafa miki Hajiya" kara kallon Ummi Hajiya tayi saikuma ta nunawa Meena Ummi tace "kinga girkin sa'onninki ko ke sai shegen kiwuya, wai wannan kamshi haka bari naci abincin nan akasa zan zauna ma" da taimakon Nura tazauna akasa ta wanke hannu takai abincin baki saita kalli Nura takuma kalli Ummi takara kallon Nura again tace "Ummin nan dai danake gani tai girkin nan"? Gyadamata kai Nura yayi sai kawai Hajiya tace "Allahu Akbar wlh tayi girkin yanda nakeso, kaga ba gishiri ba magi, sannan bata sakamin jan nama ba hanta da Koda kadai ne amiyan, cimata tamin kuma yanda nakeso, bani jakana Meena kigani" bata jakanta Meena tayi Nura ya karba, dasauri Hajiya tace "ciro duka kudin dake purse dina" murmushi yayi ba musu yaciro dubu goma da dari biyar ne ta karba tamikama Ummi tace "ga tukuicin ki dan kin dadada mini rai kinsa natuna na diyata Aisha mai bin Nura

tana aure a eygpt ita kadai kemini abinci irin wannan taste din  wannan tarban da akamin bazan taba mancewa da ita ba, nagode ko Ummi amshi kudinki” akunyace tace “Mama kibar shi ni nadafa miki ne kawai wlh” Hajiya tace “laaaa ungo amshi nace” dan satan kallon Nura tayi shima kallonta yake ahankali yace “bazaki amsa kudin Hajiya ba kinsan kalan makon Hajiya kuwa? Ba kasafai akecin kudinta ba, ke kinyi sa’a tabaki” dariya duka sukayi harda Ameena, Hajiya tace “atoh dan haka karbi abinki” gently Ummi tasa hannu ta amsa ahankali tace “nagode Mama Allah ya ninka miki dubun su” Hajiya tace “Ameeen Ameeen” Ummi na murmushi takalli Ameena tace “nadafa miki shinkafa dafa duka dakuma taliya na manja wanne zan kawo miki” dasauri Ameena tace “taliyan manja” harzata tashi saikuma tadan kalli Nura dake kallonta kasa kasa tace “Alhaji mezan kawo maka bakayi breakfast ba kaima” abincin Hajiya yakalla yace “zanci abincin Hajiya” gyadamai kai tayi tawuce kitchen karaf akan idanun Hajiya yanda Nura ke kallon yarinyar amman batace komi ba, saida sukaci sukai kat Ummi takawo mata juice na cucumber kadai data mata Hajiya tasha sosai sannan Nura yakaita sama dakinsu dakin dake kusada na Hadiza inda Hadiza ta kwana ranan ta gyara Hajiya ma sai complain take ita batason sama Nura yace yafiso ta kwana inda zai dinga jin motsinta hakanan ta hakura.
Wuraren 12 suka fice asibiti Ummi tasake gyara gidan.

Sai wajajen shidda saura suka suka shigo gidan da gudu daga Aman har Amal sukazo suka rungume kakansu abinci Ummi takawo, tama Hajiya unripe plantain porridge datasa shuwaka da bushashen kifi da daddawa aciki shima ba maggi ba gishiri sai kamshi daddawa da kifi sun bama abincin taste, tayi jellof rice da naman rago ma sauran mutane, duk suka baje harda Nura za’aci abinci anan falo, Ummi takoma gefe ta duka Hajiya tace “kema taho nan kici, an taba haka ki mana girki saiki koma gefe, tahonan” dan satan kallon Nura tayi shi harya faracin faten Hajiya ma, da idanu yamata tazo nan,  hakanan taje tashiga cikinsu suka faracin abinci, ita da Ameena da su Aman shinkafa sukeci, tunda tafara aiki yaune rana na farko data ji kaman tana gidansu Hajiya ne Gwaggon ta Amina kuma yan uwanta, sai hayaniya su Amal keyi anacin abinci, no wonder Alhaji keda kirki mahaifiyar shi batada matsala at all. Nura yace “Hajiya dan ban juice din cucumber dinki nasha” jug din Hajiya ta kalla tace “kai Nura na tsammaka na tsammaka harna gaji da sammaka wai kaine mara lafiyan nan ne”? Dariya akayi Ummi itama dan boye dariya ta tayi ganin yanda Hajiya keda barkwanci, takalli Nura tace “inje inmaka kaima Alhaji”? Batare daya kalleta ba yace “a’a kihuta zansha na Hajiya” kofi Hajiya ta dauka ta tsiyaya mai rabi ya karbe ita ta shanye rabin tace “Allah miki albarka Ummi zaki koyama wannan shashashan Autan nawa kafin mu koma” gyadama Hajiya kai tayi, Hajiya tace “Auta dukta cinye ke bakici komiba” dasauri Ummi tace “naci sosai wlh” kashigo falon ji zakayi inama haka farin ciki zai dawwama agidan, Nura yana lura da yanda bini bini Ummi kecin abincin tana duba Amal da Aman, chan kuma saita debo tai feeding Amal da mostly wasa take da abincin at this point bazaiyi karyaba yarinyar ta shiga ranshi sosai barinma dayaji labarinta dazu, yaji ta taba aure har ta haihu dudda pre matured birth tayi amma saiyaji yakara natsuwa da ita, wato saisa takeson yaranshi kuma saisa takeda hankali koba komi tanada experience, baison yayi mu’amala da yara masu danyan kai that knows nothing akan aure koba komi tasan menene aure kuma tayi zaman aure, tayi rainon ciki, sannan tayi nakuda, hakan is perfect for him.

Sake lura da yanda yake satan kallonta Hajiya tayi daidai nan aka bude kofa aka shigo dukansu suka dago kai cikeda fara'a Hajiya tace "oyoyo oyoyoo, sannu da dawowa Hadiza" tundaga inda Hadiza ke tsaye tabi kowa na falon da kallo da yanda falon yayi kacha kacha dudda bawai kacha kachan yayi ba kayansu ne jaka da gyaluluwa dasuka zuba akan kujera dan dawowansu kenan Ummi ta taresu da abinci sai abincin da Amal da zuzzubar a falon rice din, daidai nan idanunta yasauka akan Ummi dake cin abinci tareda Amina dakuma yaranta akasa tana kokarin bama Amal abinci abaki hankalinta kwance dan akasa take zaune technically batayi laifi ba yau. "Ke menene aikinki? Jibi yanda gidana yayi kacha kacha zama kikayi kinacin abinci? Kina yar aiki waya gayamiki kinada darajan zama inda mijina yake kici abinci eh"? Yunkurawa Ummi tayi jikinta yayi sanyi zata tashi dasauri Hajiya tace "dakata Ummi" takalli Hadiza dake tsaye awajen da taje tace "ninace taci abinc……" "Hajiya dan Allah kidakata badake nake magana ba" Hadiza tayi maganan rai abace dasauri daga Nura har Ameena suka juyo suka kalleta da mugun mamaki itama Hajiya tayi tsuri tana kallonta dan batasan haka Hadiza tazama tasan ta dai da rashin son aiki ko sunzo babban salla Kano dama ba zama take agidanta ba saidai ta gudu gidansu so bata wani zauna da Hadiza one on one na dogon lokaci ba, ganin abun zai zama wani kala yasa dasauri Ummi ta tashi zata juya strictly Nura yace "dawo ki zauna kicigaba da cin abincin ki" cikeda tsoro Ummi takalli Nura gabanta na faduwa tadan kalli Hadiza dake kallonta rai abace ahankali takoma ta zauna abun ya mugun mugun yima Hadiza ciwo dan yaune rana na farko daya nuna bata isaba agaban yar aikin yawanci ba agaban idanunta suke tsiyansu ba, zuciyanta wani kalan baki yayi takalli Nura tace "muzuba nidakai badai anzo har cikin gidana ana nema ajuyamaka kai ba tun yanzu an fara kulla kisisina da shairi ko da sunan rashin lafiya amman bakin mutum rass yazauna yana zakalkalan abinci to wlh muzuba dani dakai" Ameena jitayi kirjinta na tafarfasa badan Ya Nura na zaune wajen ba da wlh saita durama Hadiza ashar wucewa tayi fuuuu tayi sama kunyan duniya rufe Nura yayi abinda matarshi tama Hajiya jiyayi ma abincin ya isheshi kowama hatta yaran jisukayi abincin ya ishesu Hajiya ta kalli Ameena tace "tashi keda Ummi ku gyara wurin" kunya yasa Nura yamike yama kasa kallon kwayan idanun Hajiya yajuya yace "bari nazo Hajiya" baima jira amsanta ba yafice dasauri Hajiya tabishi da kallo saitaji dan nata yabata tausayi.
Kayan daya sayo dazu yasa mai gadi ya kwashe yakaima Ummi sannan yaja mota yabar gidan.

Abin yama Hajiya ciwo sosai, ya sosa mata rai, ta haifi yaran dasuka girmi Hadiza, yaranta mata uku biyu sunyi aure saura daya, ita Hadiza zatama rashin kunya haka. Dawowa daga kitchen Meena tayi ganin ba Yayanta awajen tazauna kusada Hajiya tace "Hajiya Hadizan nan yar iska ce kuma wlh wlh ta ijiye iskancin ta a inda tasabayi let her not try that nonsense da ke inba hakaba ni kadai na isheta wlh dan idan nakira su Ya Aisha har gida zasuzo sumata shegen duka ba Egypt ba Ya Aisha zata iya barin  ko'ina take aduniya tazo muma duk wacce ta zageki shegen duka……" hannu Hajiya tadaga mata tace "banson maganan nan Auta, Matar yayanki ne"  cikin fushi Meena tace "koma waye dama nasha gayamiki halinta tunda kika fara rashin lafiya sau daya bata taba kiranki taji yajikinki ba, yar iska kawai mahaukaciya wacce batasan darajan iyaye ba idanma kinci abinci na kanin ubanta kikaci kona danki, okay saitaga kina

shurin mutuwa ne zatasan baki da lafiya dakikiya kawai" Hadiza dataji duka maganganun Meena dan saukowa tayi zataci abinci takoma sama saikuma gobe, takarasa saukowa takalli Ameena dabama ta lurada itaba tace "did u just call me dakikiya Ameena"? Dasauri daga Hajiya har Meena suka juyo suka kalleta Meeena zatai magana Hajiya taja hannunta cikeda hikima irin na manya tace "a'a badake takeba Hadiza wani labari take bani daya faru a kano" kwafa Hadiza tayi tace "gwara dan wlh dasaita bar gidan nan yanzun nan kema kibita" fizge hannunta Meena tayi daga hannun Hajiya tamike tsaye tai wajen Hadizan dan rainin wayon ta yayi yawa ta nunata da hannu tace "an kiraki dakikiya dake nake Hadiza idan baki koreni daga gidan nan ba baki cika yar halas ba" Hajiya datake daga zaune tahau yunkurin tashi tana kwalama Meena kira itama Ummi tafito daga kitchen da gudu  tazo wajen yaran ma haka daidai Hadiza na nuna Hajiya tace "kinga dakikiya chan not me" Meena batai wata wata ba ta daurama Hadiza mari abaki jikake tasss!!!! Haba sai jini Hadiza ta kurma ihu tadaura hannunta kan bakinta dataji lema lema tacire hannu taga jini ahaukace tace "ni kika mara"? Ta chakume gaban rigan Meena da karfi, dambe sukahauyi ba kama hannun yaro Hajiya tafashe da kuka sosai Ummi tashiga rabasu amman ina basa rabuwa, dukan juna suke sosai bana wasa ba, Meena ta fizge ribbon din gashin nan taja gashin kaman zata cire mata su daga tushen kwakwalwa, da gudu Ummi tayi waje Mai gadin su takira yazo da kyar aka iya rabasu aiko Meena ta bala'in lallasa Hadiza bakinta sai jini yake ta yayyakusheta a wuya da hannu, dudda itama Meena ta daku a hannun Hadizan amman bata sami any ciwo ba kaman yanda tama Hadiza kowa sai nishi yake, shiga tsakaninsu gateman yayi Ummi tarike Meena tace "dan Allah kuyakuri" cikide zuciya Meena tace "kada kice na yakuri Ummi ba'a haifi wacce zata zagan mini uwa agabana banyi wani abu ba, am I even my mother's daughter idan agabana za'ahau zagin Mamana nai yi shiru eh? Is she mad? Ba'a bata tarbiya agidan su bane? Idan ba'a bataba ni I will give u, dagayau kowace uwa kika tashi zagi zaki tuna diyar wata ta taba miki duka dakika zagan mata uwa, you are very very very stupid to insult Hajiya kinji, shegiya mai halin matan da iyayensu sukama baki" cikin ihu da kururuwa Hadiza tace "wlh, wlh, wlh yau saina kulleki a police station na rantse da Allah, ni kika daka kin san wacece ni anan Abuja? Number one, the most successful business owner anan Abuja, kinsan award guda nawa ke cikin office dina? BBC  waye waye duk anyi hira dani, nizaki zo har gidana ki daka? Wlh wlh u are a small girl yau zan nuna miki your place" tana maganan tayi kofa bayan ta fincike key nata awajen tray na car key ta shiga motanta tafice dasauri Ummi tasaki Meena tayi wajen Hajiya dake kuka shikuma gateman yace "ayi hakuri ayi hakuri" yawuce yafita.

Dukawa Ummi tayi takai hannunta tana sharema Hajiya fuska tace "Hajiya kiyakuri" da kyar Hajiya ke iya magana tace "Ummi kiramini Nura gobe goben nan zan koma gida  Meena batajin magana nasha gayamata zuciya batakai mutum ko'ina, kowani zagi Hadiza tamini sai mene ita ta zaga basaita bartaba akanme zatai dambe da Matar yayanta eh akan mene daga zuwa na garin nan yau yau din nan? To ko warakata na nan nahakura kiramin Nura idan akwai jirgi yanzun yanzun nan ma komawata zanyi kano" yanda Hajiya ke kuka tana bama Ummi wayanta yasa takira Nura, yana dauka yace "Hajiya" ahankali tace "nice kazo gida Hajiya na nemanka" hakanan jikinshi yabashi wani abu daman baiyi nisa ba duka duka yana ta gaban estate nasu fruits yaje saya yasan yanda Hadiza tadawo saitai rashin mutunci saisa baiyi nisa ba at all dasauri ya katse wayan, ijiye wayan Ummi tayi tadauki Amal dake kuka sosai ta goya Aman ma ta lallasheshi dan duk kuka suke sunga anci uwar Maman su, taje wajen Meena dake wajen

dinning zaune akasa yanda Hajiya ke kuka yasa she's feeling so guilty dan yanzun nan hawan jininta zakaga yatashi, yana isowa gidan ko parking baiyi da kyau ba yafito yashigo gidan Hajiya yagani tana kuka sosai yaranshi suma kuka Ummi sai jijjiga Amal take ga Meena akasan dinning idanunta sunyi jazur kayanta ya chukurkude kaman wani abu yafaru dasauri yayi wajen Hajiya ya duka yace "subhanallahi hajiya menene haka?" Cikin kuka tace "kaga Ameenatu yarinyar chan bazata taba daina jamini bala'i aduniya ba, duba jirgi yanzun nan idan an samu mukoma kano nahakura da asibitin Nura bazan iyaba bazan iya da tashin hankali ba" rungume Hajiya yayi yace "ya isa Hajiya ya isa daina kuka muje ki kwanta gobe da sassafe saiki koma" yay maganan trying to just calm her down, yace "ya isa ko I'm here now, everything is gonna be fine".

Sama yakaita yana zuwa wani allura yamata a hannu da Dr yace adinga mata idan anga hankalinta yatashi nan da nan bacci yadauketa yasauko kasa yazo inda Meena take zaune yace "Meya faru?" Baki tabude zatayi magana saikuma tafashe da kuka cikin kuka tafada mai duka abinda yafaru batai karyaba zaiyi magana daidai an bugo kofa an shigo Ummi ce dawasu yan sanda guda biyu ta nuna Meena tace "officer ga tachan" tashi da sauri Nura yayi yana kallon Hadiza da yan sandan guda biyu wanda ganin Nura yasa basu karasa shigowa falon ba duk suka tsaya anan mini parlor dasauri yakaraso inda suke ya mike musu hannu yace "officer lafiya"? Mutumin yace "Madam dinka ne tashigar da kara kan mother Inlaw ta da sister Inlaw sunzo har gidanta sun mata taron dangi anmata duka, kuma munga shaida bakinta da wuyanta saisa muka biyota muyi arresting sai amusu sulhu a police station" ijiyan zuciya yasauke yajuyo yakalli Ummi dake faman jijjiga Amal tana kuka tarike hannun Aman yace "ku tafi sama keda Meena dakin Hajiya ku rufo kofa" dan yasan Hadiza zata iya kamasu da duka kuma, gyadamai kai tayi tawuce takama Meena duk sukai sama, Hadiza tace "ba sama ba ko lahira kukaje sai anyi arresting naku yau wlh" officers din duk suka kalli Hadiza Nura yace "bismillah ku muje waje" binshi sukai waje Hadiza tabiyosu officer da kanshi yace "ki barmu maza muyi magana mana Madam" tsayawa tayi saikuma ta buga tsaki takoma daki, explaining komi Nura yamusu yama nuna musu some magungunan Hajiya dake motanshi yabasu hakuri kan kada suyi arresting kanwarshi, ganin kamalan shi da natsuwan shi duba kuma da babban mutum ne, a well known businessman anan Abuja kuma ba yaro ba sannan sunga yanda Hadizan keyi itama borkonon kanta ce yasa sukai Na'am dudda haka saida suka amshi 20k a hannunshi kafin su tafi, suna tafiya ya tsaya ya jingina da mota yadan sauke ijiyan zuciya baiso ya yanke decision cikin fushi yakai 5min awajen sannan yakoma ciki afalo yaga Hadiza jikin window tana ganinshi ta taho tana ihu tana tafi tace "u bribe them and send them away sabida kar ayi arresting sister ka da Maman ka ko? To rest assure wlh wlh I will so deal with them, wlh saisun barmin gida, babu wani mahaluki dazai shigo gidana and snatched my peace of mind for me to menene amfanin karatun danayi? Ina zaman zamana wata Maman miji ta dawo gidana da zama is that even fair? Ba manyan asibitoci ne a Kano? Why here why Abuja? Let's be fair fa Nuri, lokacin da Maman ka ke gidan mijinta mother inlaw dinta tazo ta tare mata agida? Then why me? Kuma ace ban isa nayi complain ba? Still sun shigo ur sister nada taurin zuciyan ta daken ni? Ni Hadiza? Wlh u have to choose one koka tattarasu kaje ka nema musu hotel ko ka maidasu kano, this house belongs to me and you Nuri aure yabani gidan nan, dan haka wlh sai sunbar

gidan nan” girgiza mata kai Nura yayi, cikin kakkausan murya yace “wlh saidai ke kibar gidan nan not my mom! ki tattara kayanki kibar gidan nan don’t sleep in my house Hadiza, Na Sake Ki SAKI DAYA!”.

The foundation of Marriage is built on trust, respect, biyayya and love which I think Hadiza broke all awajen Nura, now do you all support sakin daya mata? Or do you think he should’ve done something entirely different???

Now the major abu da matan aure fears dayasa basason yan uwan miji suzo is because Men always tends to take side din yan uwansu and neglect side na matan su tambaya na anan shine Nura shima yadauki side din yan uwanshi kenan?? Or kuna tunanin he should’ve done better???

As a woman can you stand kiga an zagi mahaifiyarki data haifeki? Do you support action din Meena or not? Dan two things are involve Hadiza matan yayan tane sannan Hadiza ta girmeta far far and surprisingly Nura bai cema kanwarshi Meena anything ba….hmmmm share your two cents on this😞

Now overall tambayata is kuna tunanin basics na mata akan basason yan uwan miji suzo gidansu uhmmm to some extend sunada gaskiya dan maza always takes side na family su gaskiya ne???
How should a family Man dazai sami kanshi a tsakiyan conflict tsakanin relatives nashi da matanshi address the matter??

See y’all Saturday 💃

💫 MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

BONUS💃
EPISODE 6
Dum dum dum!! Hadiza taji kalman sakin ya daki zuciyanta kaman saukan aradu cus ko

amafarki, like ko amafarki dai wannan bata taba tunanin Nura zai taba bude baki yace yasake ta ba, duk yanda takeson tai kokarin controlling yanda hannunta ke rawa kasawa tayi wani kalan reflex rawa hannayenta suka fara tama kasa magana sai idanunta data kwalaloo kaman zasu fadi akasa tana kallon Nura daya hade rai kaman wanda baitaba murmushi ba aduniya ya nuna mata kofa yace “get out of my house, out!” Yadaka mata tsawan da saida ta firgita, ganin taki motsi yasa yayi inda take azuciye yasa hannunshi yakama hannunta datake rike da key motanta yawani jata dan ranshi yabaci ainun ta daukoma Mamanshi da kanwarshi Police haba nooo enough! Dasauri Hadiza tashiga cewa. “Nuri, Nuri, Nuri” bude kofa yayi yafito da ita har zuwa wajen motan ta yace “get out of my house” dasauri tace “Nuri ni zaka cewa kasaka are u for real? Wait mafarki nake? Nine zaka saka because of your family now can u see why I was against zuwan family miji cause all they bring into your home is chaos? Nuri ni Hadiza zaka saka? Ni zaka kora from my home”? Wani kallo yamata yace “you are dumb, foolish and you are crazy Hadiza, bakin halinki yasa I don’t have any feelings left for you azuciyana, duk matan da have no regard towards my mother can never have space in my life or home dan haka get out, go and do your feminism awani waje not inda uwata take” yana maganan yawuce ciki ya maida kofa yarufe da key yabarshi ta yanda she can’t come in, Hadiza was completely in a state of shock ita Nuri zai saka, ita Hadiza, wajen kofan tayi tadaga hannu zata buga saikuma tace ai sai su Meena su mata dariya damai gadi, tama zubar da ajinta kenan rokonshi zatayi yabude mata kofa kome? Yasaketa  tayi tafiyanta mana, deep down zuciyanta cike yake fal da damuwa sai tambayan kanta take ita Nuri yasaka just now? Ita Hadizan nan saki fa? Saki dai datakeji anama wasu matan itama yau anmata so yanzu she’s a divorcee? Ta tambayi kanta saikuma ta juya tashiga motanta tazauna takai awa daya ahaka dataga dai da gaskene yasaketa ta tada mota ta tafi yanzu inama zataje ta tambayi kanta taje gidan kawarta ne? Ina zata? Parking tayi cikin premises na shagonta tai dialing number yayanta ringing daya ta daga kafin Anty Jamila tai magana Hadiza tace “Anty kinga yasakeni ko”? Shiru Anty Jamila tayi irin shirun son gane abinda tayi, saikuma tace “ai yamiki kyau gashinan jikinki yayi sanyi hankalinki yafara dawowa” cikeda karfin hali da tsiwa tace “jikin wa yayi sanyi? Da ace namai laifi ne sai jikina yayi sanyi? Ni Nuri zai saka sabida yan uwanshi wlh zai gane he’s mistaken idan yana tunanin yasakeni kuma na sakun mai wlh karya yake yacimini mutunci haka yakoreni wl…..” takasa karasa maganan sabida kukan daya taso mata tai shiru Anty Jamila tace “kinason mijinki Hadiza, kina mutuwan son mijinki amman bakin hali da al’adan yahudu da nasara yasa kin zama shaidaniya, shine your eye and accept keda shi are not one amman kin dage ke da shi are one kin dage, kin dage kaman bakar mayya accept cewa ba komi ne arayuwan nan must always go your way ba, idan haukan dakikeyi ko feminism din dakikeyi na solving matsala go and solve this one mana da feminism din look at abinda shegen feminism din yasa kika girba saki and this is just the beginning saikin rasa mijinki sannan zaki gane kene da kanki kika saka kanki a wahala, yanzu bama wannan ba Meya hadaku”?

Dudda akule take ahaka tabawa Anty Jamila labarin komi salati Anty Jamila tayi tace “wlh da niyyata muna gama maganan nan nakira Nura nabashi hakuri amman wlh, wlh bazan kiraba saidai Mama takirashi, Hadiza uwarsa kika zaga? Wai aljanu gareki ne koko kin fara having mental disorder ne? Konine bazan tsaya wata tazagi Mama agabana ba sai inda karfina yakare, Meena tamin daidai ke baki girmama nagaba dake ba tayaya nakasa dake zasu girmama ki?

Kadan kika gani Allah yab…….” Ihu Hadiza tayi tace “ni dama nasan u will never support me what’s wrong with abinda nakeyi? I am just going with the trend? A home belong to the woman so she should be the one to call the shot, Anty Jamila fisabilillahi da aurena agidana amman bazan fadi ajiba banda say, haka akeyi eh? Nasa yar aiki tamin girki yahanata, yasa yan uwanshi suzo bazai tambayi permission dina ba ita Hajiyan haka aka mata eh? Ta kawai shigo gidana tahanani sakat ana cewa batada lafiya kinga abincin danaga tana zakalkala aciki ne tana zuba surutu? Tanaji aka sakeni aka korani bata fito tasa baki ba that’s shows plan work ne, All I ever yearn for and I ever do was to be incharge of my home, kome zai faru inhar it has to do with gidana nizan fadi ayi ba Nura ba, duk fadan dazanyi dashi akan abinne, idan zaimin haka nima zanmai komi yanada abokai yasan haka akeyi a Abuja har kunya nake kar kawayena suzo suga abinda ke faruwa agidana su bahaka sukeyi agidan su ba” dan ijiyan zuciya Anty Jamila tayi tace “Hadiza baka forcing control da ownership, Nura zai iya bari kina calling shots agidanshi idan yaso amman means dakike bi is not right, tell me one thing dakike yima mijinki tell me?” Cikeda bakin takaici kaman ta make Anty Nafisa ganin taki fahimtan ta tace “Anty Nafisa pls pls understand nan ba kano bane this is FCT for crying out load, city of wealth, a Abuja u don’t have to do anything for mijinki as a wife, a woman is a queen dayakamata tanada ma’aikata which I have, su yakamata suyi komi, in this aspect banyi any laifi ba nagaya miki I’m just going with the trend zamanin damuke kenan, I don’t have to cook, sweep, take care of the kids or anything akwai masuyin aikin abiyasu duk wata Anty Nafisa nan ba kano bane kigane there’s nothing extraordinary anan abinda ke faruwa kenan wlh” hmmm! Anty Nafisa tasauke ijiyan zuciya dan lamarin Hadiza mai girma ne tace “Hadiza kinyi nisa are you saying yanzu kuka koma Italy al’adan Italians zaki dauka kicema mijinki dan Nigeria dole sai yayi? When will u understand mijinki bazamfare ne girman kano, Sana’a ce takawoshi Abuja, Nura is educated but rayuwan bokon nan da wayewa tamasu kudi dakikeso shi baya gabanshi, ace yana aurenki bazaki bashi ruwa dakanki yasha ba menenen ma amfanin ki? Wai kuma ahaka bakimai komi kuma kinaso shi yamiki komi, kome kikace yace Naam ko tunda gaki mamallakiyan Nura sannu Hadiza mai fadi aji, yanzu kina ina?” “Shago na” cikeda isgilanci Anty Jamila tace “maisa bakije gidan kawayen naki ba to”? Ahankali tace “ai abin kunya ne suji abinda yasameni, that means I don’t even have any power or influence agidana inhar mijina zai koreni daga gidana sabida yan uwanshi wlh wlh abin nan yamini ciwo Anty Jamila, you have no idea yanda matan Abuja are powerful agidan su amman ni Nura bazai bari nai enjoying that luxury ba, kuma wlh wlh wlh zai sani” anatse Anty Jamila tace “Hadiza keba yarinya bace you’re 32, ke kinsan abinda kike bai dace ba, uwarmiji uwarkice, ita tahaifo abinda kikeso and nurture him, groom him into the man he’s today, miji ba abin wasa bane dazaki dinga experiment naki akanshi, this is just 1saki Nura yabaki, idan ba u wanna loose him for ever ba ki gyara, all it takes is apology, kije kibama mahaifiyar shi hakuri kibashi hakuri ki gyara the way kike abubuwa agidan ki before it will be too late for u kina jina? Idan zaki dawo kano ne kidawo, zandai gayama Mama nasan zata kirashi amman ni Allah yasan bazan iya kiranshi ba take care Allah kuma ya ganar dake kafin lokaci yakure miki”.

Katse wayan tayi tadade zaune amota saida aka tafi magrib sannan tafito ta tafi sama tabude shagon tashiga tamaida tarufe tawuce sama office nata ta shiga kwanciya tayi kan dogon kujeranta tayi shiru tanada kudin kama hotel ta kwana abinta amman takasa, takasa zuwa wajen kawayenta kada amata dariya tagama cika baki, da kyar ta lallaba taje tai salla wasa

wasa har 12 nadare takasa bacci sai juye juye take yanzu shikenan Nura yasaketa ya koreta daga gidanta shikenan bata da gata? Itane yau da kwana a shago? Hakanan kawai saitaji tana kewan yaranta koba komi kobadan suzo wajenta ba amman muryansu da hayaniyansu datakeji da Ummi is something sai kawai taji tayi kewansu sosai din nan, lema lema dataji akan fuskanta yasa takai hannunta dasauri ta taba ashe kuka takeyi dasauri ta tashi zaune tace “no feminist don’t cry, with or without Nura I can create my world why am I sad? Dan yace yasakeni, yakoreni daga gidanshi? Why nakejin badadi nakasa bacci 9 nayi bacci jibi lokaci yanzu nakasa why?, Yanzu Nura harya isa yacusamin bakin ciki? Then menene amfanin the belief I stand for? The whole feminism an fito dashi ne dan anunama mata they don’t need men or approval na men to survive on this world, all she need is herself” share fuskanta tayi tass tace “Nura kayi kadan kasamin kunci” ijiyan zuciya tasauke tafara fadama kanta words of affirmation. “I’m Hadiza diyar Tijjani, I’m strong, independent and beautiful dudda tsinanniyar yarinyar nan tamin scars din yakushi yanzu awuyana, I’m smart, unapologetic, resilient and bold, I don’t need a man ko anybody to be happy, Hadiza is enough for kanta, a man can’t downgrade or belittle Hadiza, I’m as tall as the mountain ,as hard as rock, as thick as thicker, no one can break Hadiza saidai ni nai breaking, I’m unbreakable, I’m happy, I’m happy, yesss I am happy!!” Tafadi ma kanta tana murmushi tana dukan kirjinta saikuma wasu munafukan hawaye suka kara fitowa daga gefen idanunta tadaura hannunta akan fuskanta tafashe da kuka sosai tace “na shiga uku why am I sad? Nura ni zaka saka awanan sad mode din? Ni Hadiza zakama saki Nura? Ni kanwarka zatama duka sannan kayi throwing dina out kahadan da saki jibeni a shago zan kwana? Ni Nura?? Wlh saina gwada maka kayi da diyar halas wlh kuwa” wani shegen kunci takeji the state datake ciki ita kanta batasan Nura is this important to her ba sosai take sonshi but bata saniba, she’s extremely sad takasa bacci, kaman ta hadiye zuciya takeji tamutu.

Wajajen 3:30AM Hajiya ta tashi daga bacci, Meena tagani agefenta dasu Amal duk suna bacci komi daya faru dazu dawo mata yayi sauka tayi daga gadon da dafa bango tafito dakin Nura taje sallama tayi ahankali ga mamakinta bude kofan yayi yana sanye da jallabiya hannunshi rikeda charbi dasauri yariketa yace “Hajiya kin tashi” shigar da ita dakin yayi yamaida kofa yarufe akan couch na dakin ya zaunar da ita shikuma yazauna agabanta akasa yakama hannunta yarike ahankali yace “Hajiya kiyakuri sabida ni Hadiza tamiki rashin kunya yau” girgixamai kai tayi kafin tazare hannunta daga nashi daya rike ta tallabo fuskanshi cikeda tsantsan soyayya irin na d’a da mahaifi tace “maisa baka taba sanar dani abinda ke faruwa agidanka ba? Nura yaushe Hadiza takoma haka? Kamata wani abu ne”? Duk yanda yaso ya daure kasawa yayi ahankali yadaura fuskanshi sanan cinyan Hajiya murya chan kasa yace “Hajiya nagaji I’m tired, sometimes I feel maisa namayi aure? Da auren nan gwara rashin sa but then nakalli yarana Aman and Amal sainace Alhamdulillah Allah has already blessed me with the most beautiful kids aduniyan nan” yayi shiru yace “Hajiya I don’t have peace of mind idan nabar gidan nan kaman kada nadawo tunanin yarana kesa nadawo, babu one single thing da Hadiza kemin amatsayinta na matana and bantaba mata wani abuba, Hajiya sometime ina zama na gayama kaina indai this is wat comes out of auren educated mace to gwara auren gidahuma jahila dazata maka biyayya and be a wife for you cus Hadiza is a wife for herself not for me, tanada masters in business Administration tanada business kudin sun shiga hannunta,

yanzu taga am useless koda ace yau zan rabu da ita tanada future she has money, and money is everything idan kanada kudi baka bukatar komi kuma zata iya kula da kanta, everything data mini I tolerated it dudda she's 32 but kallon mahaukacin yarinya nake mata Hajiya she insulted you today tayi magana dake kaman ita ta haifeki saisa nace tabarmini gida taje na sake ta saki daya" dasauri Hajiya ta kalleshi dago kanshi yayi idanunshi sunyi jaaa sosai yace "Hajiya kin sanni sama da kowa kinsan inada hakuri kawaici juriya dakuma yafiya yaune rana na farko dazan rokeki Al farma kada kice nadawo da ita please I want a break from this auren mu besides I've grown feelings for someone kuma inaso naje garinsu na nemi aurenta" Hajiya na kallon fuskanshi tace "Ummi?" Dasauri yace "tayaya kika sani Hajiya"? Dan murmushi tayi tace "sabida nina haifeka" dan shiru yayi chan yace "Hajiya nakamu da son Ummi sosai, tagayamin ta taba aure tama haihu……" yabama Hajiya labarin yace "Hajiya inason Ummi sabida some odd dalilai" ahankali yace "Hajiya nakamu da son Ummi sabida duk wani abu da Hadiza kedashi ita batada shi" yadan sauke ijiyan zuciya yace "inason ta sabida she's not educated, sabida batada kudi, sabida she's not independent, sabida she's innocent, sabida she's polite, sabida she respects me, sabida she pay attention to me, sabida tanason yara na, sabida she feed me, sabida tana magana dani calmly her voice is so soothing to my heart, I love her sabida she's weak, fragile, sabida she's a soft woman not strong woman, ina sonta sabida matace da idan na aureta nine zan zama ragamar rayuwanta and she will let me be the husband and above all nayi istikhara akanta naji azuciyana na natsu da ita, Hajiya inason na aureta amman saikin bani go ahead" murmushi Hajiya tayi tana kallonshi hannunta takai ta share dan guntun hawayen daya fito daga gefen idanunshi tace "na amince kaje kauyensu ka nemi aurenta amman da sharadin kadawo da Hadiza" dasauri yakalli Hajiya, murmushi tamai tace "Nura no marraige is perfect, kowani aure da crisis din dake ciki har Ummin idan ka aureta you guys will have ur differences and issues but what makes Marraige works and last is the ability to work on your issues understand each other better, forgiveness and moving on without holding grudge, kaga all this fadan yanasa akara fahimtan juna, kuskuren Hadiza shine tunanin datake itada mijinta daidai kuke wanda bahaka bane u are the leader and she's your subordinate dole ta bika, but I'm sure yanzu she learnt her lesson sabida duk ranan da mace zata kwana awani waje ta dalilin saki ranan bata iya bacci mai kyau ko itace da laifi ko ba itace da laifi ba, saki babban abune, saki is powerful, duk randa aka yishi alarshin Allah na girgiza, duk randa akai saki shaidan na party's jin dadi, duk inda Hadiza take yanzu tana cikin damuwa sosai, kayakuri kadawo da ita kodan yaranku, kada ka manta Annabi yace akama mace saki daya yakamata tana zaune agidanta ne kacigaba da bata ci da sha har zuwa ka maidata dan haka bring her back karka sabama koyarwan addinin mu" dan ijiyan zuciya yasauke yace "dazu Mamanta takirani tabani hakuri I just told her naji" dasauri tace "yauwa ka kyauta, yaushe zakaje neman auren Ummin? Ka sanar da ita kana sonta?" Girgizama Hajiya kai yayi yace "saina kaita kauyensu zan fada mata inaso sai mun koma
Munga Dr gobe naji mai zaice game da ke, kafin nasan ranan dazan kaita" shiru Hajiya tayi ita bataso tacigaba da zama agidan nan ahankali tace "koma me ake ciki gobe daga asibiti ka kaini gidan kanin marigayi mahaifinku daganan suma ai zasu dinga iya kaini asibitin ballama nasan magani zaa bani ace nadawo bayan one week, koma menene inason jibi ka maida Ummi gida ka sanar da yan uwanta banson yanda soyayyanta ya kullu aranka tana zama karkashinka shaidan is real kana jina kaje garinsu jibi ayi magana muji me ake ciki idan da hali zasu baka sai

adaura auren achan ma sai kaje tareda kanin Babanka da wasu abokan naka, da Meena kuma Ubangiji Allah yasa albarka ni kaina na yaba da natsuwan yarinyar kuma ta kwanta mini arai.

Ba karamin fada mahaifiyar Hadiza tamataba kuma tace tabama Hajiya hakuri da Nura, washe gari ba dudda idanunta a kone suke amman kana ganinta tai zuru zuru sanda Mamanta tagaya mata Nura yace takoma har ijiyan zuciya tasauke aboye baro shagon tayi wajajen 8.
Around 9 takai gidansu tana parking motanta Nura na fitowa daga gidan rike da Hajiya da Meena suna hira suna dariya yayi wani irin kyau yana sanye da soft material milk yasa sunglasses a idanunshi, hada ido tayi dasu dasauri ta dauke kai haderai tayi tamau ta taho saida tazo dab dasu tace “sannu ya jiki” bata jira amsan Hajiya ba tawuce ciki tabude kofa ta shiga ta bugo kofan Nura yajuya yakalli kofan Hajiya tace “muje kaga 10 fa likita zai ganmu” wucewa sukayi suka tafi.

Tunda Ummi taga Hadiza tadawo ta shiga ta natsu tana gama aikinta ta tafi bayan gida a garden ta zauna akan kujeran lilon su Amal da wayanta a hannu tana buga game, ringing wayanta yayi dasauri ta kalla batasan number ba amman tadauka takai kunnenta ahankali tace “hello” anatse Nura yace “Hajiya Ummi” batasan lokacin datace “laaaaa Alhaji yakuri bansan kai bane, ina yini, Ya Hajiya kunkai asibitin? Wani abu kake bukata nayi?” Duk ta jero mishi tambayan atare, cikin kwantacciyan murya yace “Hajiya natare da Dr, tagama ganinshi kuma zan kaita chan Gwarimpa anan zata cigaba da zama gidan kannin Abba na” “okay” Ummi tafadi but zaka iyajin nuna jin dadin ta a muryanta, ahankali yace “kinada katinki na kasa? National identity card?” Dasauri tace “eh inada shi” shiru yasakeyi yace “kituramin hoton shi ta whatsapp sannan ki shirya kayanki gobe zan maidaki kauyenku Adamawa ko?” Maganan yazomata abazata dasauri tace “eh” saikuma chan asanyaye tace “wani laifi nayi”? Ahankali yace “kin manta alkawarin dana miki zan kaiki kiga Gwaggon ki shine zan cika” murmushi tayi taushi tace “Allah yasaka maka da alkhairi” murmusawa yayi shima yace “kinga kayanki cikin kayan danasa gateman yakawo miki?” Dasauri tace “naga slippers dina na dauka, naga wasu kaya duk sainakai store na ijiye” cikeda so yace “nakine akwai wani black abaya mai stones ahannunshi shinakeso kisaka gobe kinji” gyadamai kai tayi kaman yana gabanta tace “to nagode Alhaji” shiru yayi bai sake cewa komiba tagaji da shirun tace “hello” kaman daga sama yace “zaki aureni Ummi?.

Matan Abuja!
Matan Abuja!!
Matan Abuja!!!
Haaaaa, HADIZA has been making countless reference daku, the women of Abuja come close are you all the way Hadiza ke suffanta ku? Ance idan miya yayi yaji??? Ai dole yaji ne zai saka miyan yaji ko??
So kunada dogon explanation you guys need to come clean🤣

But then again all I see in Hadiza is so much soyayya for her man but this stupid mentality nata

is leading her astray, why must you be the one to call shots agidan mijinki? To shi mijin is there for what? Name ko fame????

Hello Ladies both married and unmarried are you learning one or two lessons from this novel nawa???

But again kuma let's not be sentimental, mu kalli Hadiza da kyau, all she ever wanted is power which is normal akwai dominating mata dama, itama tanason kawayenta susan tana juya mijinta but maganan yayanta is valid sabida kunje Italy saikice saikin maida mijinki Italian???
Share your 2cents ladies and gentlemen ❤️
See you asabar💃
💫MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE7️⃣
THIS PAGE IS FOR YOU ZEE, MY NUMBER 1 MOTIVATOR, I LOVE YOU❤️❤️
Saukan tambayanshi Ummi taji kaman daga sama saikuma takai hannunta ta taba kirjinta daya buga, to kodai sabida yanda taketa tunaninshi tun jiya yasa taji kaman yace mata zata aureshi? Ta tambayi kanta, me Alhaji zaiyi da itama in banda shirmen tunainta hakan yasa tace "na'am banji abinda kace ba Alhaji?" Ijiyan zuciya Nura ya sauke wlh yadade baiji murya mai dadi kaman na yarinyar nan ba komi nata sanyaya mai zuciya yake, the feelings he's developing for her is growing a fastest rate, cikin taushashiyar murya dake kashewa mace zuciya yace "ina sonki da aure Ummi zaki aure ni?" Yanda gaban Ummi ke bugawa saida tacire wayan dasauri daga kunninta takifa shi kan cinyanta tadaura duka hannayen ta biyu kan wayan ta runtse idanunta tana breathing so fast this is unbelievable, yasan tana sonshi ne? Yasan tana tunaninshi ne? Ta tambayi kanta takai almost minti daya sannan tamaida wayan kunneta daidai Nura nacewa bakice komiba, itama wlh bala'in nauyi da kunya takeji tace ta yarda haba saikace jira take, kaman yana magana da little Amal yace "Ummimy" yanda yakira sunanta har cikin jinin jikinta taji itama anarke tace "Na'am" cikeda so da bege Nura yace "ataimaka abawa Alhaji amsa eh Hajiya Ummi na" rufe fuskanta tayi dasauri akuma kunyace, murmushi yadan subuce daga bakinta da yaji karan kadan hakan yasa yayi murmushi yace "Ina jinki" Abala'in kunyace tarufe fuskanta da hannu daya tarike waya da dayan hannun akunnenta tace "idan munje kauyen mu ka tambayi Gwaggo na" murmushi yamata shi babba ne this amsan kadai ya wadatar da curiosity dinshi yace "okay yanzu kije kiyi sallama da matan gidan kice mata zakije kauyenku gobe an kiraki daga gida, kada ki fada mata wani abu bayan haka kinji" gyadamai kai tayi tace "toh" dan ijiyan zuciya yasauke kaman kada yayi sallama da ita yace "tom saina dawo" akunyace still tace "mezan dafa maka"? Cikin kashe murya yace "nabarwa Hajiya Ummi zabi"

dasauri ta cire wayan daga kunnenta takashe sai murmushi take, amsanshi melt zuciyanta, wai itadai Alhaji keso ya aura ikon Allah, takai awa daya awajen zancen zuci take ita kadai sannan ta tashi tawuce sama sallama da knocking tayi gaban dakin Hadiza akace shigo bude kofa tayi ta shiga Hadiza na kwance kan gado da babban IPad dinta na apple tana kallon cctv footage na shagonta yanda yau takasa zuwa shagon dan batada karfin zuwa dukawa Ummi tayi tace “sannu da hutawa Anty” kallo daya Hadiza tamata tadauke kai tace “lafiya?” Kan Ummi na kasa tace “Anty tafiya takamani kauyen mu gobe!” Dasauri Hadiza ta yunkuro ta kalleta hakan yasa Ummi tace “Gwaggo na batada lpy tace tanason ta gani maza maza” wani kalan harara Hadiza tamata tama kasa magana to idan ta tafi yaya zatayi da yaran nan gashi kafin su sami wata yar aiki dazasu saba da ita sai an wahala, cikeda asalin rashin son ta tafi tace “inhar kinsa kafa kinbar gidan nan da sunan tafiya to kisani na sallameki daga aikin nan kinajina”? Gyadamata kai Ummi tayi ahankali tace “toh” tsaki Hadiza taja danta dauka she will start begging her tace tafasa tafiyar, rai abace tace “sabida dan rashin lafiya ne yanzu harsai anwani kiraki kinbar aikin ki dake ciyar dasu kinje kauye? yanzu ma tukunna kwana nawa zakiyi idan kinje? Kan Ummi na kasa tace “sati daya ko biyu hala” Hadiza jitayi ranta yabaci datana da wani power da wlh saita hana tafiyan nan cus yaranta zasu shiga wani hali yazatayi dasu yanzu? Ga agency nan kokai requesting yan aiki unless akwai akasa shine zaka samu fast Inba hakaba sai an kawo, tsakin takaici takaraja tace “tashi kifita ki tabbatar dai goben kin shirya yaran nan sun tafi school kafin kibar gidan nan dan da sassafe zanje aiki yanda yau banje ba din nan” “to zanyi Anty, nagode” Ummi tafadi tana mikewa tafice daga dakin tawuce kasa yan karikechan ta tashiga hadawa bayan tagama taje tayi girki, yaran suka dawo ta shirya su bayan sunci abinci takaisu islamiyya dake nan cikin estate nasu itama takasa gayamusu zatai tafiya dan tasan kuka zasuyi sosai amman wlh zatayi kewansu sosai.

Wuraren 10 yashigo gidan zama yayi a dinning yaci abinci bura busko Ummi tamai da wani miyan veggies mai dadi abincin dayaci saida yabashi tsoro tass yagama yakalli dakinta yayi murmushi yawuce sama ga mamakinshi Hadiza yagani a falon sama kwance kan dogon kujera daga ita sai wani dan black short mai kaman pant yanada lace abakin wandon very sexy, tasaka half vest milk na silk material mai kyau shima, dan juyowa tayi suka hada ido itada Nuran sannan ta maida kanta kan throw pillow ta kwanta tana kallon tv, ita kanta bama tasan maisa tayi gayun nan tazo nan ta kwanta ba, deep down so kawai take ya kulata, dakin Aman Nura yashiga yadubashi yamai addu’a yafito ko kallon inda take baiyiba yashiga dakin Amal yamata addu’a yafito ta gefen ido Hadiza keta binshi da kallon ganin su Hajiya basu dawo tareda shi ba to ya komar dasu Kano ne? Ko yamaka musu hotel ne?.
Dakinshi yashiga bayi yafada direct yayi wanka fitowa yayi daure da towel a waist ga mamakinshi Hadiza yagani kan gadonshi ta kwanta tana kallonshi exactly irin kallon shima yamata yadauke kai yawuce gaban madubi ya shafa mai ya feffesa lafiyayyun turarenshi yaje gaban wardrobe yaciro pajamas nashi yakoma bayi yasaka yafito, ganin ya dumfaro gadon yasa Hadiza tasoma jin dadi aranta agaban gadon ya tsaya yasake kallonta ido cikin ido itama kallonshi take right in the eye amman bazata iya bude baki ta gaidashi kota cemai sannu ba taga shigowanshi gida tun dazu, dauke idanunshi yayi daga kanta, filon dake gefenta yasa hannu yadauka yayi wajen kofa yabude yafita yawuce dakin Aman kan gadon Aman yahau

yana kashe wuta ya kwanta abinshi yana sauke ijiyan zuciya.

Bugo kofan Hadiza tayi tashigo ta kunna wuta dakin yayi haske takalli Nura tace “kanka akeji daman sabida Mama tamin fada ne nazo turakan ka amman jibi yanda ka wulakanta ni, ka shanyani agado kataho dakin danka zaka kwana anjima kahau cewa ban maka komi na aure, oya kajika gabanka aruwa kasha mana kasan ai ka iya biyo sahu idan jarabanka yataso maka ka lallabani nabaka, ina jiran ranan zakasha mamaki na nima wlh” tajuya fuuu tafice daga dakin ta bugomusu kofa saida Aman ya firgita cikin bacci dasauri yarike Aman yana patting head nashi, chan bayan yakoma bacci yatashi yakashe wuta yadawo ya kwanta yayi bacci abinshi.
**

Washegari normal aikinta Ummi tayi Hadiza tasauko tai breakfast around 8 tawuce tafita abinta ko biyar bata bawa Ummi ba dan ba son tafiyan takeba, saukowa Nura yayi yana sanye da wata farar shadda yayi kyau bana wasa ba har gaban dakin Ummi yaje yayi knocking bude kofa tayi chak numfashin shi ya tsaya ganin Ummi tana sanye da sabon black dogon rigan daya saya mata, ta tsife kanta jiya da daddare ta wanke da sabulun wankanta abinta ta taje tayi Parking batada cikan gashi at all dan kanta ma small head gareta amman wani kalan coily blonde-black hair gareta dan gashinta ba baki sidik bane irin jajajan nan ne orange orange baki baki, fari fari irin gashin agwai haka gashinta yake ta yana gyale akai daya dan ja baya tasa kwalli a idanunta, rigan yamata chass ajiki ganinshi dan tun jiya sai yanzu suka hadu yasa ta juya dasauri zata koma cikin daki karaf yakamo hannunta dasauri tajuyo suka hada ido ta zubamai fararen idanunta dasuka sha kwalli ta diga kwalli in between giranta guda biyu tayi wani kalan unexplainable kyau, ahankali yasaki hannunta dayaji yamai taushin gaske kaman yarike hannun Amal sai kawai yajuya dasauri yayi dinning dan rabon dayaji wani abu yatadamai da sha’awa harya manta, ganin Ummi da dan kama hannunta dayayi just awaken libido nashi zama yayi a dinning yayi crossing leg da sauri batare daya juyoba yace “kin gama hada komi ina gama breakfast zamu wuce” daga chan ta dakinta tace “eh nagama” itama komawa daki tayi dasauri yanda taji hannun Alhaji cikin nata sai taji tana fitar da numfashi kashi kashi.

Tass yayi lafiyayyan breakfast sannan yazo wajen kofan yace “kawo kayanki mutafi” bude kofa tayi rike da ghanamasgo dinta akunyace kallon Ghanamasgon yayi sai kawai yajuya yace “ina zuwa” sama yakoma yadauko babban suitcase nashi yakawo har gaban dakinta ya duka yabude ya karbi Ghanamasgon baiji kunya ko kyama ba da kanshi yabude yashiga jera mata komi a suitcase din, yarinyar nada tsafta dudda kayanta sun mutu but komi awanke alinke ga dan black leather dayakai hannunshi zai taba dasauri Ummi ta duka tarigashi dauka hakan yasa ya kalleta sai kawai yayi murmushi dan yasan menene turawa tayi akasan akwatin nan da nan yagama hadawa suka kulle yaja akwatin waje Ummi na biye dashi har mota gaba yau yabude mata yana kallonta shiga tayi ahankali ta zauna yakallulle yadawo gaba shima yatada mota har Gwarimpa bakaramin addu’a Hajiya tamusu ba sannan Meena da Baffan shi da ita suka tafi airport ga mamamkin Ummi abokanshi tagani a airport already suna jiransu da Musa da engineer sunci manyan kaya sai kallo Ummi suke munafukai saijin dadi suke, jirgi suke shiga kalan tsoron da Ummi taji a ko tadauka mutuwa zatayi haka sukakai Yola motoci taga suna

jiransu guda daya daya security personnel sauran nasu nan aka dauki hanyar kauyensu though sun tsaya a hanya anyi sayyaya na ban mamaki kayan abinci shopping da sauransu.
Tunda Ummi taga sun dauki hanyar kauyensu gabanta ke faduwa hannunta suka fara rawa komi nadawo mata sabi fill
Hannunta Meena tarike tace “ga dukanmu, ga mopol yan sandan chan babu abinda wani katon dan daban kauye ya isa yamiki” tafiyan awa daya da rabi yakaisu kauyensu, kauye ne da yamayi developing ga government work akwai government school, burtsatsai, primary health care da sauransu sai kallon ko’ina take komi ya chanza ta dade rabonta da garin har gidansu wanda yake babban gida ginin kasa irin na da din nan.
Wata tsohuwa sosai haka na zaune a tsakar gida tana mulmula hura taji ihuuu hayaniya a waje tace “Allah yasa ba shaidanin yaron nan ne yazo dawani bala’in ba yau” da gudu wata yarinyar mai kama da Ummi yar karama da bazata wuce 13yrs ba tashigo tana hakki. “Gwaggo Gwaggooo Ummi, Umm…..” kafi takarasa magana Ummi tashigo gidan tareda Meena, mikewa tsaye Gwaggo tayi saikuma tasa zani ta murje idanunta tasake kallon Ummi data tsaya tana kallon Gwaggo, Gwaggo tace “Kodai mutuwa ce tazomini yasa nike ganin kaman Ummi achan tsaye dawata balarabiya” dawani kalan gudu Ummi tazo tafada jikin Gwaggo sai kuka ga kanwar Ummi ta biyun itama tashigo sai kawai dukansu sukahau kuka dagota Gwaggo tayi tace “Ummi kene binni ya karba haka kin ganki kuwa ya akayi kikazo? Banace kada kizo ba duk sati sai Mudi yazo gid…..” fuska Ummi ta share tace “Gwaggo akwai baki maza awaje dauko tabarma Aisha ki shimfida wajenki zukazo” dasauri Gwaggo tace “bakin yan uwan baturiya nan ne, yaki yarinya gaki fara kaman madara” murmushi Meeena tayi tazo ta gaida Gwaggo, Gwaggo ta aika Aisha ashigo dasu nan da nan aka shigo dasu wai bakin Gwaggo yaki rufuwa taga manyan dattijawa ansha shadda fura tashiga hada musu kowanne a kwarya mai kyau su Aisha harda Ummi dama Meena natayasu har Baffa saida yasha huran sun dade basu sami aslin ingantaccen fura irin wannan ba sukai salla.
Daukan nasu huran sukayi su Ummi duk suka tafi daki saida aka gama Baffa ya gabatar da zancen daya kawosu wai Gwaggo kasa boye farin cikinta tayi nan ta sanar dasu komi game da Ummi da aurenta ada tace zancen aurenta kuma maigari ne mai bada yaran aure Dan haka atafi wajenshi nan akanshigo da komi aka shiga mota aka tafi wajen mai gari shima yayi naaam babu wani wahala Dan Auren bazawara ba wahala and tanada right Ummi tafito da mijinta yanzu tunda nabiyu ne kuma itane takawoshi har kauyensubnan da nan su Musa suka ijiyema abokinsu sadaki dubu dari uku aka daura aure tsakanin Nura da Zainabu Ummi akan sadaki 300k mutane dayawa sun shaida aka kawo su goro cingam menene menene aka rarraba wai Nura sai murmushi yake he just can’t believe it duk suna wajen Aisha tazo da gudu tace “Gwaggo ga Mudi chan yazo amman yan sandan nan sunmai duka” tashi Nura yayi da sauransu Maugari yace “dan Allah kukai yaron nan gidan yaro ya addabi mutanen Hm kauyen nan” komawa sukayi akai arresting Mudi nan fa Gwaggo tayi throwing small party itadai Ummi taja makale adaki taki fitowa Meena ko tafito sai video take yanda matan kauye ke rawa Musa yakawo bakinshi saitin kunnen Nura yace “kai mutumina bura’uban chan haka kauye keda tsala tsalan mata bazanyi wuff dawata ba kuwa anan kai jibidai kirjin wanchan dake rawa” tureshi Nura yayi yace “dan iska” dariya Musa yayi yana kallon yammatan, Musa yataba engineer yace “kaga yara amman Allah yamusu kindirmo a kirji” Nura yayi kaman baijishi ba aranshi yace “na Matata Ummi tamafi kowa nan kindirmo” yadan lashe lips yana kallon agogo, Aisha ne tazo tace

“Gwaggo tace kazo” binta yayi zuwa falon Gwaggo tana zaune ga Ummi agefe kanta akasa zama yayi ahankali Gwaggo tace “Nura na yaba da hankalinka ne saisa nabaka Auren jikata dan mutumin kwarai ne zaisa diyarka a mota da yan uwanshi azo har kauyenku a nemi aurenta dan haka nabaka ita amana kagansu nan su hudu ne dukansu marayun Allah ne ba uwa ba uba kaji tsoron Allah bamu da kowa a binni dazance je gidan Ummi dobamin ita, tana hannunka ka kulamin da ita na yarda da tarbiyan dana bama yaran nan sunada kunya natsuwa amana da girmama na gaba dasu Ummi bazata taba cutarda kai ba Ummi matace karike ta amana sai kuma inaso nadan roki alfarma ka barta tadanyi ko sati guda ne anan wajena a danyi mata gyaran amare” abu Nura yaji ya tsayamai awuya Gwaggo tace “kayarda”? Ahankali yace “ba matsala” Gwaggo tace “yauwa tunda an kama shegen yaron nan banda sauran tashin hankali na gode Nura bari nafita nabaku guri kuyi sallama” Gwaggo ta tashi tafice.

Juyoda kanshi yayi yakalli Ummi da kanta ke kasa tana jikin bango kaman ruwa ya hadiyeta mikewa tsaye yayi yana duba agogon dake daure da writs nashi sannan yakalleta yace “tashi ki rakani Amarya zan tafi” akunyace Ummi tadaura duka hannayenta kan fuskanta tarasa inda zatasaka kanta sabida kunya, he loves yanda takemai yarinta yarintar nan kunya kunyan nan, gently ya duka agabanta dab da ita yana kallon dogayen yatsunta masu fararen kumba dake kan fuskanta daya rufe yayi shiru, kamshin da Ummi taji na shiga hancinta yasa tadan ware two of her right fingers kaman munafuka tadan bude idanunta dan so take taga ina yake dan yanda takejin kamshin turaren nan nashi karaf suka hada ido ya leko fuskanta ta spice na yatsun ahaukace ta yunkura zata tashi karaf yariketa hannunshi daya yakai ta waist nata yarikota dasauri taboye kanta akirjinshi sosai takejin kunyanshi, yanda yaji fuskanta akirjinshi yasa ahankali yasaki hannunta yakai dayan hannunshi daman bayanta yaturata tashiga kirjinshi gabaki daya sannan yacire hannunshi daga waist nata yasa dukansu abayanta ya rungumeta da kyau tareda sauke ijiyan zuciya ataushashe yace “Assalamu Alaykum Matata Zainab” wani irin sanyin kunya Ummi taji tanaji takasa yarda jikin Alhaji take arungume haka, wlh kirjinshi bala’in taushi ga fadi kaman wani katifa, tun tanajin kunya taki sakin jiki hartai lamo tadaina motsi tanaji yanda kirjinshi ke beating ahankali, wayanshi ne yahau ringing batare daya saketa ba yazare hannunshi daya yaciro wayan yakai kunne Ummi bataji akace ba, amman da muryanshi dataji harya chanza launi yace “bari nagama sallama da iyalina nafito” yana maganan yacire wayan daga kunnenshi yamaida aljihu kafin ahankali yakai hannunshi daya yadago kanta daga kirjinshi maida kanta tayi da sauri, murmushi yayi cikin whispering yace “ina sonki Ummi, amman banji amsan soyayyata aranki ba aka daura mana aure kina sona”? Noke kanta tayi akafadanshi kaman yanama yarinya magana yace “kunyana kikeji?” Gyadamai kai tayi, ahankali yace “nazama mijinki yanzu babu ragowan kunya, yaushe zaki bani amsa?” Kanta yasake dagowa for the second time wannan karan batai musu ba ahankali ya manna mata peck agoshi batare daya cire bakinshi akan goshinta ba yace “zanbar miki Meena da some mopol anan ranan itiyau zan dawo na dauke, banda yawo, idan kinason wani abu ki kirani ki sanar dani kinji”? Gyadamai kai tayi ahankali yasa hannunshi a aljihu yakamo soft hannunta yasa bandir na 500 aciki yace “ki ijiye kudin nan tare dake kome kikeso kiyi dashi kinji”? Gyadamai kai tayi, har lokacin bakinshi nakan goshinta lips dinta ya kalla tanada a bit chubby soft bottom lips sai na saman is slightly thin a bit pinkish a bit dark he seriously wanna kiss her like right now but then yanason tazama comfortable dashi dan ijiyan zuciya yasauke kadan kafin ahankali

yasaketa yace “zan tafi” dan komawa baya kadan tayi kaman kada tafita daga jikinshi tana sussunnar dakai tace “Allah maidaku gida lpy nagode da abubuwan daka kawoma su Gwaggo Allah kara budi mai albarka” Ameen yafadi yayi wajen kofa dan juyowa yayi yakalleta kaman yadauketa yakeji yadai daure yadaga labule yafita daga dakin.

Bin dakin Ummi tayi da kallo ganin littafai da byro akan wani dan table yasa taje wajen ta bude tsakiyan book yafalllontahsiga rubutu, dasauri take rubutun cikin 2min tagama tadaga takara karantawa sannan tashiga linke paper wani kalan linki tama paper kaman flower wow yarinyar is creative fitowa tayi daga dakin da sauri Aishan su tagani tabata tace “imaza kaima mijina Shatu maza kafin su tafi” da gudu Aisha ta fanfala sai alokacin Ummi tadaura hannunta kan bakinta jin tace mijinta, Aiaha nafita suna tafiya haba tabi motan da gudu tana ihu yaran anguwa suka bita suna tayata ihu ana. “Mota ku tsaya ku tsaya” abunku da yaran kauye, Musa yafara hangosu dasauri yace “Nura wanchan ba kanwar Ummi bace ke biyomu da gudu da tawaganta” lekawa Nura yayi ganin yanda yara ke gudu ana ku tsaya yacema driver ya tsaya parking sukayi da gudu su Aisha sukazo wajen Musa dasauri yabude kofa dan daga Nura sai shi sai engineer Baffa na dayan motan, ana bude kofan Aisha da karfin muryanta tana haki tace “Yaya Ummi tace nabawa mijinta wasikar nan” tamikama Musa wasikar juyawa Musa yayi yakalli engineer dake murmushi sannan Nura daya hade rai Musa yamika hannu yace “to sannu da aiki Shatu kawo” hannu yasa zai amsa saiga hannun Nura ya fizge ya sa a aljihun gaban riga yabama yaran wasu kudi daya ciro daga aljihu yace “nagode” yaran suka kwasa aguje Musa yarufe kofa yace “jamuje direba” yakalli Nura yace “wowww Ango wlh soyayyan kauye tayi ne jibi wani wasika da aka aiko maka an mata wata kinmin fulawa kaga engineer billahillazi a kauyen nan zanzo nima na nemi amarya inaaa kai kaga yaransu ne sunsha kindirmo tun suna jarirai yanzu duk yakoma kirjinsu” dariya duk sukayi Engineer yace “kaidai kwarto ne Musa shegen gari, kai ranan kasa na kusan kashe madam wannan maganin basir ai bala’i ne” dariya Musa yayi suka cigaba da hira ganin haka yasa Nura yaciro wasikar yana yaban design da magic na maida sheet of paper into flower shape da Ummi tayi ya warware ahankali.

“Assalamu Alaykum Baban Amalily, wanda yazama mijina ayau rana uku ga watan maris. Amsan tambayan kace awannan sakon”
Gyara zama Nura yayi yacigaba da karatu.
“Acikin wani bakin dare mai duhun duhu daban taba tunanin zanga haske awannan daren ba wani haske ya gauraye inda zuciyan Zainabu Ummi take, kasan haske nada zafi a ido dakuma fata sai wannan hasken ya kasance mara zafi, mai taushi ce dakuma da tsantsa kyawu, kyawu irin wanda bantaba sanin akwaishi ba awannan duniyan sunan hasken nan NOOR wato NURA! Ana haka wata kalan guguwa mai karfi ya taso dake dauke da kifiyoyi guda uku masu zafin rabasheshen dalman wutan kauna ce ke tashi daga jikinsu, suna zuwa chak! Chak!! Chak!!! Suka sossoki zuciyata, kifiyoyin nan guda uku na dauke da kalma guda uku ne na farkon yace I nabiyun yace LOBE na ukun yace YOU!!!, I lobe you My Noor Baban Amalily” Yihuhuuuu!!! Nura yabuga ihu kaman dan daba dayasa su Musa duka suka juyo suka kalleshi yace “wlh Yarinyar nan ta tashi kaina, billahillazi dauko matata zanyi, kai dereba juya kan motan nan kaga

ku kusauka ku shiga dayan motan, ba’a taba gayama Nura irin wannan kalaman soyayyan ba, wayyoo zuciyata nima kifiyoyin dalman soyaya sun chakeni” tsayawa duk sukayi suna kallon Nura kaman kanshi ya kwance.

Hahahahah Guys rate sakon soyayyan yan kauyen M shakur naku, I crafted this on my own chaiii yayi making sense kuwa???😂😂😂😂😂

Ummi fa zata haukata mana Nura Hadiza sorry for you, just look at how Ummi ke feeding mijinki soyayyan kauye, soyayyan uneducated girl.

💫 MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE8️⃣
kaman ta mutu takeji tace “amman Nura kacika annamimin, makirin, munafuki maci amana da tsoron Allah, Nura wato all this while you’ve been fooling me kana soyayya da yarinyar nan kazo kasata tacemin zataje kauyensu duba kakarta kuka tafi kaje ka aurota, Nura yau 14days sau daya nayi magana dakai u don’t return my calls, u don’t reply messeges dina, Nura ni Hadiza kama kishiya wai Ummi, Ummi dai yar aiki na? Nizaka yaudara kaci amanata Nura, eh”? Hannunshi yadaura kan nata yacire daga gaban riganshi yace “bandawo gidan nan to fight with you ba so just respect yourself kidena haukan nan kar co wife naki ta rainaki” kaman ya zubama Hadiza fetur wucewa tayi stairs tace “durun uwan cowife, ita Ummi hartanada liver aure mini mijina? Wlh Nura auren nan trust me dream kakeyi baka isa bane kuma kayi kadan kamin kishiya na rantse mama da Allah sainasa gidan nan ya gagareta zama billahillazi la’ilaha illahuwa, babu macen data isa ta auri mijin Hadiza kai ko yar boko mata masu usuli da daraja basu isa su auremini mijina ba balle kuma yar aiki, mijina Ummi ta aura ni? Aiko tanaso ta mutu” da gudu gudu take hawa stairs daidai takai falon sama Nura daya biyota ya fizgota azuciye tai ihu tace “saken mini hannu Nuri” kobi takanta Nura baiyiba dakinta yabude ya jefata ciki yashigo shima tareda maida kofan yana rufewa yana saka key yazaro key ya jefa a aljihu dasauri ta taho wajen kofan tayi ihu tana dukan kofan da hannu tace “kabude mini kofa nafita I need to show that girl her proper place which is trash, wlh, wlh I will never share mijina da wata balle kuma Ummi yar aiki, kabude kofa! Nura open this door ko na fasa kofan nan” “Enough!” Nura yadaka mata tsawa da saida tadan firgita dan kaman zai daketa, nunata yayi da yatsa yana kallon kwayar idanun ta da idanunshi da sukai jajir yace “enough of your nonsense Hadiza! The only reason I even let you back into this house sabida Hajiya ne! Aure is not a do or die matter, idan kinga bazaki iya cigaba da zama amatsayin matata ba let me know I will let you go, but wannan haukan naki nagama dauka Hadiza your time is up, koki natsu and live peacefully under me ko u can leave the Marraige nagaji, nagaji da stupid, wild attitude naki always barking woo woo kaman karya haba! Don’t you get tired of shouting? Why do you think violence is always the way out for you? Kina behaving kaman ba mace ba, is something wrong with you upstairs I can take you to the asylum adubamini ke, nayi aure and so wat?” wani kalan kallo Hadiza kema Nura tunda ta aureshi yau kusan 10yrs kenan dan bata haihu da wuri ba yaune rana na farko da Nura yabude baki yamata masifa haka, bawai basa fada bane no sunayi but masifa ya kwakkwance mata haka yaune rana na farko, sosai take kallonshi Nura jikinta na bar-bar duk yanda taso ta daure ta cije tahana kanta saita kasa sabida yanda yakirata karya, harda mahaukaciya ma dan cewa yayi zai kaita asibitin mahaukata aduba ta, yana kuma threatening nata da rabuwan aure kawai saiga hawaye sharrrr ya sauko daga idanuwanta masu mugun zafi, muryanta babuma karfi balle kuzari tasake nuna kanta tace “Nuri ni? Ni kake gayama bakaken maganganu haka? Nuri nika tsana haka? U just called me a dog, mahaukaciya and so much more, Nuri you hate me sabida kayi aure? You hate the sight of me, Nura ni zaka cima mutunci ta hanyar auren yar aiki na? Idan ka tsaneni haka kagaji dani zaka iya cika ragowan saki biyun dasuka rage why marry maid dina? Kasan yanda nakeji azuciyana Nuri ni, kaci amanata, ka yaudareni, ka munafinceni” wucewa tayi dasauri taje gaban gado tazauna akasa ta kankame kanta tana shaking kaman ta haukace, saikuma tafara buga kanta ajikin gado jikinta ko’ina da bakinta na rawa tana maganganu. “yar aikina, yar aiki, Nuri ya auro mini yar aiki na, Nuri ya tsaneni, ya tsaneni, ya tsani ganina, ya cuceni, ya wulakanta ni, ya toxarta ni, Nuri zoka kasheni nasan bana duniya namutu kayi auren nan, aure fa? Aure Nuri

yayi aboye sai yau bayan sati biyu yake fadamin kuma yar aiki na, Ummi, Ummi, Ummi uhmmm Ummi”.

Nura kawai yayi shiru ya tsaya yana kallonta he can’t even remember the last time dayaga Hadisa na kuka haka maybe tun kafin aurensu, cus irin hard ass ladies dinnan ne ita, she’s in total shock dan bamatasan tana kukan ba, strong woman Hadiza ke kuka hakayau, he wanted to ignore her amman kuma saiya kasa ganin yanda take hitting kanta is getting serious sai kawai yawuce tabashi tausayi, kishiya koyaya batada dadi azuciyan mata but yazaiyi she pushed him yayi? Wucewa yayi yacire kayan jikinshi yarage daga singlet sai boxer, sannan yadauki wani bottle water daya gani adakin yataho inda take gently ya tsugunna agabanta ahankali yakai hannunshi yadaura kan fuskanta yana cire kanta daga jikin gadon dasauri ta kabarda hannunshi tana kuka wiwi komi najikinta rawa yake tace “kada kasake tabani da hannun nan daka taba wata, Nura nika yaudara haka kaci amanar alkawarin mu, Nura nizaka wulakanta ka tonama asiri ni Hadiza the mother of your kids, Nuri what have I done to you to deserve this eh? How can you comfortably hurt me this much? Nuri haka ka tsaneni?” girgiza mata kai yayi ya ijiye ruwan agefe ganin yanda jikinta ke rawa she’s seriously having a panic attack gumi na keto mata tana zufa duk kalan Ac dake dakin, ahankali softly yace “come here Hadiza, u are not in right state of mind yanzu kome nagaya miki bazaki gane menake cewa ba, zonan” da karfi yasata ajikinshi tana ihu kasakeni, sata akirjinshi yayi da karfi yana patting back nata kaman yakara cemata takara karfin kukan wani kalan kuka take kaman anmata rasuwa yacigaba da patting nata lovely yace “shiiii it’s okay” kankameshi Hadiza tayi sosai da sauri ita kanta batasan iyakan son datakema Nura ba sai yanzu dayay hugging nata kaman yana waking feelings din datake dashi for him she became so vulnerable and weak, yau batada karfin nuna she’s a strong woman dan zancen kishiyan nan hit her so damn hard, kuka take bana wasaba harda shesheka singlet din Nura ya jike sharkap da hawayenta, she’s just crying, crying bana wasaba kaman zata mutu takeji, wani luteten dunkulelen bakin ciki takeji bana wasaba, sosai Nura ke lallashinta ta hanyar buga bayanta yana manna mata few kissing agefen wuya like a baby, tana jikinshi cikin kukan tace “Nuri dan Allah kada kamin kishiya kaji, Nuri dan Allah wlh I can’t stand naganka da wata zan iya haukacewa barinma yar aiki na, dan Allah kaji Nuri mena maka zakamin kishiya da Ummi eh”? Yana bubbuga bayanta yace “Hadiza u are a very very stubborn woman, when I married u bahaka kikeba, I loved you kaman ba gobe you know, waye baisan kalan soyayyan damukayi ba, but everything changed damuka dawo garin nan, tunda na aureki baki taba cemin kinason kaza na hanaki ba, I change kayan daki anytime kikcemin kinason a chanza, I change cars for you, banwani damu da zuwa vacation ba but kinaso ke we go on vacation every year banda Umara da every now and then nake kaiki, have I ever wronged you kona hanaki abinda kikeso? Farko farko ai kinamin girki rana daya kawai kika ijiye, bakimin komi, baki damu dani ba nor my children wanda kinsan banda abinda nakeso aduniya kaman su, I can’t talk to you kafin nayi miki magana daya kinyi magana dari, kinamin ihu aka kaman yaron dakika haifa, bakiganin girmana ko darajata, Kona Hajiya, all I ask is for your attention and care, respect sannan kisa ido akan yarana but kin nuna ban isaba ban isa incemiki yi kazaba agaban idona zakice no, Bana iya tankwaraki ko kadan, u feel nidake daya ne, abu kadan kice feminism bazaki bari nayi demeaning naki ko belittling naki ba, you’ve been

maltreating me doing as u wish, Hadiza ni ba yaro bane am 49 clocking 50 Allah yahoremini arziki da abinyi all I want yanzu is peace of mind and watch my kids grow na barmusu this company suyi taking over but kinki cooperating, u pushed me so hard and kinfi kowa sanina banda son mata banda biye biye, I've always been a one woman's man but u made me look outside Alhamdulillah bantaba zina arayuwana ba and bazantabayi ba that's the reason nakara aure don na sami kwanciyan hankali" cikin kuka sosai tana wani kalan sauke ijiyan zuciya tace "to saika auri yar aikina" Yana tapping bayanta har lokacin yace "Ummi ce the only macen dake rayuwana banda ke, kema kinsan ko kallo mata basu isheni ba, halinki made me notice the girl, yarinyar is a very good girl, she's young, smart hardworking, she can cook and above all yarana na sonta sosai sais……." jin zafin yanda Nura ke yabon Ummi yasa cikin kuka Hadiza tace "banson ji, toka saketa dagayau kome kace nayi zanyi please ka saketa na yarda ta kwana agidan nan yau gobe da sassafe tabar mana gidanmu I promise zan chanza kome kakeso zan maka amman kasaketa please Nuri karufamini asiri, I can cook nima, gani hardworking, smart, intelligent kuma I'm educated unlike yar aikin, kasaketa wlh zan chanza namaka alkawari" ahankali Nura yajaye jikinshi dagana Hadiza yakalleta batare dayace komiba, fashewa da kuka sosai tayi takai yatsanta ta taba harshenta tace "na rantse da Allah Wallahi Wallahi Nuri kaji na rantse ko kasaketa zan dawo sak Hadiza na nada, nadinga maka komi, bazan kara bata maka raiba, please karufamin asiri kada kasa duniya tamin dariya akaji ka auri yar aikina, please kasake ta kaji Nuri" dan lumshe idanu Nura yayi yabudesu yakalli Hadiza dake kallonshi tace "kaji Nuri kasaketa" girgiza mata kai yayi ahankali yace "bazan iya sakin Ummi ba Hadiza!" Dum! Gaban Hadiza yabuga dasauri harsaida takai duka hannayenta saman kirjinta wani sanyi na ratsata tace "mesa Nuri bayan nagaya maka zanyi komi infact nama gama daukan yar aiki har abada, dakaina zan dinga komi and take care of su Amal maisa bazaka saketa ba? U don't need anything from her again, nice dama kuma nace zan chanza dagayau, maisa bazaka saketa ba"? Yana kallonta right in the eye yace "sabida nariga nakamu da sonta kaman yanda nake sonki!"
Tunda Allah ya hallito Hadiza bata tabajin wannan kalan pain din datakeji azuciyanta yanzu ba jin mijinta nagaya mata da bakinshi cewa yakamu da son wata kuma yana gayamata right before her eyes wai bazai iya rabuwa da itaba sabida yana sonta kaman yanda itama yake sonta wato harya soma raba musu komi equally irin ita da yar aikinta duka abu dayane yanzu azuciyanshi, kawai saitaji kaman zuciyanta ya buga kawai tai baya luuu bawai ta suma bane tanaji sarai yanda yake kiranta da yanda yariketa yana shafa ruwa a fuskanta kawai her energy is just on a zero level idanma akwai minus zero energy level nata na wajen, kaman ya lura da hakan hakan yasa Nura yadauketa ahankali yadaura kan gado ya kwanta gefenta tareda kashe wuta ahankali ya rungumeta cikeda lallashi yace "I still very much love you Hadiza don't hurt yourself okay, you are my first love Hadiza, Maman yarana, yaran dasuka zame mini haske arayuwana, u gave me the most beautiful, adorable and sweet kids aduniyan nan no one yataba bani kalan gift din dakika bani Hadiza how can I even hate you eh my Didi"? Bakaramin tausayi tabashi ba, wlh yayi auren nan but ko kadan baimayi tunanin kalan wannan reaction din zatayi ba he was just expecting haukanta as usual baitaba sanin she will be this down ba and weak tana kuka haka having panic attack hakaba, so dama tana sonshi, batason taganshi da kowace mace but shine takemai all abubuwan datake, lallai kishi babban abune awajen mata.
Gently yadaura bakinshi kan nata hannunshi yana share hawayen dake fitowa daga idanunta

yana kissing nata kafin ahankali yafara yunkurin making love da ita cikeda rashin karfi dakuma kuka cikin muryan bakin ciki tai ihuu tace “kada kasake ka sadu dani Nuri gabanka daya shiga jikin yar aikina bazai kara shiga jikina ba wlh kajini” hada bakinshi yayi da ita bai kara bari tayi magana ba dudda batada karfi saida tai kokawa dashi dan bataso yamata wani abuba but still saida yayi sexing nata da karfi da yaji she have no option but to succumb jikinta ya mutu gabaki daya kawai sai kuka takemai, dole ma Hadiza taso mijinta tayi kishinshi, Nura nada kirki ne sosai lallashinta yake bana wasaba yadinga shafa kanta duk uban bakin cikin datake ciki saida soyayyanshi yayi suppressing nashi bacci yayi awon gaba da ita sai ijiyan zuciya taje saukewa ajikinshi he cant lie is just soothing sex ne kawai wannan to calm her down dan sex na rage bakin ciki da damuwa, that fun da excitement dinnan ajikin Ummi kadai yakeji, lullubeta yayi da bargo yatashi bayinta yawuce yaje yayi wanka yafito kayanshi yasake maidawa yayi wajen kofa ahankali yabude yafita yaranshi yafara dubawa yayi mamaki ganin duk Ummi tamusu wanka sunsa kayan bacci tarufesu da bargo tarage musu AC addu’a yamusu yafito dakinshi wanda yake dakin Ummi yanzu yawuce ahankali yabude kofan tana kwance akan gado tai lamo dudda ba bacci takeba dan takasa bacci tun bude kofanshi taji, zama yayi ahankali bakin gadon yakalli fuskan Ummi feeling a bit bad cus baimata saida safe ba hannunshi yakai ya shafa kumatunta tareda dukowa ya manna mata kiss akai yace “good night Hajiya Ummi” sannan yamike yaje gaban wardrobe ya debi some clothes nashi yawuce yafito tareda rufe mata kofa yakoma dakin Hadiza hawaye Ummi taji sun gangaro mata daga ido kawai jitayi tana bama kanta tausayi most maganganun Hadiza tajisu dan maganan Hadiza ihu ne, maganganunshi ne batajiba but duk taji abinda Hadiza tafadi da cewa yasaketa datayi zata chanza shiyafi komi tada mata hankali saitaji takara raina kanta tana tunanin kodai Auren nan kuskurene, ita Allah yasani ba kwacema Hadiza miji tayiba babu wani mugunta aranta but tasan harga Allah dan bazata iyama Allah karyaba tanason Nura tana mutuwan sonshi, batajin zata iya rayuwa ba yasaketa ina! Tanason mijinta fa kome zatayi zatayi dan yazauna da ita karya rabu da ita, tuna yanda har kaman ya sadu ma da Hadizan dan taji Hadiza nacewa kada ka sake yasadu da ita da gabanka daka sadu da yar aikina, hawaye ne yazubo mata tasan ita yar kauyene bata waye kaman Hadiza ba sannan batai karatu ba but tanada hankali, sannan ta girma, ashirin da uku tana neman da hudu ba wasa bane, tasan menene miji sannan tasan banbancin miji mara kirki damai kirki, dan ta taba Auren mara kirki mugu yanzu yanda Allah yabata miji mai kirkin nan, wlh zatai kome dazatayi ta siye zuciyanshi takuma kara siye danginshi ta samanma kanta lafiyayyan wuri axuciyanshi, koda basuyi wani soyayya kafin aure ba yau alkawari takeyi zata samama kanta waje, bazata tabama Hadiza mugun abuba kawai dai bazata bari wani mahaluki aduniyan nan kap yarabata da Alhajinta bane, dan bata tabajin tanason abu kaman yanda takejin son Alhaji ba, yanda Allah yabata miji nagarin nan dare daya batare datai wani abuba bazata taba bari ya subuce mata ba tashigo rayuwan Alhaji tashigo kenan har abada Wallahi kuwa!.
Tai maganan tana goge idanunta tasake juyi agado takasa bacci, sati biyun nan datayi tana kwana ajikinshi saitaji yau baccin ya gagareta, tashi tayi tafada bayi tafito daure da alwala tahau kan dadduma tayi salla tafara addu’a kan soyayyan ta da aurenta da Nura.

Auuuucchhh I’m too emotional naso nacigaba but let’s take a moment of silence for our lioness Hadiza da Nura yay shattering ego nata today😎

Poor thing couldn't hold back those tears 😭 ashe ta iya kuka😂

Auuu now I feel bad for HADIZA wlh, kishiya fa batada dadi but kuna ganin misali da Nura zai saki Ummi zata chanza????

Wai HADIZA ce ke kuka haka our strong fire for fire, feminist woman😂😂

Ummi dai tace taga miji, kuma tasamu gidan miji, zama daram injita mutuwa kadaice zata fitar da ita daga gidan mijinta Nura😂

Allah karabamu da kishiyoyi irin Ummi mayun maza😂😂😂

Anyway my people don't forget to join MATAN AURE CLASS dina with just 1k today and tomorrow 💃

💫 MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE1️⃣3️⃣
My people wai kunji labarin BUKKISH FABRICS N MORE??
Ku saurara kunji bantaba ganin masu harkan Atampas, laces dakuma lafiyayyun gangariyan ready to wear kaya ba dake badawa akan sari kwashakwasha kaman BUKKISH FABRICS N MORE ba, both
wholesales n retails sunayi, sunefa akama taken PAY LESS STAY IN FASHION, wato ki biya kudi kadan amman ki saka kayan yayi adama dake, ku tura musu message now ku kwashi kaya with little kudi, danna link din nan kimusu magana👇🏼
wa.me/+2349034368170
Zaku iya duba shagonsu a TikTok- Bukkish fabrics n more

13
Wuraren 5 Nura yatashi daga bacci, Hadiza dake gefenshi yakalla har lokacin bacci take, sauka daga kangadon yayi yawuce bayi, wanka yafito ya shirya cikin wani jallabiya yana zuba kamshi yazo gaban gadon yadago Hadiza like a baby softly yace "jekiyi wanka kizo kiyi salla My Didi" bude idanunta tarr Hadiza tayi takalleshi yamata wani irin kyau yau saita ganshi yafi koda yaushe kyau dasauri takai hannunta tadaura kan fuskanshi tana kallonshi everything is coming back to her daya faru da ita jiya, cikin murya mai raunin gaske tace "Nuri mafarki nayi ko? Ai baka auri Ummi yar aiki na ba ko"? Dan murmushi kadan Nura yayi yakai hannunshi yacire hannunta dagakan fuskanshi yace "tashi kije kiyi wanka kiyi salla Hadiza" yana maganan yawuce yabude kofa yafito dakin Ummi yabude yashiga bata kan gadon harta gyara gadon,

yabi dakin da kallo komi a gyare tsaf jin karan ruwa abayi yasa yaje gaban bayin ya tsaya tareda knocking cikin cool voice yace “wankan me kikeyi? Mafarkina kikayi?” Ummi nacikin bayin akunyace tace “wanka kawai nakeyi, ina kwana Mijina dafatan kayi bacci mai dadi kuma katashi lafiya?” Dan ijiyan zuciya Nura yasauke ahankali, he loves how Ummi always greet him, gaisuwa takemai not common gaisuwa but gaisuwa mai dauke da details, baki yabude zaiyi magana saikuma yace “ba’a magana abayi, maza kifito kiyi salla natafi masallaci” “uhm Uhm” tafadi amatsayin amsa hakan yasa yayi murmushi yace “naughty gurl” wucewa yayi yasauka kasa, yau monday he wants to see Hadiza ta chanza, he wants to be miji mai adalci, he just pray and hopes Hadiza will cooperate which he’s highly doubting it, dan yau girkin ta yakamata ita zatai girkin breakfast dasauransu, ijiyan zuciya kawai yasauke yatafi masallaci he’s just hoping zai dawo yaga tayi dama ga gidan na bukatan gyara.

Bayan Ummi tayi salla wani lafiyayen super tadauko tasaka cikin atampopin daya dinka mata dogon rigane fitted tazauna gaban madubi ta shafa hoda tasa kwalli tashafa wani pink janbaki sannan tayi dauri bayan tasaka dan kunne, shiru tayi tanason tafita taje ta daurama yaran nan girki zasuje school but tana shakkan Hadiza deep down kuma tasan idan tabari babu mai musu at the same time tana tsoron kada ace tayi shishigi bayan yau girkin Hadiza ne amman kuma tanaso tanunama Hadiza bawai dantaci mutuncin ta ta auri Nura ba ita kawai tanason Nura ne, kusan 3min tayi ahaka sanan tabude kofa kaman munafuka tafito ta maida kofan tarufe batare data bari yayi karaba tawuce tasauka kasa falo tafara gyarawa agurguje da dinning ta tattara duka kwanukan cokalan tawuce dasu kitchen tashiga hada abincin gida tanama Hajiya girki tana gyara kitchen din duka at the same time.
6 Nura yashigo gidan yau bai wani zauna a masallaci ba dan baiso Hajiya tafito daga daki ta nemi Ummi da bala’i, falon daya gani harya chanza kama yasa yayi shiru dan kawai ranshi yagayamai Ummi ne barin dayaji motsi a kitchen kitchen din yawuce a kofan ya tsaya yana kallonta tuwo take tukawa, ahankali yashiga cikin kitchen din dasauri Ummi tajuyo jin motsi ganin Nura ne yasa tayi murmushi tace “Sabahal khayri Baban Amanu” takowa yayi yazo inda take sai kawai ya rungumeta ta baya yana shakan kamshin datake yayi shiru itama saitai shiru tanajin saukan ijiyan zuciyanshi, bai damu dadan zufan datakeba ya goga gefen fuskanshi anata kaman mai whispering yace “maisa kika shiga kitchen yau ba girkin ki bane”? Dan shiru tayi kaman bazata ce komiba cikeda hikima tace “Anty tana zuwa aiki ni bana aiki, shine nace bari nafito nakama mata ta hanyar yin abincin kari saikuma inaso nama Hajiya girki dazataci kafin ta tafi asibiti, tunda nadawo nizan dinga mata abinci, ita nakema tuwon alkaman nan” shiru Nura yayi yana rungume da ita abayanta, akwai wani kalan hikima da Ummi kedashi da wlh ko educated mata dasaukai karatu daidaikune kedashi, yarinyar is good with words, Ummi is smart, tanada broad hikima kan zaman aure wanda yasan aikin Gwaggon tane, yanda ta tashi da safen nan tanama mahaifiyarshi girki abin warm his heart, dago kanshi yayi ya manna mata peck akumatu yace “godiya nake Hajiya Ummi” dasauri tace “nika dainamin godiya dan nama Mamana abinci” murmushi yasakeyi saikuma kawai yasaketa tareda juyoda ita yayi hugging nata so tight yace “thank you Hajiya Ummimy na” akunyace tazare jikinta daga nashi tace “tuwo zai kone” murmushi yamata sabida baiso tai wani abun yace “bari naje natada yaranki namusu wanka na shiryasu” dasauri Ummi tace “kabarshi zan musu zansa sanwan miyane nazo sama”

girgizamata kai yayi yace “aikin zai miki yawa just do the cooking zan musu wankan” yawuce kofa saikuma yajuyo yace “kimini shayi” gyadamai kai tayi tace “angama maigidana” murmushi yayi yabita da kallo kaman yazo yamata wani abu saikuma dai yadaure yafita dan murmushi Ummi tayi dudda tanada damuwa tana cikin shakku da fargaban karya saketa bazata taba nunamai ba tama kanta alkawarkn nan.

Nura na zuwa sama baimaje dakin Hadiza ba dakin yaran yaje direct Aman yafara tarawa yakaishi bayi yasamai brush sannan yafito yaje dakin Amal yadauketa yakaita bayi yamata brush da wanka yafito da ita da towel yakoma dakin Aman yamai wanka shima wlh aikin yara is not easy yafito dashi da towel ya kwashi kayanshi sukazo dakin Amal anan yashiga shiryasu sunamai hira yana wasa dasu.

My people wai kunji labarin BUKKISH FABRICS N MORE??
Ku saurara kunji bantaba ganin masu harkan Atampas, laces dakuma lafiyayyun gangariyan ready to wear kaya ba dake badawa akan sari kwashakwasha kaman BUKKISH FABRICS N MORE ba, both
wholesales n retails sunayi, sunefa akama taken PAY LESS STAY IN FASHION, wato ki biya kudi kadan amman ki saka kayan yayi adama dake, ku tura musu message now ku kwashi kaya with little kudi, danna link din nan kimusu magana👇🏽
wa.me/+2349034368170
Zaku iya duba shagonsu a TikTok- Bukkish fabrics n more

Nan da nan Ummi tagama abincin Hajiya tahada breakfast tasoya chips ta sossoya eggs da sausage ta hadama su Amal abinci a lunch bag tadauko tafito zata ijiye a dinning tahada ido da Hadiza dake tsaye a dinning din tana sanye da riga da wani palazzo trouser mai shegen kyau na material pink tayi folding hannunta a kirji tana kallon Ummi da jajayen idanunta dasuka kumbura sukai jazur kaman mai ciwon ido abinku da faran fata, chak Ummi ta tsaya anan gaban kitchen din takasa karasowa dinning din ayanda zuciya ke diban Hadiza jitake kaman tazo ta shake Ummi tamutu gabaki daya, daga kafanta tayi tafara tafiya ahankali akuma zuciye tace “how dare you Ummi kika aure mini miji? Ni Hadiza kika aurama miji? Kin manta lokacin dana taimaka miki kina neman aiki ido rufe wayanda kikema aiki ada sunyi japa sun koma Canada anata gantali dake a Abuja ana nema miki gidan aiki baki samuba, na taimaki rayuwanki nabaki aiki nakuma biyaki da kyau, yan aiki da ake biya duba ashirin, dubu shabiya but ni nace zani dinga biyan ki dubu hamsin sabida duka gidana zaki kula dashi da yarana sabida bani zama ina fita aiki, sakkayan dazaki mini kenan ki aure mini miji, mijina Ummi? Nura na?” Ihu Hadiza tayi tana tafiya tace “ki daga fuska ki kalli kwayar idanuna bakar munafuka, algunguma, makira bakar mayya, butulu, shedaniya watsassiya, sai bayan kin aureshi zakizo ki kasa kallona kina sunnar da kanki kasa kaman baiwar Allah, dagakai ki kalleni Ummi, nace ki kalleni!” Hadiza tai maganan tana ihu daidai tana kaiwa gaban Ummi ta finciko gaban riganta gamgam tawani kalan jijjiga Ummi ta mugun makureta tana kallon fuskanta tace “wulakantacciyan yarinyar irinki harta isa ta aure mini miji, ni Ummi kina yar aiki na, sabida ina fita na barmiki gida kikai using opportunity nan kika auri miji na eh”? Hadiza tai maganan tana buga Ummi abango saida Ummi tasaki lunchbag din kasa tai kara Hadiza ta makure mata wuya tace “wlh, wlh, yau saidai afutar da gawanki ki daga gidan nan, ke! Dakikiyar yarinyar irinki tayi

kadan tace inyi kishi da ita, bazan taba iya raba Nuri dakowa ba balle ke jinjiran yar iska kinajina? I will kill duk wacce tace zata auri Nuri na, dagani sai shi har lahira” “Hadiza!” Nura daya sauko tareda yaran suna surutu ya hangosu da gudu gudu ya sauko daga bene yazo wajen da sauri ya bambare hannun Hadiza daga wuyan Ummi yace “are u mad kasheta zakiyi”? Tari Ummi tahauyi sosai tana nishi idanunta sunyi ja, cikeda fada Hadiza tasake yowa kan Ummi tace “Nuri ba ruwanka awannan fadan is between me and this this munafukar makiran yarinyar” dasauri Nura yatura Ummi bayanshi daidai su Aman suna zuwa wajen da gudu zasuyi wajen Ummi suna “Anty Ummi sorry” rikesu Hadiza tayi dasauri tana tafarfasa tace “ku zonan ina zaku?” Dasauri Aman yace “wurin Anty Ummi, u hurt her Mom” cikin ihu Hadiza kaman zata make Aman tace “waye Ummi? Me kuka hada da ita? Who is that girl to you? Dagayau baku ba ita Aman kaida sister ka, Ummi is a bad evil person, babu wanda yataba cutata arayuwan nan kaman ita, bantaba nadaman abu arayuwana kaman nai nadaman ranan dana dauketa aiki ba, kar wanda yasake kiran sunanta cikinku agidan nan, Ummi is the worst evi…….” “Hadiza!” Nura yasake kiranta ranshi abace dasauri Hadiza takalli Nura tace “what!? Nura I said what kake kirana? Don’t tell me ka yarda cewa yar aikin nan son yarana take? Okay bakaso nagayama yarana she’s evil, Lemme tell you something today Yarinyar nan bata taba son yarana ba, she just use them tayi winning heart naka da nawa damuka yarda ta zauna gidanmu, bata taba son yarana ba, she use them taja ra’ayinka kasota, tunda ta kyallara ido taga muna biyanta 50k instead of 20-15k da ake biyanta a inda tabasa aiki ta kudurci aniyan saita aureka, saita zama matarka, saisa taja yaran jikinta sabida tasan you love yarannan morethan ur life sune the way to your heart, your weakest point Nura, open your eyes and see Ummi played you and me, Nuri Mezakayi da this village evil girl yar aiki fa eh Allah kadai yasan mazan mutane nawa taci, I will post her pictures on social media to makesure babu wanda yakara daukanta aiki a abujan nan tunda she’s a witch, ka barni naci bura’uban yarinyar nan Nuri tasan cewa Allah dayane” Hadiza takaima Ummi nushi Nuri yatare hannu ta hanyar rike hannunta gam cikin kakkausan murya yace “karkiyi kuskuren tabamin mata Hadiza stop all this thing!” Nura yayi ihu saikuma cikin turenci yace “I’ve given this respect leave this girl alone before I disrespect you in front of her” tafi Hadiza tayi tace “akwai disrespect daya wuce na kariga ka aurota ka kwanta da yar aikina taga kalan buranka dani uwar dakinta keci akwai Eh Nura talk!” Hadiza tai ihuu dayasa Nura ya runtse idanu yabude su ahankali yakalli Aman da Amal daduk ke kallon Maman nasu sunyi tsuru tsuru, dan juyowa kadan Nura yayi yakalli Ummi dake labe abayanshi yace “tafi dakinki” gyadamai kai tayi tawuce Hadiza zatayi kanta Nura yariketa gam, Hadiza tabita da kallo tana duramata ashar tace “munafuka, jibeta kaman bushashen kifin dayay kwantar a kasuwa oporoko, banda ma namiji kanshi kaman kan jarirai ne mezakayi da yarinyar nan mai kama da fiffiken kunkurun dayay shekara dari da uku aduniya eh, makira  zuciyanta yafi fatar jikinta baki, tanaji da lebe kaman wacce ke aiki agidan giy……” “Hadiza!” Nura yayi maganan yana fizgota su Aman suka fashe da kuka Nura yakalli yaran saikuma yasaketa yace “look at yaranki ko breakfast basuyi ba zasuje school kina haukan nan bakisan zaiyi affecting mental health da cognitive development nasu ba” cikin fushi tace “eh bazasuyi breakfast dinba ka gayama yarinyar chan bata ba yarana, kada ta kara dafa musu abinci kota musu wani abu, wlh ko hannunta nagani akan jikin yarana kome namata ita taja and kada ka ta kara shigan mini kitchen” Nura yana wani kallonta yace “kitchen banaki bane, duk wani abu naki na kitchen din nabaki dama ki kwashe ki ciresu daga kitchen din zan sayo wasu nasa cus Ummi will enter this

kitchen and cook for me" Nura yakallesu yace "zo kuyi breakfast" rike hannun yaran tayi tace "Nura bari kaji yesterday you took advantage of my fragile state kayi yanda kaga dama dani not anymore, billahillazi Nura zan nuna maka cewa yimini kishiya was the worst mistake daka tabayi arayuwan ka, bakana fadin bakada kwanciyan hankali ba yanzu kafara ganin asalin rashin kwanciyan hankali, muzuba nidakai I will deal with you and deal with that thing daka kawomin gidan nan as matan ka, bakasan ba'a wasa da fire ba because u will get burn, Nura I will treat you f*ck up wallahi kuwa" sosai Nura ke kallon Hadiza but sabida yaran saiyayi shiru yatako har gabanta yaduka yakama Aman da Amal dake kuka looking terrified ya karbe su daga hannunta yace "bani yarana" yajuya zaiyi dinning dasu kafin yaje Hadiza tarigashi zuwa dinning din duka abincin da Ummi takai dinning dan breakfast Hadiza ta kabar, dasauri Nura yaja Aman baya dan yadauki Amal gudun karya kone da ruwan zafi yana kallon Hadiza, ahaukace ta duka ta kwashi lunchbox na yaran da Ummi ta watsar akasa dataji shaka dazu ta bude tana ciro komi tana zZzagewa akasa tace "baza'a aci abincin yar aikin ba, yarana bazasu karacin abincinta ba, nace baza'a ciba, angama cin abinci again, Nura that peace dakace bakasamu dani ba ajikin yar aikina zaka samu wlh, wlh, wlh bazaka sameshi ba, Nura u will never know peace now dakamin kishiya I swear by Allah" sosai Nura ke kallon Hadiza kaman ba itane tagama kuka jiya kaman wacce ke shirin mutuwa ba, baice mata komiba yajuya yakoma falo yazauna yaciro wayanshi yakira school din yaran yace abasu breakfsat da lunch yau daidai motan school din zuwa, lallashin yaran yayi yadauko juice a fridge yabasu sannan yafita yasasu a school bus sannan yadawo cikin gida Hadiza na tsaye a tsakar falon tarike waist nata tan kallon Nuran.

Baiko kalleta ba yawuce zaiyi stairs tabishi da sauri tana ihu tana surfafa masifa tace "bakaji kunya na ba sabida kaine babban munafukan mazan duniya, Nura the president of MMA! Mugayen Maza Association, zaka kama ka auremini yar aikin dana samo nakawo gidan nan, kabita har kauyensu ka aureta kaje kayi honeymoon da ita batare daka dauki wayana ba for that 2weeks,  shine kanada audacity kazo da daddare ka lallabani kana samin jikinka ajikina jikinka daya hadu dana yar aikina eh Nura? I looked up to you kullum as a role model cus Nadade banga namiji mai hankalin kaba, but I was wrong gaskiyan bature ne dayace a fool at 40 is a fool forever dan tell me why will a sensible, educated wise old man zai kama ya aurowa matarshi yar aikinta? Nura yar aikina ka auromini sabida daidaicewa da wawatsula" uppan Nura baice mataba wardobe nata yabude yadauko kayanshi yawuce yafito daga dakin duk tana binshi yaje dakin Aman ya ijiye komi kan gado yafada bayin yayo wanka yafito yadauki cream din Aman yashafa still surfafa bala'i Hadiza take tsaf yagama yafito yasauka kitchen yaje yadauki babban kulan dake kan Island Hadiza takawo hannunta anan ne Nura yace "idan kikai kuskuren ko gigin taba abincin mahaifiyata Hadiza I will show inda haukanki ya tsaya anan nawa yafara" yana maganan yawuce ta yafita tabiyoshi tace "ai dama nasan kai mahaukaci ne dan mahaukaci kadai zai auroma matarshi yar aiki" fita yayi anan gaban kofa ta tsaya tana kallonshi dan bataso tafita tana fada, estate dinsu da ake ganinta as don aga tana fada, abincin ya ijiye a bayan mota ya kulle motan yadawo cikin gida Hadiza tasake binshi kitchen din yashiga ragowan friend Irish daya gani a pkate da egg yadauka, spoon yadauka yafito Hadiza nabiye dashi tace "ina zaka da abincin nan eh, Nuri ina zaka da abincin nan"? Dakin Ummi yabude yashiga biyoshi Hadiza tayi ciki ga mamakinta Nura just pushed her outside yamaida

kofan yarufe yasa key tahau buga kofan da gudu tana ihu. “Nura ni kai pushing outside like that eh? Wlh wlh sainayi maganinka dakai da karuwan nan daka ijiye adaki” kallon Ummi yayi dayagani kwance kan gado kaman marainiya idanunta sunyi ja amman ba kuka takeba zama kusada ita yayi kan gadon yana ijiye abincin agefe murmushi Ummi tamai tace “shine saika kawomin abinci maisa kakemin aik…..” hannu yadaura akan bakinshi  alamun tamai shiru hakan yasa tai shiru yakai hannunshi yadagata wajen window dakin yayi da ita ya yaye window yadaga wuyanta yana dubawa yana tattabawa ganin yadanyi ja yace “dazafi” dasauri ta girgizamai kai tace “ba zafi” yana kallon kwayan idanunta ahankali yace “mesa baki gudu ba dakikaga zata miki wani abu ko kiyi ihu ki kira sunana what it tamiki wani illan?” Murmushi tamai tacire hannunshi daga wuyanta tace “Anty bazata min wani illa ba ba muguwa bace, kawai fushi take sabida mun mata laifi” dan shiru Nura yayi yana kallonta saikuma ahankali yace “Ummi aure ba laifi bane like I said ranan nan ko nan gaba naji ina bukatan wata matan zan iya nakara aure, mata hudu zan iya aura” Ummi na kallonshi tace “Anty na sonka sosai, kuma soyayyan yasa take fushi haka” yana kallon kwayan idanunta yace “kefa?” Murmushi tamai tace “nima ina sonka sosan bala’i, tafashashen so ma nake maka my Noor bai huce ba” yana kallon bakinta yace “Allah yar matata”? Dan dariya tamai tace “da gaske, ba Hajiya zakakai asibiti ba lokacin na tafiya kazo kaje” dan ijiyan zuciya yasauke yace “banso na bar gidan nan ahaka” dasauri Ummi tace “babu abinda zai faru kaje ka kai Hajiya asibiti abincinta na kitchen a flask kadauka” ahankali yana kallonta yace “nadauka” ganin ya tsaya yana kallonta yasa tace “menene?” Yana kallon kwayan idanunta yace “Aman da Amal yaranki ne kada ki rabu dasu sabida Maman su kinji” murmushi tamai tace “tom Baban Aman da Amal” rungumeta yayi ahankali yace “kiyakuri da abubuwan da Hadiza tafada miki kinji, kada ki riketa azuciyanki, kiyakuri Hajiya Ummi” dudda taji wani iri amman tadaure tafita daga jikinshi dasauri tace “komi yawuce katafi” Gyadamata kai yayi yace “biyoni ki rufe kofan da key” biyoshi tayi yace “kiyi breakfast zan dawo yanzun nan” gyadamai kai tayi yabude kofa yafice tasa key dasauri ganin Hadizan na tsaye awajen yawuce Hadiza tasakebin Nuri tana masifa tace “tell this girl ko dakin yarana takara shiga wlh saina watsar da ita, karta kara taba wani abu that belongs to me in this house wucewa Nuri yayi yawuce yashiga motanshi yabar gidan Hadiza ta dawo sama tashiga surfafa zagi na uwa da uba ma Ummi, Ummi tayi shiru.

Tashi Hadiza tayi ganin taki kulata tazo gaban dakin ta bubbuga tace “kifito mana idan ke diyar halas ce yadade da tsufa a inda yatafi yanzu, dagani saike agidan, kifito muyi magana woman to woman mace to mace, cus inada wasu abubuwa dazan fada miki kifito Ummi kibude kofan nan kifito” Hadiza tai dariyan keta tana tafiya tace “dan kauye dan kauye ne, ni wlh at this point ma tausayi kike bani Ummi, bari nafada miki wani sirri dabaki sani ba for free” tasake shiru tace “kinga Uwargidan miji itace kokon rayuwanshi, Ummi bar ganin kin zauna agidan nan kinga nida mijina munada yan matsaloli sai kikai yan dabarun ki na gidahuman kauye kikaja ra’ayinshi ya aureki to tsaya kiji wani abu dabaki sani ba game da mijina Nura”  Hadiza takara murmushi tace “Nura kwata kwata dakikan mata dabasuyi boko ba basa burgeshi kije ki tambaya kiji, Baban Nura professor ne a BUK abinda yadawo dasu kano kenan daga zamfara, Hajiya wannan dakike gani tsohuwan secondary school English teacher ce, kannen Nura kap dukansu graduate ne dasuka gama jami’a har Meena Kwanan nan tagama bautan kasama, kinganni nan

Nura bai yarda ya aureni ba saida nagama jami'a gabaki daya muna dawowa garin nan yasa nacigaba da karatun wuce jami'a wato masters sabida dan boko ne shi, yanason yaga matarshi yar gayu yar boko tanuna ma business partners nashi, kinsan mesa nake gayamiki maganganun nan"? Hadiza tasake dariya tace "sabida ke dakikiyace jaka kuma, Nuran dakike gani kin aura yau Nuran daya sami yar karaman matsala da Hadizan shice, kije kano ki tambaya abaki labarin kalan soyayyan damukayi, ban bashi jikina ba damuwa da sha'awa kinsan mutum shiru shiru mara magana yasa yaga kaman yana sonki wlh Ummi kindaiji na rantse miki Nura baya sonki sabida baki cikin kalan ko siffofin matan dayakeso" wani abu Ummi taji ya tsayamata awuya chak yaki wucewa takasa hadiyewa, Hadiza tace "bansan ko kinji magananmu jiyaba, jiya nace yasakeki zan chanza Ummi kinsan meyace mini"? Hadiza tai maganan cikeda tsantsan tunzura mutum saikuma ta kyalkyace da dariya tana tafi tace "wohoho ta yanda zaki gane kin tafka shirme Ummi kin auri mijina kin dauka kin sami gidan mijin cemin yayi nafara chanzawa tukunna yagani, idan na chanza nakoma Hadizata nada zai sakeki ki tafi mucigaba da rayuwanmu mukadai hankali kwance" dasauri Ummi ta tashi daga gadon zuciyanta na rawa tanajin wani iri, Hadiza tace "haka yadinga lallabani har saida ya samu nabashi hakkinshi that means keba komi bace awajenshi ba sati biyu dakukai kuna amarci kaman yanacin kashi haka yaji saida ya kwanta dani jiya yajishi daidai, yajishi damdam yajishi yakoshi, kuma kada ki manta rashin jituwan damuka samu dani da dashi yasa yaje yama nemeki" hawaye Ummi taji sun sauko daga idanunta, Hadiza tace "Ummi ki rubuta ki ijiye kwanan nan Nura zai sake ki kibar gidan nan dan bazai taba hada jini da jakan kauye ba da turenci nan nan bata iyaba wlh saiya sake k……." Bude kofan Ummi tayi dasauri tafito idanunta sunyi jazur tahada idanu da Hadiza for the first time tunda tadawo gidan tace "Hadiza kinyi kadan ki rabani da Nura" sosai Hadiza ke kallonta ganin idanunta sunyi ja maganan ta shigeta kenan yasa ta taka zuwa gaban Ummi Ummi ta tsaya chak tana kallonta ba gudu ba jada baya, Hadiza namata wani kalan kallo tace "nabaki daganan zuwa sati biyu saikinbar gidan nan dan baki da waje awajen mijina" Ummi na kallonta tace "Hadiza ban auri Nura dan na kuntata miki ba, shiya nemeni da aure na aureshi kuma magana daya zuwa biyu zan fadamiki, nifa nayi miji kuma naga wajen zama, zama kuma daram! Wallahi ko ana hamaza hamata bazan rabu da mijina ba, barima kiji mutuwa kadaice zata iya fitar dani daga rayuwan Nura!" Hannu Hadiza ta daga zata kaima Ummi mari Ummi tarike hannun gam idanunta sunyi masifan ja kirjinta na tafarfasa itama jin ance Nura zai saketa tace "Hadiza kul!" Ummi tazare mata idanu kaman yar daba tace "dazu nariga nabarki kinmin hukunci sabida nasan ban kyautamiki ba na auri mijinki daya nemeni amman yanzu kikai kuskuren dukana Hadiza kin tuna kalan dukan da Meena tamiki"? Ummi tayi maganan tana kallon kwayan idanun Hadiza kaman yanda Hadiza ke kallonta mamaki yagama kasheta, Ummi tace "wlh saina miki dukan dayafi wanda Meena tamiki domin shiru shiru ba hauka bane, dan hakin daka raina shine yafi tsole ido, kul Hadiza! Wallahi kul! Duk abinda zakiyi kiyi but Ummi tariga tayi miji, kuma taga gidan miji, danhaka zama daram, dam, damm ehe! Sai kija please ki rungumi sorry dan haka askus me" ta yarda hannun Hadiza a air tawuce takoma dakinta tarufo kofa tasa key Hadiza tasaki baki mamaki ya cinyeta har zuwa bone marrow, she was like wattt! Ita village girl dinnan tama rashin kunya haka? Askus, askus? Did she just said excuse me as askus me? Sai kawai Hadiza tahau dariyan kuka, she's laughing so hard and crying so hard as well, ita Nura zai auroma wannan jahilan askus me yar kauyen yarinyan???? Wow lugubrious!!!!!

Mata Mata mata sau nawa nakira mu???
Please we should all learn to stop abusing opportunity sabida idan wasu suka sami that opportunity there's nothing u can do in this world dazaisa su saki that golden opportunity daya shigo musu.

That is what happened between Hadiza and Ummi, Allah yama Hadiza kyautan close to perfect husband but she abuse everything and toss him outside like a coin, Ummi grabbed that coin tace atafau koda za'a guntule hannunta ne she won't let go off wannan coin din, wazakuyi blaming wacce tai tossing coin din ko wacce grab the coin???

Sainaji daga gareku and always remember shi opportunity sau daya yake zuwa miki.
Allah ya kiyaye and see you'll Saturday  Fanmily and Askus me❤️

WEEKEND PROMO💃💃

I have special announcement masu son shiga class na MATAN AURE you can all pay 1k now kafin Monday yakoma 2k, registration is still ongoing kafin murufe.
🔊🔊🔊🔊🎊🎊🎊🎊🎊

Don't miss MATAN AURE dina class for anything, I will give you all!!
Sirri zan baku da dama
Zan koya muku how to love mijinki in your own way kaman yanda Ummi keyi.
Shagwaba, iya magana 🥰
Uwa uba iya kwanciya❤️, yanda ake siyan zuciyan miji, how to steal heart na Inlaws naki and so much more.😍
Idan kina tunanin asiri ko kayan mata ke siyan zuciyan miji come to my group na nuna miki gaskiya.
HAUSA CLASS NE BA TURENCI BA

REGISTRATION IS 1k NOW

6353995766 M Shakur world Moniepoint
Send ur evidence of payment ta PC zanyi adding naki a group.
click on this link and chat me up directly +2347012181461
💫MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE1️⃣4️⃣

Wai yan uwa yau magana ake ta kayan dadi da shan dadi, kun gane irin juice dinnan mai kaloli daban daban, kiga juice din kaman duka tattalin arzikin Nigeria ne aciki?? To ku tsaya kuji labari yau nakawo muku MOCTAILSBYTEEHA indai magana ake ta harkan Mocktails, milkshakes, frozen Mocktails and fresh juice 🥤 babu part two dinsu akap yanar gizo, zaki dan hada wata liyafa? Kirasu sumiki handling harkan abubuwan jika makoshi, for weddings, naming ceremonies, dinners, birthdays, graduations e.t.c name it zasu miki chat them up now ta hanyar clicking on this link👇🏼 karkuji tsoro service dinsu is affordable
wa.me/+2348168045600
Idan kinason kiga hotunan kalolin juice dasukeyi da sauransu check them out a IG AND FOLLOW THEM❤️
Instagram handle @mocktailsbyteeha
14
Juyawa Hadiza tayi jin atmosphere na gidan has become so unbearable for her tawuce dakinta, gyale tadauko da wayanta tafito idanunta sunyi jazur kaman tayi wata daya tana kuka, kasa tasauka tadauki car key nata tawuce tabude kofa tafice ta shiga mota ko kallon gateman dinsu dake gaisheta batayiba tawuce ta tafi.

Gudu kawai take shararawa akan titi, tayi nisa sosai ta gangara gefen hanya tai parking  tadaga wayanta Anty Jamila takira tana bubbuga kirjinta dayake mata kaman an daura zuma rock akai, ringing biyu Anty Jamila tadaga duk karfin halin Hadiza kasa magana tayi, ita datagama cewa bazata kara kiran Anty Jams kan matsalolinta ba gashi yau tasake kira, kunya ma sai yasa takasa cewa komi kawai tahau kuka, shiruuuu Anty Jamila tayi tana jinta saikuma chan tace “gani nan cikin motan da mijinki yaturamin a airport za’a kawoni gidanki” dasauri Hadiza tace “eh”? Dan batagane tana hanyar zuwa gidan ta ba, dan jim Anty Jams tayi tace “mijinki dake bala’in sonki dakin kasa gani cus you’ve gone blind, dakanshi yakirani tareda Baban su Waleeda yarokeshi da cewa you need me right now nazo abuja, dakanshi yamin booking flight to and fro, yaturamin ticket ta WhatsApp, gobe zan koma kano dasafe, gani a mota, yanzu dai kina ina dan naji karan motoci”? Cikin kuka Hadiza tadago kanta bamatasan inda takeba hakan yasa tace “kizo shagona” katse wayan tayi Hadiza tasake tada mota taja kusan atare daga ita har jams sukakai shagonta, Babba ce Anty Jamila dan akalla zatakai 42yrs itace first born dinsu, Hadiza na ganin yayarta bata damu da suna plaza ba da gudu tai wajen kawai ta rungume Yayanta bakaramin tausayinta Anty Jamila tajiba, duktai zuru zuru, idanunta sun kumbure, fuskanta duk yakoma ja sabida kuka gashi yau kodan makeup da gayun data saba batayiba sabida damuwa, dagota Anty Jams tayi tace “ja gyalenki kirufe fuskanki muje ciki” yanda yayarta tafadi haka tayi suka shiga cikin babban shagonta staff din Hadiza na gaidasu Anty Jamila ce ta amsa suka wuce sama Hadiza tabude office nata suka shiga tana maida kofan tarufe sai kawai tayi wajen Anty Jamila data sami waje kan kujera tazauna.

Zama Hadiza tayi dirshan akasa takifa kanta akan cinyan Anty Jamila sai kawai tahau kuka. “Anty Jams na shiga uku, wlh na shiga uku na lalace, Nura ya cuceni, ya ci amanata ya yaudareni, Nura ya cuceni yakuma wulakantani” dudda yanda kanwar tata tabata tausayi but Hadiza needs to hear the bitter truth, da dan zafi Anty Jams tace “wlhy Hadiza kene kika cuci kanki, kika wulakanta kanki, kika yaudari kanki, u did all of this to yourself” Dasauri Hadiza takalli yayarta takai hannu tana share fuskanta tace “Anty Jams is it a crime kanada yar aiki? Laifi ne daukan yar aiki? Yarda danayi nakuma aminta da mijina cus zanma Nuri shaidan nan har ranan gobe kiyama shi ba dan iska bane kuma ba manemin mata bane, hasalima irin mazan nanne da mata basu damesu ba, Anty jams kiduba kiga this big shago i mange everything dakaina, am a business woman, an entrepreneur da aka san dani, I need to maintain level na integrity da face na business dina, niba housewife bace and I have kids so dole na dauko yar aiki dazata dinga managing mini gida da yarana, but shine Nuri zaibi bayana ya auremini yar aiki? Kinsan yanda nakeji azuciyana kuwa? Yar aiki ta fa? Yarinyar dana dauka tanamin bauta zai auro mini, Anty Jams jinake kaman na mutu kawai nahuta yafimin, naji na tsani kaina nagaji ma dakomi” takara kai hannunta ta share hawayen dasuka zubo mata saikuma takama bakin gyalenta tadaura kan idanunta, sosai Anty Jamila ke kallonta yanda Hadiza is looking this humble, ta zauna dabas akasa gabanta kaman mai daukan karatu tana kuka yasa saitaji kaman itama ta tayata kukan but dole ita ta daure, mikewa tayi zuwa table tadauko kwalin tissue tazo wajen tazaro daya ahankali takai kan fuskan Hadiza tashaga sharemata hawayen cikin fada irin ta manya tana goge mata fuskan tace “kinga abinda I’ve been telling you ko all this while but kikai kunnen uwar shegu dani, Hadiza kalli yau yanda kike kuka wiwi kaman bakeba, Allah yasa hakan yazama darasi agareki Hadiza, Allah kuma ya shiryeki ya ganar dake gaskiya yacire miki bakin akidan nan dakika dauka kika daurama kanki dayay landing naki in this situation, Hadiza ina ganin nafiki jin bakin ciki da Nura yakirani dakanshi dazun dasafe nida Baban Batool yana fadamana gashi gashi yayi aure, Ya aure Ummi and u don’t look okay plssss Baban Batool yabanni nazo naganki just for today gobe nakoma” Anty Jams taidan shiru tareda ijiye tissue daya gama jikewa tanunama Hadiza dake kallonta da jajayen idanu kirjinta tace “I was deeply hurt wlh danaji maganan but then again koda murya zan chanzawa Nura wanda zai nuna labarin baimin dadi ba nima nazama butulu kaman ki dan nasan kanwata ce caused everything and Nura has been annoyingly patient dake, cus hakurinshi ma at a point haushi yake bani yanda baitaba daddaura miki mari ba yafasa miki bakin dakikemai rashin kunya sannan yakado ki gida” Anty Jams tayi shiru tana kallon yanda Hadiza ke silent kuka tana shesheka tace “babu the most bitter punishment da zakama matarka irin ka auromata yar aikin ta, Hadiza yar aikin ki fa dababu abinda bata saniba dake faruwa agidanki ba, yarinyar dake zama cikin gidanki safe, rana , yamma, dare dakuma another safiya har na tsawon close to a year, rana daya mijinki ya aurota a matsayin kishiya Ya Allah! Allahumma Ajirni fi musabati!” Saikawai Hadiza tarushe da kuka Anty Jams ta girgizakai tace “I was deeply hurt but I couldn’t say a word sabida kin riga kin sani a position din dabazan ma iya bude baki nacema Nura haba Nura maisa zakawa Hadiza wannan sakkayan, but nakasa dan Hadiza ni kaina wani zubin idan kikai wani abun jinake kaman kada na sake kiranki har abada but then again bazan iyaba jini yariga yayi bounding dina dake for life, ni kenan balle kuma Nura dashine kikafi yima kashi aka, atleast ni kinadan shakka na kina ragamin, but still last time damukai magana cewa kikayi bazaki kara kirana ki gayamin matsalanki ba cus blaming naki

Mamana da Babana sun rasu na wahala a hannun mutumin nan da Gwaggo tazo tarabamu dashi, yana zuwa gida yadakeni nida Gwaggo ina kwance ina rashin lafiya kullum jinake Allah yakawo wani rayuwana wanda zai soni, ya killace ni daga hannun mugun nan, ya adana ni yanda Babana zaiyi idan yana raye cus babana yana sona" tasake rushewa da kuka tace "Allah yasani ban aureka danna cutarda Anty ba, inason Anty inason yaran data haifa, kawai zuciyata ta aminta dakai, sabida kanada hankali, ka darajani ka girmamani, gaka babba nasan idan ina taredakai ina tareda kwanciyan hankali, inaso nazama matarka ina zaune karkashinka, da abin yafaru sainaji kaman banda rabo aduniya kaima baka sona shikenan banda kowa" awwwn Nura jiyayi idanunshi sun cika da ruwa da sauri ya tsayar dasu yadago fuskanta yace "Ummi ina sonki sosai bazan taba wulakanta ki ba wlh, badan na wulakanta ni na aureki ba, zuciyana nada fadin dazata iyaso Mata hudu, lokacin hankalina atashe yake kuma I see you kinada understanding ban dauka zaki fushi ba saisa nai haka Ummi, but na gane kuskurena tun alokacin ma da Hajiya ta sanar dani, Ummi mata na miji na samun sabani but communication shine ke warware sabani, kome zan miki kada kiyi zuciya ki banni ki sameni ki gayamin mu tattauna akai kinji" gyadamai kai tayi saikuma gently tai kneeling agabanshi ahankali tace "kayafemin kuskuren dana maka na zuciya da rashin fahimtarka danayi Baban Aman, bazan karaba dagayau" tsayawa yayi yana kallonta the way she's kneeling saikawai yaji this is what you call a wife! Da sauri yaduka ya dagota yace "nayafe miki, nima kin yafemin, i hurt you my baby, nasaki kuka harda majina, kuma kinyi kuka sosai lokacin ko?" Gyadamai kai tayi kaman yar yarinyar tace "idanuna harda kumbura" dasauri Nura yakama kunnenshi yace "auuuchhh tuba Nura yake, an karbi tuban ko za'a bani punishment" dasauri tai murmushi tana cire hannunshi daga kunnenshi tace "nayafe ma Mijina kuma ina sonka sama da rayuwana Noor" murmushi yamata yajawota jikinshi ya rungumeta so tight, sun dade ahaka yace "I will be taking you on a date anjima da daddare, soyayyan dabamu samu munyi kafin muyi aure ba da kyau yanzu zamuyi agidan Hajiya, jibi zan koma Abuja zan barku nan zanje duba gidan mu upper week kotasaman zamu koma gabaki daya, yanzu jeki shirya zan kaiki for shopping na kaya dan anjima da night gayu nakeso kici sosai, zakije shopping"? Gyadamai kai tayi dasauri, yace "yauwa, daganan zan kaiki Bank kibude account akwai wasu kudade danamiki kyautan su a hannuna" yadagota yana share mata fuska yace "jeki shirya gani nan zuwa nima, I love you" ya mata peck akunyace tawuce tafita ranta fesss saikuma ta juyo takalleshi suka hada ido tace "bayan mun dawo da daddare zan maka suprise wawatsula!" Wlh kalman saida yasa gaban Nura ya harba dasauri yakai hannunshi wajen yakama yana kallonta yace "zo kifadamin anan menene wawatsula" dariya tayı tana make kafada tace "nizakama wayau ka danne nagaji bye mijin Ummi" tamai gwalo tareda bude kofa tafice da gudu Nura yayi dan dariya ya kalli abin yace "kaikuma kai hakuri mana ance anjima za'amana suprise wawatsula".🤣

Shopping yamata na ban mamaki, daganan sukaje bank abokinshi ne take yanke aka bude mata account ya zuba mata miliyan biyar dakuma 2m extra, 1M na ranan tazuge 1M na jiya, Ummi saida ta rungumeshi a bank tana realle bata taba ganin kudi hakaba haka suka dawo gida Hajiya sai dadi takeji ganinsu.

Bayan isha'i harda Hajiya da Meena aka shiga shirya Ummi that was going on a date da Nura, Hajiya takawo gold bangles nata tasama Ummi a hannu ta sanya wani red lafiyayyen gown Meena tamata makeup su kansu yaran sai cewa suke Anty Ummi kinyi kyau kiranta Nura yayi awaya hakan yasa Meena tace "tashi kije yana mota" kasa tashi tayi sabida Hajiya, Hajiya tai dariya tace "tashi ni kafin na kwadeki gulmamma" akunyace Ummi ta tashi tafito tana tafiya kaman hawainiya, Nura saukowa yayi daga jeep din Hajiya yafito yana kallonta kaman yau yafara ganinta, su Hajiya da girmanta sai leke suke ta window harda yaran fa kaga abu, wayanahi yaciro yace "wait lemme snap you dan kinyi kyau matan Nura" yana murmushi yamata hotuna sannan yasata amota ya maida yarufe suka wuce hannu Hajiya tadaga sama tace "Alhamdulillah Ya Allah ka dawwamar da farin ciki arayuwan su" Meena tace "amin".
Omoh jama'a love sweet wen money enter is sweeter cafe gabaki daya yayi booking Nura. Anyi arranging an zuba flowers suka shiga Ummi sai murmushi take bata taba ganin kalan abinba, abinci daban daban ake kawo musu da wanda ta iya ci da wanda bata iyaciba bayan sun gama aka bawa Nura speaker zaiyi karaoke ya karba yana kallon Ummi yace "yau zan miki wakan soyayya Ummi kin shirya"? Gyadamai kai tayi tana murmushi sai yatashi ahankali yadan tsaya nesa da table daidai ansa wakan but volume din is soo low ta yanda idan Nura zai bi muryanshi za'afi ji, yadan fara motsi da kafa in a very classic way yana bawa Ummi wani love look chan ya lumshe idanu kafin yabude su kadan ya nunata da yatsa yafara"
"Ina kewa, Ina kewar masoyiya, Ina kewa, Ina kewar aminiya, Abokiyar shawara, Ke ce kin dara, Kin san inba gake ba, Sai in hakura, Ki bani yar dama, A san da ni nima, Ki mini alfarma ki sanya ni a zuciya, Ki kauda yan gulma, Irinki ke nema, Suna ta shan fama, Sun zaga ko ina Mace ba aiba kece, A ido riba kece, Kuma kin san mundace, A kanki na zauce, Magana daya (ba shakka), Bude kanjin ka, Ta ya-ya zai dauka Samun ki baiwa ce, Bakya fushi, Ki murmushi, Dan sanki na shiga rai na
Ko ba ni in kinka tuna ni wannan shi ne muradi na, Nasan kina da buri
Kuma sannan kina da tsarin ki, Da zaki sa cikin ran ki nine zan zama angon ki, Farar tumfafiya ta daban cikin mata, A sanki nai rata a kanki na gane kaina! Kece naiwa alkawari, Mace daya kuma kin zarce dari, Kinzam min bangon sikari ko a ina kece, Sirrin ciki yazo fili, Kin iya ado da dan kwali, Mai kyan ido da sa kwalli, An iya maki zanen lallai, Tunda na sameki na huta
Saura sun ka kazanta
Bana iya kallon mata kiji kalmar da na furta
Akwai dadi abun da kakeso in ya so ka!…….
Ummi kawai sai kuka, staff suka bata tissue ta karba da sauri tana goge idanu tana kallon Nura she felt love, taji soyayyan shi in every part of tissue and born na jikinta, bata taba sanin Nura ya iya waka hakaba, kuma saiya mata wakan hausa wanda yasan shine ta iya takuma ke ji, tana cikin kukan taga hannu dasauri ta dago jajayen idanunta Nura ne, ahankali yace "zaki rawa dani yar matata?" Gyadamai kai tayi da sauri tana murmushin kuka tasa hannunta yadagata shima ya mike aka kunna wani soft wakan hausan cikeda so yace "no more kuka" gyadamai kai tayi daidai an fara wakan yabi wakan yana nuna fuskanta yace "Kyakwawar fuska na kalla ta deben kewa
Kuyi min san barka na samo fitilar 'yan mata" itama Ummi tana kallonshi daman ai ita oganniya ce awaka tace "Kyakwawar fuska na kalla ta deben kewa
Kuyi min san barka na samo dan auta na maza" Nura nadan tafiya kadan kadan da ita dan bai

iya rawa ba yace “Masoyiya” Ummi ta nunashi cikeda kware wa tace “masoyi na kai ne” yace “Aminiya,” tace “aboki na kai ne” yace “Ke zuciya” tanuna kirjinta kaman fa wata yar film tace “rabin raina kai ne” “Ke jijiya” tawani lumshe ido tace “jinin jikina”
Yace “Kin zama komai na, abun kallo madubi na” Ummi tana wani reverse baya tana wani adorable kwarkwasa tana nunashi tace “Kai ne tinanina a barci na da mafarki na” Nura na murmushi dan yanda tayi ya mugun birgeshi yace “ban bari ki cutu, Zan zama garkuwa, Komai yake zuwa, Gareki zana tare shi” Ummi tazo yakama hannunta sukai juyi juyi chan yacigaba yace “Adadi na ruwan sama wanda suke zuba, Adadin kifaye ma ba a san su ba, Adadin bishiyoyi baza su kirgu ba, Haka soyayyarki a rai ban santa ba, Koda za'a au'na ba sikele wanda zai dauka
Bata misaltuwa soyayya wace nake miki a zuciyata” Ummi tace “An san farkon rikici, ba a san karshen sa ba
Soyayya gamu ciki, baku san haduwar mu ba
Alkhairi ne a ciki, sam sam ba sharri ba,Karda ku ce, "Zaku raba, bazaka ku iya ba" yanda Ummi ke rawa sai kawai Nura yaciro kudi yana mata mani baitaba ganinta this happy ba, bakinshi yakai saitin kunnenta yace “kar rawan nan ya gajiyar min dake fa ban manta da wawatsulan nan ba”.

💫 MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE 3️⃣3️⃣

Magana ake ta kayan kwalam da makulashe😋 Kun gane kalan Kayan makulashe din kuwa? Toh bari kuji yau na kawo maki shahararriyar nan da aka sani da Crave and Indulge mai gullisuwan en gayu🌚 Indai magana ake ta gullisuwa, tuwon madara, tsami gaye, kwakumeti, Ridi, da halaka kobo,garin danwake da yaji! toh ba Irin ta a Nigeria. Zaku iya order ma kan ku, yaran ku, loved ones dinku har ma kuyi ma ‘yan uwa da abokan arziki souvenir😁 Ga tsafta ga dadi kuma✅ zaku iya tuntuban su a shafin su na instagrams @crave_n_indulge ko kuma ku musu magana ta WhatsApp https://wa.me/message/SAFXLSMA7TI6L1

33
Duk tafiya akayi yarage daga ita sai Mama afalon dake kallon yanda take kuka, kaman taje ta lallasheta but itama at this point she support Babanta 100 percent, yayi maganin Hadiza, ya gyarata, kuma she trust Baba Hadiza zata ladabtu, kuma zata bada nata gudunmawan ma agayarata, tashi tayi tawuce corridor dakin dake kusada nata tabude daganan tace “taho ki shiga dakinki kiyi wanka ki chanza kayan jikinki kiyi salla” ahankali Hadiza ta tashi ta taho sai kallon fuskan Mama take data hade giran sama da kasa so kawai take Mama ta lallasheta but Mama nosend hatta shige dakin dake da yar katifa yar daidai akasa dawata yar fanka asama

babu AC babu POP normal silin ne asama, sai akwatinan kayan ta kakap wanda Nura ya aiko dasu duk suna dakin nan aka ijiye, shiga ciki tayi Mama tasaki labulen ta wuce taje ya debo mata abinci da ruwa da kanta tazo ta kawo dakin, ganinta azaune yasa ta daka mata tsawa.
“My friend stand up kije kiyi wanka nace!” Kallon Mama Hadiza tayi saitaga kaman ba Mama dake nan nan da itaba, jiki asake ta tashi taje bayi tai wanka Mama na tsaye akanta ta shirya tai salla tasa taci abincin dole taci kusan rabin tuwon sanan tawuce tafita da plate din tadawo daki ta kwanta tayi shiru tana kallon fankan dake kadawa asama yana kara dake damun brain dinta sai kawai taji hawaye yafito daga idanunta saita tashi ta zauna ta zubama akwatinan ta ido tana kallonsu sai kawai taji hawaye yakara fito mata a fuzar da iska komi da Zeenah tamata na dawo mata fresh yanzu da gaske Nuri is done with her tunda har yana dawo da komi nata gida wani kuka yazo mata tayishi ta gode Allah tai bacci.
3 dot taji ana kiran sunanta. “Khadija Khadijah” Adan firgice tabude idanunta jin muryan Baba yana tsaye gaban dakin batare daya shigo cikiba yace “Khadija” dasauri tace “na’am Baba” strictly yace “dauro alwala kifito falo ina jiranki” ahankali tace “tom” tashi tayi tana tangadin bacci tashiga bandaki ta dauro alwala ta dauko hijabi tafito falo Baba kadai tagani ya tsareta da idanu dasauri tasauke kanta kasa dadduma biyu ya shimfida afalon daya agaba daya abaya yace “hau dadduma muyi qiyamun laili” Gyadama Baba kai tayi yatada salla yafara karanto Al qur’ani kira’an Baba dadi sai kawai Hadiza taji abun ya tsuma mata zuciya, yaune rana na farko dataji aranta lallai fa tabar Allah for a long time cus bazata iya tuna the last time ta karanta Al Qur’ani ba wlh, sai kawai taji hawaye ya gangaro mata feeling fragile, Baba bai wani ja sallan da tsayi ba sabida ita, 5 raka’a sukayi yajuyo ya kalleta anatse ya daga hannu yace “idan bawa na cikin kunci, damuwa da fitinun jarabawa, bawa dan uwansa bazai iya magance masa matsalolinsa ba Khadija, ni ko mahaifiyar ki bazamu iya magance miki duk abinda ke damunki ba Allah kadaine zai magance miki kome kikeji, shine Ubangiji mai tsarki da daukaka, mai kuma mulki, Al Awwalu, Al Akhiru Al Zahiru Al Badin kuma, duk daren duniya Allah kan sauko dakansa ya amsa bukatun bayinsa, dan haka daga hannunki sama ki gayama Allah bukatun ki kakap, sannan ki rokeshi gafara bisa laifuffukan dakikamai, ki rokeshi haske da dacewa akan rayuwa babu abinda yafi karfin Allah, so kaima Allah kukan ki Khadija” Gyadamai Baba kai Hadiza tayi kuka na zuwanmata ta hannunta sama ahankali abin namata kaman ba itaba she can’t remember the last time datai salla haka ta roki Allah for anything, she’s feeling guilty kan tayi neglecting bautama Allah, sai kawai tafashe da kuka tace “Allah na tuba! Allah na tuba!” Sai kuka hakan yasa ahankali Baba ya juya yayi facing gabanshi, Hadiza tai kuka zuciyanta ya sosu she’s feeling kaman ma she don’t deserve rahaman Allah cus tamai laifi da dama, da kyar ta iya controlling kukan tafara addu’a azuciyanta, the first abu daya fito daga zuciyanta is Nura tanson aurenta da Nura tanason ya maidata, tanason mijinta, kawai saita shiga share hawaye, sosai tai addu’a saitaji wani imani da natsuwa na shiganta da tadade bataji ba, anan bacci yayi gaba da ita ta kwanta kan dadduman Baba tajuyo yakalleta yayi shiru idan yace bai damu da damuwa ta ba yayi karya, saisa ya kudirci anniyan zai gyarata yana kuma rokon Allah ya taimakamai yabashi iko dan idan Allah bai nufeta da shirya ba kome zaiyi abanza bazata shiryu ba, addu’oi yacigaba dayı har aka kira asuba sannan yatadata yace “taje tayo alwala tai sallan asuba” shikuma yawuce mosque.

Hadiza tadauka Baba wasa yake yana dawowa daga sallan asuba wanda bai dadeba dan

normally sai gari yawaye yake dawowa gida but yau ana idar da salla yayi azkar yafito yadawo gida yakirata fitowa tayi ga mamaki ta ganin Baba tayi da bagadadi da gaske saikace yarinya shima Baba yasan duk tsiya ai ta iya alifun, ba'un, Al Qur'ani suka farayi from fathiha yana karantawa tana repeating after him, suna gamawa sukai alifun har karshe zuwa alifun bil fatha yana koya mata baki dalla dalla, daganan sukai tauhidi Man Rabbuka, Hadiza jitayi zatai kuka abu ya tsayamata awuya ganin yanda Baba ke koyarda ita abubuwan da yasan ta iya, ko su Aman dinta a islamiyyan su sun wuce abubuwan nan amman ya maidata yarinya, lekowa Mama tayi tagansu tadauke kai abinta takoma daki tana samin natsuwa ganin Baba yarike wuta.
7:30 suka gama Baba yace "tashi kije ki daura abincin kari kiyi gyaran gida, tambayo Mamanki me za'a dafa" gyadama Baba kai tayi tawuce ciki ahankali tace "Mama ina kwana" batare da Mama ta kalleta ba tace "lafiya lau" murya chan kasa tace "me za'a dafa Mama?" Dan kallonta Mama tayi tace "ki surfa wake rabin tiya, saiki debi kadan ayi kosai, ki dama kamu asha dashi, ragowan kiyi alalen rana na gwangwani, injin nikanmu na backyard banason alalen nikan blender, buhun gawayi na kitchen ki hura wuta" ahankali Hadiza na kallon Mama kirjinta na bugawa tace "ba gas Mama"? Wani kallo Mama tamata tace "akwai amman jiya Baban ki yasayo gawayi buhu daya yace dashi za'a dinga girki yanzu" hawaye Hadiza taji sunciko idanunta tarikesu dasauri tace "Mama ban iya hura gawayi ba, shima wake ban iya surfaw……" dakuwan da Mama tamata yasa takasa karasa maganan, Mama da haushinta ke cikinta fall sabida yanda takaso auren gidan arziki yaro mai kudi tadawo mata gida tawani zabura tace "wlh kikkipa miki mari zanyi Hadiza kinci kaniyanki, are you stupid dazaki cemin baki iya surfen wake ko iya hura gwayi ba kin dauka nan Abuja ne? Dan mai garinku kafin kiyi aure ba da itace kuke girki agidan nan ba lokacin akwai gas ne? Sau nawa kika dafa alale agidan nan ki surfa waken kiyi komi? Hadiza kalleni nan wake up! Ki gaggauta tashi daga baccin dakike ubanki ba kowa bane haka ma ni uwarki, Babanki Malamin makaranta ne nikuma housewife ahaka muka raineku kuka taso, auren Nura shine ya jiyardake dadin rayuwa kikadan menene rayuwa adukiya, yanzu kuma kin kaso auren gidan ubanki kike look at everywhere" Mama ta nuna dakin da yatsu tace "bude idanunki da kyau ki kalla nan ba gidan Nura bane gidan mahaifinki ne Hadiza, ki gane banbancin so my dear bace min daga nan kije ki daura abincin safe" tashi Hadiza tayi ahankali tawuce tafito idanunta har zafi zafi suke mata tsabagen rashin jin dadin rayuwanta, tsakar gidan tafito zuwa kitchen dinsu ta tasaya tana kallon komi ga buhun gawayi ga murhun gawayin, ga tukwane, yanzu itane zatai aiki a kitchen din nan? Tasan tayi aiki aciki da but ta manta? She's not use to old life nata again, ijiyan zuciya tasauke tasa hannunta tadauki kaskon wutan ta ijiye waje daya, tabude buhun gawayin, tadaga fararen soft hannunta dakeshan manicure ta kalla, kuka tafashe da shi ahankali tace "na shiga uku na lalace" goge fuskanta tayi da sauri kafin ahankali tasa hannun cikin buhun ta debo gawayin ta zuba a murhun, ledojin datagani da kyallen dinki na hada kasko tadeba ta zuba tana mamakin yanda take tuna yanda ake hura wutan yanzu, bataga kalanzir ba saitadau ashana ta kunna akai makamashin suka kama hakan yasa tafito tawuce flat nasu ta auno wake 8 cup tafito tadeba ruwa ta jika tadauki turmi ta bude tadauki tabarya ta kwashe wajen ta zuba tafara daka ahankali kirjinta namata badadi ko kadan.

Kafin kaceme hannunta sun sassage from surfen sakin tabaryan tayi ta zauna akasan simentin

wajen jitake kaman zata sume ta jinginar da kanta a bango tana maida ijiyan zuciya tana yarfe hannunta, hayaki taga yana fitowa sosai daga kitchen din hakan yasa ta dafa bango da kyar ta mike tsaye ta wuce kitchen din, makamashin sun cinye gawayin bai kama ba sai hayaki suke, tari tafara sosai tafito daga kitchen din tawuce takoma daki tasami Mama afalo tana waya tace "Mama charcoal din yaki kamawa" batare da Mama tai magana ba dan waya take ta rarumi throw pillow kan kujera zata jefa mata da sauri Hadiza tafice takoma kitchen din ranta ba dadi. Mafici tadauka tashiga hurawa but still yaki kamawa fitowa tayi tawuce daki wajen Mama again data bita da kallo ganin tai buzu buzu duk toka toka akanta,  ahankali Hadiza ganin Mama tagama wayan tace "Mama yaki kamawa wlh nayi nayi, gawayin baida kyau zoki duba dan Allah" wani matsiyacin kallo Mama tamata tace "Baban ki ya shigo gidan nan baki gama ba wlh zaki gamu dashi" juyawa Hadiza tayi takoma kitchen ta duka tasake deban makamashi tasa yagamaci still yaki kamawa kawai saita fashe da kuka she's so fuatrated kaman taita zuba ihu takeji da kyar akaro na uku yakama tadaura tukunyan ruwa tafito tazo ta kwashe waken data surfa daga turmi taje gaban pampo tazo ta wanke da su attarugu da albasa taje chan backyard ta tsaya tana kallon injin din da ake mishi tadawan generator.
She used the injin before dan su basakai nika waje but yanzu batasan tayaya zatayi ba, ijiye bowl na surfen waken tayi tazo gaban injin din ta tattaba, sannan takama handle na igiyan ijiyan zuciya tasauke sau uku na gathering strength kafin ta fuza da karfinta wani tangal tangal tayi zata fadi ta dafe bango injin din yayi kuka. "Tutututututututuuuuuuu" ya mutu bai kunnu ba, sake zuwa Hadiza tayi tasake fizgan igiyan wanan karan saida ta fadi duwawunta ya bugi kasa tace "wayyooo Allah na" lekowa wajen Mama tayi ganinta akasa tsaki taja kafin taje tajima kanta ciwo bari ta tayata tada injin din just for today, ja daya Mama tayi injin din yatashi takalli Hadiza tace "tashi ki wanke injin din kiyi nikan" da kyar Hadiza ta tashi Mama tawuce kitchen din dan ganin haukan datake, ganin ta hura wutan harma ruwan na shirin tafasa yasa tai murmushi tawuce takoma daki.
Da kyar tayi nikan ta kashe injin din takoma cikin gida, tana zuwa ruwan ya tafasa ta dama kamu tadaura mai awuta ta debi kullin kosai tana bugawa sai zufa take tasa gishiri da magi guda da albasa data yayyanka albasan shima saida yasata kuka sabida yaji, wlh zaku iya mata kuka kuka ganta a kitchen din nan, hannunta duk bakin gawayi harda fuska nan, tasoya kosen ta kwashe akula tafito daidai Baba da Baffa Amadu na shigowa har ranshi Baba yaji dadin yanda she manage tai girkin dan bai zacima zata iyaba that means yanada hope zata gyaru duk fitowa sukayi zasuyi kari zata tashi takoma kitchen Baba yace "ina zaki"? Ahankali tace "zanje nasa alalen a wuta ne" wuri ya nuna mata yace "zauna kiyi karin kumalo kema" zama tayi duk sukai kari ba laifi kosan yayi dadi wlh sosai, tafa iya girki dama kawai iskanci ne ke hanata yi, tass aka cinye ta kwashe komi tafito dashi takai pampo taje kitchen ta dauki buhun gwangwani tabude takai makawarara ta wanko tazo tahada tasa alalen ta zuzzuba a gwangwani ta jera a pot tasa a wuta sannan takoma tai wanke wanke tashiga share tsakar gidan tana gamawa tashigo falon su ta gyara har zuwa dakinta sai nishi take kaman mai asma, komawa kitchen tayi alalen ya nuna tadaura ruwan zafi dazatai wanka dan babu water heather agidan nan, ruwan na tafasa tajuye a bucket ta sirka ta tafi bayinta tadade aciki dan gashi tama jikinta lafiyayye tagaji, tafito tayi shafe shafenta tayi face routine nata ganin har tasoma samin wrinkles from this work datayi tasa kaya ta kwanta agado tana nishi barci kawai takeso tayi, harta runtse idanunta zatai bacci Mama ta kwala mata kira dasauri tabude idanunta  daidai Mama na daga labulen dakin ta

kalleta hannunta rikeda kayan wanki ta zudda akasa tace “kin wanke bayinka gidan”? Girgiza matakai Hadiza tayi Mama tace “ga kayan nan ki hada da naki da kika cire jiya dan ba’a tara wanki agidan nan kije ki wanke kiyi amfani da ruwan kumfan ki wanke bayukan gidan” duk yanda Hadiza taso tadaure saita kasa danta gaji ainun, fashewa tayyi da kuka tace “Mama harda ke baki sona ko yanzu? Mama kasheni zakuyi da aiki? Wlh bayana ciwo, hannuna har bororo yayi sabida surfen danayi kalli” tanunama Mama hannunta dahar yayi ja yayi bororo tace “Mama nagaji, Mama wlh nagaji” dudda ta bala’in bawa Mama tausayi amman ta daure tace “Dan girkin dakikayi na bakinmu kadai bawai girkin tukunya lamba goma ba, da dan sharan tsakar gida da wanke wanke da gyaran falon nan dakikayi shine kika gaji? Bayanki na ciwo? Surfen wake gwangwani takwas bama tiya daya ba shine hannunki har yayi bororo? Lallai Hadiza kin sami duniya, kinsan akwai matan da kullum aduniya sai sun surfa kayan hantsi buhu buhu sabida su sami abin ciyar da bakinsu abinci? Kinsan matan dake zuwa aikatun suna share big big organizations din nan irinsu bank da hospital sannan su wanke bayukan suyi komi sabida su sami kudin ciyarda kansu da iyalansu? Hadiza kinsan menene rayuwa kuwa? Sabida kin dandana dadi? Hadiza kinsan the amount of work people are doing in this life just to survive? Kinsan akwai wayanda yasan kashin damukeyi ne aikinsu? Kinsan akwai wayanda gyaran kwatane aikinsu? Kinsan akwai yan aikin kwadago? Kika har sunyi doro tsabagen aiki? You are complaining sabida kin share falo, kin dafa abinci? To ba ciwo baya ba, ke bayan ya karye ma kinji, tashi ki karasa aikin ki, jeki wanka bayikan gidan nan ki hada kayan nan ki wanke su tass you lazy girl, u might be 33 but mu muka haifeki you must work this work, da kinsan bakison aikin dabaki kaso auren ki kin dawo mana gida ba, da baku nan aini ke komi dakaina da tsufana banda yar aiki, yanzu ko kin kaso aure kin dawo gida ai Alhamdulillah nima nahuta, you don’t expect me to be entering kitchen gaki agida, kezaki komi Hadiza yanzu kika fara, bayan ya tsinke ma inyaga dama you will get use to it,  tashi kona kira Babanki wlh ai yana wajennan” tashi Hadiza tayi kawai tafashe da kuka tace “na shiga uku” Mama tace “tukunna saikin yabawa aya zakinta Hadiza don’t think punishment ne wannan this is normal aikin gidan Babanki which You MUST DO” cikin kuka sosai Hadiza tace “Mama to nayi order washing machine da generator? Na yarda zan dinga wankin a washing machine, koba wuta saimu tada gen, Mama ni gas dinma zan iya sayo wani daban tunda bakuso ina girki da naku, please Mama dan Allah Mama basai Baba yasani ba kurufamin asiri Mama ki yarda wlh zanyi order yanzu nabiya kudi akawo” wani kallo Mama tamata ganin har yanzu da sauranta Mama tace “Hadiza dagani har Babanki are not interested in your money, kudinki is useless agidan nan, abinda Allah ya hore ma Babanki yasaya dashi zamuyi amfani, shikuma zamuci dan haka ko amarfi don’t even dream of zaki sayo wani abu ki kawo cikin gidan nan, karki bari nadawo nasameki zaune  adakin nan”.

Kuna ganin idan Baba da Mama suka gyara mana Khadijatul Kubrah bazatama Ummi fincikau ba kuwa🤣

Tundaga Alifun Ba’un fa aka fara mata.

Akwai wani magana da manya keyi na cewa no matter inda kasami kanka arayuwa  always remember where you are from 💔

💫MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE3️⃣4️⃣

Lokacin sabunta BUDURCI yayi…Lokacin sake HONEYMOON yayi…Lokacin dawo da martabar SOYAYYARKI da maigida yayi Shi lokacin AMARCI yafi ko wani lokaci dadi a rayuwar aure…shiyasa yau NASARA NERA ke gabatar muku da SABON package dinmu wato VIRGIN AGAIN VIRGIN AGAIN package ne na musamman ga duk wacce kaddara ta gifta ta rasa BUDIRCINTA Wannan package ya k'unshi 🔥Powder 🔥Steaming herbs 🔥Gel 🔥liquid Me kike jira??? idan ma aure zai k'ara kina da damar kasancewa daidai da amarya, idan kuma haihuwa kikayi zaki iya daidaita kanki kafin resumption, in kuma bazawara ce kin samu damar tashin kan ango🔥🔥 Me kuke jira??? Virgin Again wato sabon budurci munyi shi ne don min matan aure dage fama da matse war gaba ,kaman matan da suka haihu,ko kuma matan da Allah ya hada da kaddarar fyade. Bayan matsi da ya keyi yana maganin Infection.
07064487800
https://chat.whatsapp.com/lPh3BxlWPT6D9QsS49DkfB
Our FLAT TUMMY PACKAGE is made with ingredients such as honey, sip and lipton and results is achieved within a maximum of 50days …Yes its no magic, not 5days …50days of FLAT TUMMY JOURNEY….would you like to join the flast tummy gang?

Send us a DM NOW!!!

34
Bayan Wata Daya.

Tafiya tai tafiya rayuwa taja, tunda Hadiza tazo gidan Baba wannan routine din nan Baba yake bitamata kullum yaumin, babu randa bazasuyi karatu ba, kowani abu kotanaso kobataso bata isa tace bazataci ba, zaman gidansu yasa taga life from a different angle cus Baba technically shows her kudinta is trash a inda yake dan bai mata amfanin komiba, at the same time itama tai regretting so many things, cus zata iya cewa business dinta da jikinta dasu Amali kawai take kashema kudin, chanza mota, siyoma yaranta designers outfit na yara she neglected gidansu, bawai sabida rowa tai neglecting ba but sabida taga Nuri namusu komi, sai yanzu data shigo gidan tai zaman gidan saitakeji inama ita ta buge gidan gabaki daya an chanza gini, ta zuba air conditions da sauransu dudda tasan ba lallai Baba ya yarda ba, then she remembered ko kafin Baba ya yarda da motan da Nuri yasayomai saida aka kai ruwa rana but dudda haka maybe da Baba yafi zama comfortable da cin kudinta than na mijinta and funny enough ko Mama or Baba

basu taba rokonta wani abubu, so taga rayuwa outside abinda tayi and she must say she has not been a good daughter to them wlh nor a good mom to yaranta, abubuwa alot made her to reflect back and ask kanta what is wrong with me?? Inata rayuwane all this while kaman tinkiya, infact I have no right to blame Ummi sabida yarana na sonta wlh wlh nine nasa suka sota sama dani mahaifiyarsu gashi yau wata daya kodan kewanta basuyiba balle suce akirata suyi magana da ita,abun yadameta matuka.
Ko kofar gida bataje ba tun bayan tashigo gidan nan ta iPad nata take monitor business nata da daddare dan bata samu ta zauna kota huta through out da rana, tunanin Nura da yaranta ya addabi zuciyanta takira Nura amman number shi baya shiga, WhatsApp taga yayi blocking nata, IG ma dan business page nashi na real estate business nashi a IG taje ta duba she can't find d page shima yayi blocking, batada any means na ganin yaranta, kowa na gidan ya tauysaya mata but tasasu in a position da kowa kunyan kiran Nura yake sabida abinda ta aikata, but bala'in tausayinta suke barinma ranan data basu labarin abinda Zeenah tamata inda Mama tace yamata daidai it serves her right amman fa sun tausaya mata kuma ba Mama kadaiba hatta Baba duk suna mata addu'a kan Allah yasa Nura ya komar da ita kafin tagama Idda dan Nura mutum ne da kowa zaiyi sha'awan auren shi da diyarsa, gashi tana masifan kewan yaranta, for the first time in her life saitaji tai nadaman yanda yan uwan mijinta da mahaifiyarsu bata shiru dasu da nan nan ko Meena saita kira zata samu tai waya da yaranta abin ya taba mata rai sosai, ta wajigu kuma tagane ta tafka shirme karatun da Baba ke kara mata yakara samata tsoron Allah da tsantsan nadama aranta kullum sallan darenta saitayi addu'a kan Nura yakomar da ita dakinta, aurenta da rufin asirinta dan duk business da kudi is all trash idan ba namiji.

Yauma kaman kullum ta tashi tayi duka abubuwan datakeyi ta daura ruwa awuta taji da kanta da cikinta na ciwo wanda tun jiya da daddare taji hakan amman datai bacci ta tashi bata karaji ba sai kuma yanzu datake kitchen din nan.

Iza ruwan tayi tamike tsaye ahankali saitaji maranta ya rike sosai mamaki tayi period zatayi ne to ko shine ai bata ciwon mara haka, daurewa tayi tana dafa bango ta lallaba tafito daga kitchen din tana fitowa kaman ance oya kara tafiya mugani kawai kafanta ya rike tana ganin jiri d next thing kawai ta zube awajen daidai Baba da Amadu na shigowa gidan tana landing akasa akan idanunsu, Baba yace "Subhanallahi Khadija" da gudu yayi wajen ya tallabo kanta tana bude idanunta kadan kadan tana kallon su, Baba Amadu ne yafara ganin jinin dakebin kafanta dasauri yace "Yaya kalli" dasauri Baba yakalli kafanta yace "Subhanallahi, je tada mota" daidai Mama nafitowa jin hayaniya ganin Hadiza zube akasa ga jini a kafanta yasa dagudu tazo wajen hankalinta tashe abinku da uwa Baba yace "Hadiza nada ciki ne?" Arude Mama tace "ciki?! Ciki kuma, Wlh bantaba sani ba, ko miyar bata taba tofarwa ba, balle zazzabi ko amai, banganta ma da alaman mai ciki ba kwata kwata, bari na dauko hijabi" wucewa tayi aguje ta dauko hijabi akasa Hadiza amota Amadu yarufo gidan sai asibiti wani madaidaicin private asibiti Baba yakaita daidai kudinshi ba irin na yan gayun nan ba, karbanta akayi akai ciki chan Dr yafito ya nuna Amadu yace "kaine mijinta"? Dasauri ya kalli Baba yace "a'a lafiya meya faru"? Dasauri yace "ina mijinta yake?" Anatse Baba yace "likita meya sami diyata nine mahaifinta? Meya faru take bleeding"? Cikeda damuwa likita yace "Baba ko'ina mijinta yake just call him yazo maza

maza, bari nakoma ciki, ya iso kwaji ko menene" yawuce yakoma ciki, Mama  da hankalinta inyay dubu yatashi tace "kira Nuran Malam, Allah ubangiji yasa yana kano" dan Jim Baba yayi saiya wuce yafita waje yaciro number Nura yayi dialing.
Cikin wani bacci mai shegen dadi sun gama watsewansu da Ummi yaji wayanshi na ringing hakan yasa da kyar ya iya yabude idanunshi, jaye Ummi yayi daga jikinshi ahankali yasa hannunshi yadauki wayan ganin Father Inlaw saida yayi dan jim har wayan ya katse bai dauka ba sannan yayi dialing number back cikeda girmamawa yace "Assalamu Alaykum Baba" dan ijiyan zuciya Baba yasauke yace "Nura ya gaji?" Ahankali Nura yace "Alhamdulillah Baba" anatse Baba yace "gamu a asibitin sangu yanzun nan muka shigo, kawai Hadiza ta sume gaban kitchen saiga jini ya balle mata" dasauri Nura ya yunkura ya tashi daga bakin gadon dayake zaune, anatse Baba yace "sunki gayamana komi Likita yace lallai lallai saina kira mijinta, ana nemanka saisa nakiraka dudda nasan kana Abuja maybe saina yasaka da Likitan awaya ko"?
Anatse Nura yace "ina kano Baba gani nan zuwa" ahankali Baba yasauke ijiyan zuciya feeling calm jin yana kano yace "toh" ijiye wayan Nura yayi yakalli Ummi dake bacci dukowa yayi yaja bargo ya rufanata yana kallon kirjinta da kullum kara girma suke yarasa dalili maybe dan yana matsasu ne oho yawuce bayi wanka yayi yafito ya shirya cikin wata farra yadi mai kyau yana cikin fesa turare Ummi tabude idanu kallonta yayi yace "kin tashi baby girl"? Gyadamai kai tayi ahankali saka agogo yayi yazo bakin gadon ya duko ya manna mata kiss agoshi cikeda so yace "zan fita me zan kawo miki idan zan dawo"? Murmushi tamai tace "babu abinda yakaika dadi ni kadawo da wuri kada in kewanka, me zakaci na dafa maka?" Murmushi yayi cikeda so yace "yau nama nakeso naci but bansan ko Hajiya nada naman rago ba idan akwai kimin farfesu idan babu call me zan kira akawo" gyadamai kai tayi tace "saika dawo Allah karemin Baban Amali" "Ameen Maman Amali" yafadi yanajan hancinta ya mike tareda daukan wayanshi yafita dakin Hajiya yaje ya sanar da ita tace "imaxa kaje Allah yasa lafiya" ahankali yace "Ameen" yawuce tareda shiga mota yaja yasan hospital din hakan yasa yaje yayi parking ya sauka tareda wucewa ciki yana shiga yaga su Baba da Mama gaban wani daki hakan yasa yakara sa wajen cikeda girmamawa ya gaisa dasu akunyace yana kallon dakin daya hango Hadiza da likitoci akanta ta glass door din idanunta lumshe, tsayawa yayi yay jim yana kallonta, kusan 10min yayi awajen saiga likitan da nurses din sunfito ya kalli Nura yace "kaine mijinta"? Danjim kadan yayi kafin yace "yes" "come with me please" Dr yayi magana yana tafiya Nura yabi bayanshi zuwa office nashi suka zazzauna Dr yace "why was parent nata skeptical about calling you danake nemanka?" Dan shiru Nura yayi sai chan yace "bana tareda ita ne yanzu" kallonshi Dr yayi yace "dudda haka dai cus na tabbata cikin dake jikinta nakane" kallonshi Nura yayi dasauri, gyadamai kai Dr yayi yace "yes matan ka na dauke da cikin kimanin 2month da sati biyu but unfortunately……" yadanyi shiru kafin ahankali yace "yafita cikin tayi barinshi!" shiru Nura yayi kaman ruwa ya cinyeshi awajen, arayuwanshi yanason yara, shifa baiki yaga yanada 20kids ba wlh cus he just love kids, da kyar ya hadiye abinda yaji awuya har saida Dr yaga yanda Adam Apple dinshi yayi motsi, ahankali Nura yace "Dr are you sure Babyna yafita? Inace ba yanzun nan tafadi aka kawota ba kunyi scanning ne? Taya kuka tantance cikin yafita"? Yayi maganan cikeda damuwa, dan murmushi kadan Dr yayi ganin mutumin nada son yara from maganan shi dukya rude ya dimauce, dan ijiyan zuciya ya fuzar yace "that's even the reason yasa nace a nemoka inaso kayi signing this document, tana bukatan wankin ciki cus cikin ya

zuba but bai gama ficewa tatas ba" dasauri Nura yadagamai hannu yace "nooooo!" sai kawai ya mike tsaye dasauri jin yanada hope yace "just give me bill let's pay zan maidata hospital na Abokina" yayi maganan yana kiran Dr Tanimu instantly, ringing daya yadaga yace "kana hospital? Zan kawo Hadiza yanzun nan" kawai ya katse wayan duk Dr na kallonshi yajuya yafita nan da nan duk su Baba na kallonshi yabiya kudin komi yataho dakin da Hadizan take shida wasu nurses suka daurata kan wheelchair duk she's unconscious suka fito su Baba suka biyosu, wajen motanshi Nura yawuce dasu duk su Baba na kallonshi, da taimakonshi suka dagata daga kujeran sukasa abaya sai a lokacin yajuyo arude ya kallo Mama dake tsaye taredasu Baba yace "Mama zoki zauna da ita anan saisu Baba su biyomu" Toh Mama tafadi ta taho ta shiga su Baba suma suka shiga tasu sukabar asibitin, sosai Nura ke sharara gudu bini bini yana juyowa yana kallon Hadiza da Mama tadaura kanta kan lap dinta, nan da nan suka kai wani babban private hospital na masu kudi already Dr Tanimu ya shirya daki da komi aka karbi Hadiza kawai Nura yasami waje ya zauna yana bug buga kafanshi akasa looking so worried, he's just praying Dr Tanimu zai fito yagayamai nothing happens to babyshi yana cikin tommy Maman shi alive and health, Mama da Baba duk tana kallon Nura suke kusan yamafisu iyayenta damuwa har ranta Mama take addu'a Allah ya daidaita Nura da Hadiza dan Nura care about Hadiza alot, jibi yanda duk yadamu, kusan 20min Dr Tanimu yadauka adakin yafito dasauri Nura yatashi ganinshi yabi shi zuwa office kasa zama ma yayi yace "tell me babu abinda yasami baby na pls".

There this connection tsakanin Nura da Hadiza i don't know am i the only one seeing it ko kuma kuna gani???

Is this real love koko kawai affection ne as per anyi zaman tare da??

Hadiza Nura yakeso ko babyn shi dake cikinta???
💫 MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE3️⃣5️⃣

Wae har yanxu bakije shagon Habisma Underwears ba?
Kode bakya Maiduguri ne?
To shin kinje shafinta na Instagram ko TikTok?

To yaude ki leqa Instagram, base kinyi following dinta ba, kawae kije Kisha kallo, in akwae wani abinda kike buqata Baki gani bama kitambayeta, wasu abubuwan basa samun dama suyi

posting dinsu!

@habisma_underwears.
https://www.instagram.com/invites/contact/?i=11rv83nzhagn6&utm_content=i5wy1kf

***

Yau I need to get somethings off my chest.
So a lot of people nata zagina, (M Shakur baki da hankali, me Hadiza tamiki kodai sunan kishiyanki Hadiza ne, akwai wata Hadiza data taba offending naki ne, the hate you have for Hadiza is too much, this writer don't know what she's doing, this writer is selfish, she's bias, Haba abubuwa sunma Hadiza yawa bakida tausayine, wannan littafin baida ma'ana idan naji wasu zasu karanta ma zan hanasu, M Shakur I hate you) hmmm my people babu abinda ke bracket din nan da ba'a gayamin ba and more all because of this book MATAN KO MAZAN???

Now listen!
If you can't take this book kidena karantawa! Allah yasan ni banjinma family mu akwai me sunan Hadiza ba or wata Hadiza ta tabamin wani abuba, abubuwan nan dakuka gayamin all because I am trying to create awareness and still teach something on top of that kesa ake cema mata munada brain din KIFI!

Are you even blind to think this book is about kishiya??? My dear this book is about feminism, are you too blind to see abinda nakeyi in this book?? Book din danai involving full circle na zamantakewa Mata, Miji, and Familyn su da iyayensu!
Kun dauka inayin this book to downgrade first wife ko second wife ne?? Ask yourself Maisa nakawo Hajiya, Kannen Nura, Hadiza, Baba and yan uwan ta, Su Zeenah and co just ask kanki.

I write this book to tell you what feminism is! To tell you how feminism are affecting our homes! To show you the implications of feminism! Abinda feminism kesa ki loosing, and to show you the end result of feminism, banda haka to show you how yan uwa, friends and family suma suke taka rawan gani in everything.

I am hurt da all the insult but it's okay! Allah knows best!
Just remember one thing ko kina team Hadiza ko Ummi ko Nura your judgement doesn't influence my writeup sakon danakeso na isar saina isar da shi!

Idan bakiso ki karanta karkiyi as simple as that!

35

Shigowa office din Mama da Baba suma sukayi hankali adan tashe, cikeda damuwa jin har lokacin Dr Tanimu bai bashi amsa ba yace "tell me, did you save my baby"? Dr Tanimu na kallon Nura a natse ya girgizamai kai cike da damuwa ahankali Nura ya dafe kanshi tareda zama akan kujeran gaban table din dabas, Mama da Baba sukai salati, ahankali Dr na kallon Nura da har lokacin ya dafe kanshi yace "I am so sorry Nura, the thing is cikin yadan kwan biyu da lalacewa ajikinta kawaidai yau ne Allah ya kaddara zai fita, sorry Abokina, Allah yasa mai ceton kune" su

Baba suka amsa Ameen, Nura yadade ahaka shi mutum ne mai tsananin son yara, he loves children, he loves children, dafashi Baba yayi yace "ya isa Nura Allah sa mai ceton ku ne" gently Nura yadago kanshi idanunshi sunyi ja ya kalli Baba tareda gyadamai kai, Baba yace "saika fito" shida Mama suka wuce suka fita, da kyar ya iya signing amata wankin cikin, yaciro wayanshi ya sanar da Hajiya, ita Hajiya ko kadan bataji dadi ba dan tanason jinin danta kodako daga jikin waye zai fito kuma tasan yanda Nura keson yara yawanci yana yawan gayamata yanaso Hadiza takara haihuwa amman ita tanason spacing yara so she really felt bad itama addu'a tamai suka katse wayan.

Fitowa yayi daga office din da tuntuni Dr Tanimu yafito yabarshi shi kadai, wucewa yayi inda su Baba suke zazzaune a reception din, sai kuma yakasa zama yawuce hanyar dakin tiyata din dayagani an wuce da ita, yakasa tsaye yakasa zaune sai zagaye yake awajen, chan yaji ihun Hadiza wlh saida kanshi yasara dasauri yayi wajen dakin da aka shigar da ita wanda yake kusa da dakin tiyata room, wata Nurse yagani zata shiga ciki tace "Sir you are not allowed to be here" cikeda damuwa sosai Nura yana kallon kofan dakin yace "why is she screaming like that please? Ba amata alluran kashe zafi bane?" Ganin yanda yadamu Nurse din tace "Sir trust me ahankali ake mata nan da 10min angama baya daukan lokaci jeka zauna please" Gyadamata kai Nura yayi yawuce jin yakasa standing ihun sai kawai yawuce fuuu yafita.

Duk su Mama da Baba na kallonshi chan saiga Anty Jams tashigo asibitin hankali tashe tawuce wajensu Mama.

Nura na tsaye jingine da motanshi wayanshi yahau ringing daga wayan yayi ganin Baba ne yasa yamaida wayan aljihu yawuce ciki dasauri, Baba yagani yana kokarin fitowa yace "angama an fito da ita anma kaita dakinta idanunta biyu Alhamdulillah" Dan ijiyan zuciya Nura yasauke, suka wuce shida Baba ciki har zuwa dakinta, ahankali Baba yabude kofan Nura na biyeda shi abaya private room ne na mutum daya idanunshi kyur kan Hadiza da idanunta biyu sun kumbura sosai sunyi jaaa ga zufa agoshinta gashin idanunta sun tartare alamun tasha kuka tana kokarin kurban ruwan dumi da Anty Jams ke bata babu wanda yagaya mata Nura na asibitin but kawai kamshin turaren shi ne yadaki hancinta da sauri tajuyo da kanta ta kallo wajen kofan, hada idanu tayi da Nuran dake kallonta bayako kyafta idanu yana kokarin shigowa dakin biyeda Baba gabanta yawani kalan fadi ganinshi, dauke idanunshi yafara yi daga kallonta yatura kofan bayan yashigo ya rufe ya tsaya daga wajen Baba yakarasa gaban gadon ya kalli Hadiza dake kallon Nura takasa cire idanunta daga kanshi yace "sannu sannu kinji Khadija, yaya jikin?" Ahankali tace "Alhamdulillah Baba" Baba yace "meke miki ciwo yanzu"? Wajen maranta ta nuna tace "nan ne kawai amman kadan" hannunshi Baba yadaura awajen ya tofa mata addu'a yace "zai daina yanzun nan, bari naje nazo" yakalli Amadu kafin yakalli Nura yace "bari nadanje nazo Nura ai kana nan ko"? Gyadama Baba kai yayi, bawai Baba nada wajen zuwa bane kawai yanason yabasu space ne sun rasa dansu yanzun nan is only right suyi magana akai, Mama itama ta dauki nufin abinda Baba yayi ta kalli Jams tace "muje muhado mata shayin akawo wani riga ko Jamila" Anty Jams tace "to Mama" suka wuce suka fice dakin

yarage daga Nura sai Hadiza dake kallonshi kaman yau tafara ganinshi yakara mata wani irin kyau a ido kaman tai shekara bata ganshi ba haka takeji, fatanshi yakara haske yanda kasan wani balarabe, she feels kaman yazo ya rungumeta and just talk to her kotaji dadi, bata tabajin ciwon rasa abu kaman yanda taji na cikin nan ba, da kyar cikin muryan mara lafiya dake a bala'in kwance sounding so weak tace “ina yini Baban Amali” dan kallonta Nura yayi kaman bazai karasa gaban gadonba saikuma yadaga kafa atsanake yakarasa gaban gadon ya tsaya tareda folding hannunshi a kirji yana kallonta kaman yanda take kallonshi heart dinta na racing kinship very close to her duka kamshin turarenshi na shiga hancinta, asanyaye akuma taushashe yace “are you having any pains?” Har cikin jijiyoyin dake zuciyanta taji tambayan dayasa zuciyanta yayi wani irin melting, girgizamai kai tayi ahankali, duk yanda take kokarin danne hawayen yakasa, she just wanna cry and cry and cry for him, she just wants to cry for her Nuri, hawaye ne masu bala'in dumi suka zubo daga idanunta takai hannunta da sauri tashare cikin wani kalan sanyin murya tace “I have no idea wlh inada ciki Nuri, nida from day one na sami ciki nake laulayi, but this is different banji komi ba, I lost our Baby Nuri, wlh koda wasa bansan inada ciki ba, I lost my baby, it's hurts” tafashe da kuka sosai mai tsuma rai, he knows Hadiza so well she hardly tell lies, hakan yasa tana fadin batasan tanada ciki ba ya yarda without a doubt, cikin kuka sosai taga an miko mata handky hakan yasa tadago rinannun idanunta ta kalleshi hada idanu sukayi takasa tantance exact reaction dake kan fuskanshi but she's happy yayi offering handkerchief nashi for her, hakan yasa tasa hannun ta ahankali tana kallon fuskanshi kaman bata taba ganinshi ba ta karba asanyaye tace “thank you” kai handkerchief din tayi kan fuskanta kamshin Nuri da warmth dake jikin handky din na jikinshi saitaji yakara tsumata tafashe da kuka sosai wanda yamafi nada, why will she make this coolest Man to hate her harya rabu da ita? Why did she pushed him to the wall, dan lumshe idanu Nura yayi yabude su ya daura akanta ahankali yace “stop crying please haka Allah ya kaddara, Allah yasa mai ceton mune, stop crying okay” yafada warming kaman yana lallashinta gyadamai kai Hadiza tayi ahankali tana goge fuskanta kukan yaki tsayamata she just wanna hug him, ahankali yace “bari naje naga Dr Tanimu” gyadamai kai tayi yajuya da sauri zai fice haryakai kofa tace “Nuri!” Tsayawa chak yayi batare daya juyoba dan lumshe idanu yayi ahankali yace “Nura dai” tsinkewa Hadiza taji zuciyanta yayi cikin murya dake dauke da tsananin shaukin so tace “I love you Nuri! I still very much do, I can never ever love anyone like you, Nuri forgiv…..” dasauri Nura yabude kofan yafice batare daya gamajin maganan ta ba Hadiza tafashe dawani kalan kuka kaman ranta zai fita.

Office na Dr Tanimu yawuce, zama yayi Dr Tanimu yakalleshi yace “sorry about your Baby Nura” gyadamai kai Nura yayi yay shiruuuu sai chan ya fuzarda iska yadago idanunshi da suka danyi jaa ya kalleshi yace “is something else wrong with her ne”? Dasauri Dr Tanimu yace “nope kaga wani abune”? Dan lumshe idanu Nura yayi  kaman baiso yayi magana sai chan ahankali yace “tayi duhu sosai, ta rame dik ta kode please kamata proper check up Dr Tanimu, she once had heart issue please kadubamin ita” ahankali Dr Tanimu yace “I think she's stressed ne, stress din nema yaja mata barin nan, but dudda haka zan mata proper checkup idan yaso gobe sai ayi discharging nata daman anjima nake shirin nai discharging nata” gyadamai kai Nura yayi sai chan ya tashi yace “thanks” yawuce yafita, dakin yakoma yaga Mama da Jams aciki ga Hadizan bacci ya kwasheta tarike handky daya bata gamgam, tana sauke ijiyan zuciya ahankali, sallama yama su Mama yace zaidawo gobe duk sukamai godiya yawuce yafita daga

dakin, daga Mama har Anty Jams babu wanda yaji dadin fitan cikin nan, hawaye Anty Jams ta share dataji ya zubomata da sauri Mama ta bubbuga kafadanta tace “is okay Allah yasan dalilin dayasa hakan tafaru, idan sunada rabon sakeyin zaman mata da miji zasuyi, so don’t worry and don’t loose hope dudda aure yakare tsakaninsu” gyadama Mama kai Anty Jams tayi takai duka hannayenta kan fuskanta ta share hawayen, tanason Nura da Hadiza dan dukansu sunason juna, but a yanzu Allah kadai yasan idan zasu cigaba da zamma taren, Hadiza tama Nura abinda take ganin kaman Nura yariga ya hakura da ita for good, Allah dai shine masanin komi.
***

Washe gari Nura da kanshi yasa Ummi ta shirya su Amali zai kaisu wajen Maman su, murmushi Ummi tayi tace “Anty tazo kano itama yayyy, Aman yau zakuje wajen Momy” tai maganan tana wasa da yaran tana shiryasu Nura yayi murmushi kawai yawuce ciki dan shiryawa, koda yafito yaga ta shirya yaran sunyi kyau sosai kaman zasuje wani event, tasama Amali hair band akai, hancin Ummin yasa yana murmushi yace “sannu da aiki Anty Ummi” murmushi tamai tana juya idanu tace “saikun dawo agaida Anty, bye Aman da Amali” yaran sukai waving nata “bye Anty Ummi”Nura yaduko tareda mata peck a goshi yace “I love you” akunyace tarufe fuskanta tace “ka gaida Anty” kumamunta ya shafa yace “kunyan gulma kinfi kowa…..” tashi tayi da gudu tawuce uwardaka yayi dariya tareda girgiza kai yawuce yafita daga dakin, sallama sukama Hajiya suka fito kaga yanda yake hira da yaran kai kanka you will wish ka sami Baba mai son yara haka.

Supermarket yakaisu yace “kuma Mommy ku shopping” yaran were so happy kowannen su ya debama Mummy abun da ransu keso, sukaje kanta yabiya kowanne ya karbi ledanshi na Amali yafi karfinta ya amsa yace “lazy Princesses” kaman zatai kuka tace “Dady I am stronger than owlett din pj mask fa ko Ya Aman”? Aman yace “yes Dady, nikuma I have lots of super power, Dady I can lift this car up” Dan zaro idanu Nura yayi yace “sannu special boy” Amali ta kwashe da dariya, Aman yace “Daddy kaga Amali ko Lazy princess kawai” wani tsalle Amali tayi zata fara halin dasauri Nura ya dauketa yace “yakuri Hajjaju, muje mu shiga mota” baya yabude ya ijiye Amali da kayansu shikuma su Aman first born adole babba ya shiga gaba yace “Dady I want to start driving nima” dasauri Nura yakalleshi duka duka fa Aman is just 4, kawai dai irin brilliant smart kiddo din nan ne sai kawai yayi dariya cikeda sonshi yace “okay Son zan koyama idan kakai 15yrs” tada motan yayi suka tafi sai hospital.

Kashe motan yayi yafito Aman yace “Dady this is a hospital is my Momy sick”? Gyadamusu kai yayi yace “but taji sauki,  muna zuwa zamu tafi mu kaita gida ma” gyadamai kai yaran sukayi ya rufe motan holding shopping din Amali suka wuce ciki sai kallon yaran ake dan Amali and Aman are so cute wlh kaman yaran larabawa, ga Ummi tamusu gayu, Aman kuma harda saka sun shade black na Rayban da Dadyn shi yasiyamai shi adole babba, dan baiso ana referring nashi as yaro.
Ahankali Nura yayi knocking tareda bude kofan dakin, Hadiza na zaune kan gado Mama na hada mata shayi zata sha aka bude bude kofan kawai taga yaranta sunci gayu kaman ba su ba, looking finer and healthier than yanda ta barsu, dawani kalan gudu suka taho barinma Amali

tace “Mommyyyyyyy” wani kalan tsalle Amali tayi Hadiza ta sauka daga gadon da sauri tadauketa sama Aman shima yazo yana cire glasses nashi, tsugunnawa Hadiza tayi tana kallonshi she can’t believe ita ta haifi this big handsome smart adorable boy, rungumeshi tayi sosai tana rike da Amal, kuka taji yazo mata but saita daure sabida su, bata taba tunanin Nura zai kawo mata su ba, she can’t even kwatanta excitement nata sai kawai tashiga mammanna musu kiss kaman zata hadiye su, Nura ya gaida Mama tabashi plastic chair ya zauna yana kallonsu kasa kasa.
Shafa fuskan Maman shi Aman yayi yana kallonta dan yaron akwai wayau he understand a lot of things batare da an fadamai ba yace “Mommy what’s wrong with you? You look so skinny and dark” dasauri Amali tace “yes Mommy, meke miki ciwo? Ya Aman mu mata addu’a kaman yanda Anty Ummi ke mana ko”? Dan murmushi kadan Hadiza tayi tace “Momy’s tummy hurts” kaman zasuyi kuka sukace “sorry Mommy” Amal ta shiga tofamata addu’a Mama tace “wannan tsohuwan yarinyar da wayau” dan murmushi kadan Nura yayi, saida tagama ma Mommy addu’a, Aman yabata ledan hannunshi yace “Mommy I got this for you get well soon” kallon Aman Hadiza tayi yanada wani kalan charismatic composure na Baban shi, she can’t believe yaronta ne Aman, Alhamdulillah! Hannu tasa ahankali ta amshi ledan zatai magana itama Amali ta sauka da gudu ta dauko nata ledan dake gaban Dady akasa ta dawo da gudu takawo mata tace “Mommy I got this for you, get well soooooon Mommyyyy naaaaa” Amali tai maganan like a little sweet girl, bude ledan Hadiza tayi trying so hard ta rike kukan datakeji, ledan Aman tafara budewa drinks ya kwaso mata cres, yasan Maman shi na yawanshan, da vita milk da cake loaf, da peanut da biscuits manya manya Oreos da chocolate cookies, tabude ledan Amali kuma su minti mai tsinke da cingum ne aledan dayawa exactly shopping din yara dai, sai kawai tafashe da kuka ta rungumesu Aman yace “stop crying Mom is the tummy still hurting Dady call Dr for Mom” girgiza musu kai tayi tace “am just so happy ne yarana sun kawomin tsaraba, yarana are all grown up kunyi kyau, and I miss u very well” Amali tace “Mommy give me one sweet” dariya Mama tayi Nura ma yayi murmushi kadan Mama tace “kin kawo tsaraba kuma kina roka, kanki kika sayomawa kenan su Amali manya” murmushi Hadiza tayi tadauki sweet tabata takalli Aman daketa kallonta shima yana lurada duk yanda Maman shi ta chanza kaman ba itaba tace “mekake so kai ma nabaka?” Ahankali yana kallonta da this affection na mother and son yace “chocolate Mommy” wani kalan son Aman Hadiza taji ya shiga ranta barinma dayace mommy, dauka Hadiza tayi tace “nabude maka?” Gyadamata kai yayi yana kallonta har lokacin, tabudemai ta bashi amsa yayi yace “thank you” vita milk daya kawo mata tadauka tabama Mama tace “Mama budemin nasha” dasauri Aman ya karba yace “Dady will open it, grandma batada hakori” yaje gaban Nura yabashi, ahankali Nura yasa hannu ya karba yakai bakinshi ya bude dan ba opener adakin yaba Aman, Hadiza ahankali tace “thank you Dadyn Aman” zama duk yaran sukai kan gado kusada ita Amali nashan sweet, Aman na cin chocholate, Hadiza na shan vita milk tana nan nan da yaran, ahankali Nura yamike yakalli Mama yace “bari naga Dr nazo” Mama tace “to” fita yayi yaci karo dasu Baba akofa suka gaisa nan da nan yayi clearing all the bill yakarbo magungunan da aka bata yabiya yayi signing discargw papers din yataho dakin yabama Mama magungunan ta yace “an sallamemu mutafi” Motan Nura Hadiza tashiga da yaran da suka zauna baya da ita sai surutu suke mata su Mama kuma suka shiga motan Baba, suka tafi gidansu Hadiza parking yayi duk aka shishiga gidan.

💫 MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE3️⃣6️⃣

Huuuuhuuuuuu agyara hanya  gafa MAMMI HAJIA tazo mana da kayan mata wey no be juju, ba jazz, ba abacadabara ko suddabaru aciki amma kuma aikinshi yafi yankan wuka, MAMMI HAJIA fa tariga tayi suna awannan harkan dan haka ku garzaya aguje kar ayi baku zaku iya shiga whatsapp group nata ta hanyar danna link din nan.

https://chat.whatsapp.com/L9xdTKd3MXZJRW8zkAMSqH

36
NOTE: akwai school of thought daban daban i read something daban daban kan idda. Ance bari terminate idda, at the same time some sunce sai cikin yazama mutum shine yake terminating idda Soo Allahu A'alam Allah masani, feel free to correct me or shed more light on the issue Allah ya ganarda mu gabaki daya Ameen.

Yadan jima kadan amota kafin ya sauko, Baba Amadu ne yakaishi wani special babban falo na Baba wanda yawanci littafai ne na addini suka cikashi ga blue rug ya rufe ko'ina akasan dakin, zama Nura yayi ahankali kanshi akasa ganin Baba shima akasan yayi filo da wata babban filo haka, shigowa Anty Jams dakin tayi takawo ruwa a tray da cincin da soyayyen naman kaza saikuma kunun aya mai sanyi tawuce tafita, Baba yakalli Nura yace "Bismillah Nura" cikeda girmamawa yadauki ruwa yabude ya tsayaya a cup yakai baki yasha kadan Baba yayi gyaran murya yace "Nura" ahankali Nura yadago kanshi yakalli Baba, Baba yace "dudda nasan kasani but still zan gayamaka dakaina miscarriage din da Hadiza tayi yabata iddan ta! Auren dake tsakaninku yakare!" Baba yayi shiru Nura yasauke kanshi kasa ahankali Baba yace "banbancin ku da wacce akama saki uku shine ita dole saitayi wani aure kafin tasake iya auren mijinta while a case dinku koda yanzu kakeson auren Hadiza sadaki kawai zaka biya a daura muku aure" Baba yayi shiru yana kallon Nura da kanshi ke kasa yace "don't get me wrong Nura, dakai da Hadiza duka yarana ne, sake aurenta ko rashin yin hakan bazai taba chanza matsayinka awajena ba and everything is your decision to make Nura kai d'ana ne, har yau har gobe har kuma jibi, sannan dagani har Amadu munsan abinda Hadiza ta aikata dan mu mazane dan haka live your life according to your rules and regulation Nura" gyadama Baba kai yayi ahankali nan Baba yakawo wani hira daban dan he don't wanna make him be uncomfortable idan yanason ya maida Hadiza dakanshi zai furta basai ancemai yafadi ba Nura ba yaro bane yasan har cikin ranshi abinda yakeso kenan amman kuma baida right na nuna hakan. Azahar sukeje sukayi suka dawo gidan Nura zai wuce Mama tace "ai baka isa ba saikaci abinci koma" ba yanda ya iya komawa yayi shinkafa akayi da stew kadan yaci shima dan kada suce yakici

sannan yatashi yama su Baba sallama, Mama tace “ka shigo ciki” shiga falon yayi Hadiza na zaune kan kujera tana sanye dawani doguwan rigan atamla red daya mata bala’in kyau hada idanu sukayi dasauri Nura yadauke kai yace “Allah kara sauki Hadiza” yakalli su Amali yace “let’s go kids” dasauri yaran sukai wajen shi suka kakkama hannunshi Aman na karban car key dake hannunshi, bawai basason maman su bane but wannan shakuwan dazaisa yaro yahau kuka shi zaibi Mamanshi ko zai zauna da Mamanshi daga Aman har Amali basu dashi, Amali da tayi but tazo tadaina dataga Mamanta no send her, hawaye Hadiza taji ya cicciko idanunta ahankali tace “Dadyn Amal bazaka barsu su kwana ba anan”? Still Nura yaki kallonta yace “maybe saidai gobe basuzo da kayaba” ga mamakinshi kaman ba Hadiza ba tace “Tom shikenan nagode Allah saka da alkhairi, nagode da komi da komi dakamin a asibiti Allah baka lada” dan dago kanshi Nura yayi just to assure kanshi Hadiza ne just agreed da maganan dayayi tashi daya hardamai godiya ganin itane dai yasa gently yace “u welcome” yama su Mama sallama suka fice su Baba suna rakasu har waje suka shiga mota Baba yadawo cikin gidan.
Da sauri Mama cikeda damuwa irin na mahaifiya tace “Malam ya nuna zai komarda ita?” Daga Baba har Amadu girgizama Mama Kai sukayi hakan yasa ahankali Mama tajuya takoma falo kawai ta sami waje ta zauna tai tagumi dasauri Anty Jams tazo kusada ita tace “Mama menene? Yace zai komar da ita”? Itama Hadizan dake zaune kan kujera tana kallon Mama jira kawai take taji ance yace zai kara aurenta dan Nura nada tausayi, shigowa dakin Baba yayi yakalli Hadizan data bishi da kallo tana zazzaro idanu kana iya ganin yanda gabanta ke faduwa zama Baba yayi ahankali kusada Mama ahankali yace “iddan ki yakare Hadiza!” Yadanyi shiru anatse yace “bazan hanaki yin kasuwancin ki ba amman dai ki kira wayanda zaki kira akwaso kayayyakin shagon adawo dasu kano kina karkashina bazan bari kına tafiye tafiye ko ki koma wani gari dazama ba, zaki iya samin wani shago anan kano akama ki cigaba da kasuwancin har zuwa lokacin da Allah yafito miki da wani mijin dan Nura kwata kwata baiyi maganan sake zama dakeba” yanda Hadiza ke kallon Baba wlh wlh zaka iya zubar mata da hawaye kanta ta nuna lips dinta narawa sosai tanaso tama foto da magana ne but takasa sai kawai tafashe da kuka wanda yafi na ko yaushe cikin kukan tace “Baba a ina zan taba samin miji kaman Nura aduniyan nan?” Cikin tsananin kuka tace “A ina zan taba samin miji kaman Nura aduniyan nan” cikin kuka sosai tana girgiza kai tace “bazan taba samun miji kaman Nura ba aduniya! A ina zan sami miji in this my age 33 dazan shiga as first wife, ko ya yarda zai aureni wani iyaye zasubar saurayin dansu ya auro bazawara mai yara biyu as first wife nashi? Mama Kozan sami miji is either me mata biyu ko uku, I can never get mijin dazamu shimfida foundation na rayuwan aure together like Nura” tayi maganan tana zubewa kasan dakin dumus akasa tana kuka, daga Baba har Mama data buga tagumi kallonta suke kaman TV, Anty Jams kuma kawai tasanya hannu ta rufe fuskanta tana kuka kasa kasa.
Hannuwanta biyu tadaura akanta tana wani kalan kuka tace “Anty Jams and Mama maisa dakuka ganni ina tsinannen akidan feminism din nan bakudau bulala kunmin shegen duka ba, ko kubani factory reset mari dazai dawo dani hayyacina ba, ko ki kira Baba ku fadamai? I was lost a lokacin all I needed was someone strict with irons hands that will put me in my place look at me today my life is messed up Baba yarana” tanuna kofa sannan takai hannunta tadaura saman cikinta tana kallon cikin tace “Baba yaran dana daukesu acikin cikin nan na haifosu duniya basuda emotional connection to me and is all my fault, look at them yanzun nan

babansu yana cewa su tafi babu ko musu, ai sunaso su zauna da Mommy basuyiba sun bishi sun tafi because basuda emotional bond dani what kind of a woman am I"? Tafashe da wani kalan kuka harda majina dayasa Mama tafashe da kukan datake rikewa acikinta sosai idanun Amadu ma sunyi jazur Hadiza tabashi tausayi Baba ne idanunshi kyam akanta cikin kuka tace "I used to believe yara damuwa ne! I used to believe providing abinda yara keso shine love not knowing spending quality time dasu, playing with them hugging them and kissing them is real love, my children never miss me but they miss Ummi sabida she's always with them, ta goyasu yarinyar nan ta goya Amali har nakan mata fada tana batamin yarinya da goyo har Aman Ummi goyawa take, I remember wata rana idan nadawo da wuri banson damuwansu nace ta kwashesu suje garden suyi ball that's how zata dinga wasa da yaran nan while I provide the ball and other accessories for playground dinsu Ummi is the one dake wasan dasu, Baba na cuci kaina dayawa" tafashe da kuka tace "Nura is my entire life, Nura yabani freedom, yabani opportunity, yabani luxury, yabani love, Baba bazan maka karyaba i know all abubuwan danama bawan Allah nan was wrong but Baba kasan mesa nayi hakan? Yau zan fadamaka gaskiyan daban taba gayama kowaba" Tayi dan shiru tace "Baba all abubuwan danama Nura nayi ne sabida nasan yana sona and he will always tolerate me ya hadiye kome namai, ina ganin cewa kalan son dayakemin bazai taba iya rabuwa dani ba, so I can match him, step on him however and whenever I want kuma bazaimin komiba, I feel I can use him to please my friends, the community and association din damuke ciki ashe hauka nayi Baba ko wayanda nake biyemawa su Zeena bahaka sukema mazajensu ba bakin ciki ne sunga yanda Nuri ke sona saisa sukaci nasaran rabani dashi, nama Hajiya all abubuwan nan babu ko darr araina sabida nasan yana sona, kuma na isa dashi, nabiyewa Zeenah nakaishi kotu sabida nasan yanasona he can not do anything, barinma yanda yasan nasami heart attack, Baba wlh wlh Nura baitabamin komiba, mutum neshi dakeson farinciki na da cigaba na, mutum ne daya tsani ina fushi koya ganni cikin damuwa, Nura can kill for me and die for me, kuna ganin zan taba samin selfless miji like Nura? Zan taba samin mijin da duk kudina bazai kalla ba he will still give me kudin salon, kudin kaya, kudin dinki kudin komi? Duk kudina bai taba cewa muyi sharing bill ba, duk kudina bai hanashi kara bani kyauta an ina zan sami kalan mijin nan"? Tayi maganan tana kuka tace "I tortured Nura, I pushed him har ya zamto gwara yadawo gidan by 1 nadare Ina bacci, Baba I took advantage of that man, took advantage of soyayyan dayakemin, Baba na zageshi is not a big deal for me sabida nasan bazai iyamin komiba yana sona, munafuki, algungumi, makiri, matsiyaci, mahaukaci, and so much more babu wanda ban kira Nura dashi ba Baba, Baba nashiga uku wlh nashigo uku Baba, nazo nakaishi kotu Zeenah ta kara da accusing nashi for molesting me, namai shairi na batamai suna i spoilt his record, Baba koni nasan after komi danayi ban chanchanci Nura ya maidani ba amman kuma wlh wlh bazan iya rayuwa babu shi ba, Baba kaga kashin jikina, bargo, jijiya, jini dakuma tsoka na jikina duka Nura sukeso hatta numfashin danake busawa nake shaka Nura yakeso, Baba tell me how can I live without him? Nura is the world best husband that knows how to pamper and spoils his woman but I ruined him, I fucked up, I messed him up and tarnish his image because of stupid feminism mentality na we are equal nidashi, Baba wlh wlh Baba zaku rasani har lahira idan Nura bai komardani ba, Baba tsoron alhaki bazaima barni nayi wani aure ba dan kowa zan aura nasan sai Allah yasa ya gallazamini azaba wacce tafi wanda nabawa Nuri na sau dubu, Baba kaji tausayina cikin nan was the hope na zai komardani cus Nuri loves children but shima yafita, kai kadaine mahaifina

hope dina Baba cus Nura najin maganan ka, yanajin kunyanka, kace ya aureni Baba, zuciyata zara tarwatse na rasa Nuri na, wayyooo Allah na ni Hadiza! Wayyyoo zuciyata na shiga uku, na bani, na lalace, na tagaiyare na ga ukuba, Baba dan kaunar dakakema Annabi Muhammadu SAW kasa Nura ya maidani" Tafashe da kuka majina shabe shabe for the first time Baba yasauke kai daga kallonta shima idanunshi sunyi jaaa but baiyi kukaba amman kowa na dakin harda Amadu tasa kuka.

Kuna ganin Baba yama Nura magana???

But then again! I feel bad and emotional for Hadiza, for ita da kanta ta zauna tai analysis na laifukanta haka dudda ance hali zanen dutse but ina ganin mu jira Muga new Hadiza ne ko Yaya??

Kuna ganin ta chanza ko a'a???
💫MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE3️⃣7️⃣

CHAPTER ONE IS COMING TO AN END😫 Labarin Nura da Hadiza yasoma karewa have you subscribe for chapter two?? Is just 1k, zamuyi magana akan Matan aure da Mazan aure masu biye biye, no judgement but I will teach you something you never knew about cheating and I will help you overcome it.
Kome kikeyi don't miss this chapter 2!!
Chat me up today and make payment.
wa.me/+2347012181461

37
Juyoda kanshi Baba yayi a tsanake ya kalleta dudda ta bashi tausayi but ya danne, yakalli Mama yanda take kuka da Anty Jams dama Amadu ya nuna Hadiza yace "duk sabida yarinyar nan kuke kuka?" Saikuma yayi shiru dan yanda Hadiza tafadi abubuwan datayi da bakinta sai zuciyan Baba yasake sosuwa ya nuna Hadiza up and down da hannu yace "kin dauka wannan borin da hayagagan nan dakikeyi shine zaisa nakira Nura namai magana?" Baba yadanyi murmushi mai ciwo yace "Hadiza yanzu haka ki fadi awajen nan ki mutu ni nasan cewa lokacin ki ne yayi bawai damuwan Nura ko wani abu bane yakasheki ba, cuta ba shine mutuwa, shi mutuwa lokaci ne kinsan mutane nawa har wankan gawa aka musu daga baya suka farfado why? Because lokacinsu baiyiba, idan lokacin mu yayi, ko yanzu, ko anjima, ko gobe, ko jibi ko gata, ko citta ko badin badadan zamu mutu Hadiza" yanuna kanshi da hannu yace "kin ganni

nan dattijon arziki ne sabida ke bazan zubar da kimata a idanun Nura ba, bazan taba mishi magana yakomar dake dakinki ba idan yanaso yayi yayi idan bayaso duka daya awajena abu daya zan fada miki ki kama Allah ki rike addu'a kuma, sannan ki nemi gafarar wayanda kuka kuntata mawa Allah yasa mudace tashi Amadu muje" tashi Adamu yayi suka fice Hadiza tai kuka tai kuka har saida Mama tai ihu tace "wai bazakima mutane shiru ba kashe kanki zakiyi da kuka, kima mutane shiru dalla" tashi Anty Jams tayi tawuce inda Hadiza take kama hannunta tayi tadagata tace "muje daki" da kyar Hadiza ta iya tabi Anty Jams daki.

Sunyi nisa sosai, Nura yana tuki yana kallon hanya ahankali Aman dake gefenshi yana kallonshi yace "Dady" dan juyowa Nura yayi yakalli yaron yace "yes Son menene?" Dan shiru Aman yayi sai chan yace "you don't want to make Mommy come back home with us"? Dan kallon yaron Nura yayi sometimes tambayoyin Aman nabashi mamaki kaman wani babba, dan shiru yayi baice komiba ahankali Aman yace "Dady is it because Momy na zaginka"? Dasauri Nura ya kalli yaron kafin yace wani abu Amal ta taso da gudu tana leko da kanta ta wajen takalli Aman tana zaro idanu kaman wacce zatai gulma cikin whispering but kana iyajinta sarai tace "Ya Aman Momy use to call Dady munafuki……." "Amal!" Nura yakira sunanta da tsawa saida yarinyar ta firgice tace "Dady sorryy ai bantaba fadi ba ko Ya Aman"? Gangarawa Nura yayi yay parking motan gefen hanya, yasan yaran sunsan suna fada but baitaba sani har zagin sun sani ba, dasauri yajuyo yakalli Amali daduk ta rude strictly yace "kika kara fadin something like this I will be very angry with you kinason Dadyn ki yayi fushi dake?" Girgiza mai kai tayi tafashe da kuka tace "Dady sorry" dan shiru yayi yana kallon yanda take kuka saikuma yace "come here" dasauri tazo hannunshi yasa ya share mata fuska yace "stop crying okay babu kyau yana suna saurarон fadan Momy and Dady is a bad habit" gyadamai kai tayi tace "sorry Dady" peck yamata a goshi yakalli Aman dake kallonshi yace "I dont want this discussion ever again am I clear"? Gyadamai kai yaron yayi yace "yes Dady" zaunar da Amali yayi, yatada motan tareda dan sauke ijiyan zuciya yawuce.

Ummi na zaune dakin Hajiya tana matsa mata kafa basu dade da dawowa daga kesson ba itada Meena taga yaran sun shigo da gudu abin ya bala'in bata mamaki da Nura yayi sallama yashigo falon sai mamakin ya idasa kasheta batasa ran ganinshi ba yau danta dauka awajen Anty zai kwana yau, gaisawa yayi da Hajiya Ummi ta kalleshi akunyace sabida Hajiya dake wajen tace "sannu da zuwa Baban Amali" dan kallonta yayi yasakin mata good smile yace "me kika dafamin am hungry?" Tashi tayi tawuce kitchen din Hajiya, Hajiya dake kallonshi tace "yamai jikin?" Ahankali yace "dasauki gobe zansa driver ki yakaisu suje su kwana jibi su dawo, gata dasafe zamu wuce Abuja dukanmu" gyadamaikai Hajiya tayi tace "Allah kaimu, shima yaron nan dake neman auren Meena ai katuna gobe zaizo yaganka ko"? Anatse yace "natuna Hajiya Allah kaimu" abinci Ummi takawomai yaci yayi damm sannan yawuce masallaci bai dawo gidanba sai around 9, dakin Hajiya yawuce yamata saida safe sannan yawuce side dinshi Ummi na zaune tana duba wasu books yashigo da sauri tasaki books din ta tashi dagudu tai wajenshi murmushi yayi yace "ammata na" ahankali tace "an samari na" murmushi yayi yadagata suka wuce kujera suka zube lamo tayi ajikinshi ahankali tace "na dauka awajen Anty zaka kwana"? Remote yadauka yashiga kunna tv irin wanda bayason maganan nan yace "anan zan kwana"

lurada yanayinshi datayi yasa bata kara cewa komiba daura idanunshi yayi cikin nata yace "kallon fa wawatsula kikeso?" Wani irin murmushi Ummi tayi tun ranan data gayamai kalman yarike gam yake fadi, kannemai idanu tayi tana lashe baki ahankali tace "ni gwaguyanka nakeso nayi" ohhh shi baimasan yanda zai misalta abinba but kobaiso dazaran Ummi tamai batsa sai jikinshi yatashi bakinta ya shafa idanunshi na kankancewa yace "menene kuma gwaguya baby" sauka tayi daga kan jikinshi takai hannunta kan idanunshi tace "rufe idanunka kagani" kulle idanunshi yayi kawai tai kneeling agabanshi tasa hannunta ta daga riganshi sama tana kwance mazariyan wandon yadin jikinshi hmmmmm…
Saida Ummi takusan sakashi sakin mata fitsari abaki anan falo suka watsewan su.
**
Washe gari around 11 nasafe Nura yasa driver Hajiya yakai yaran gidansu Hadiza.
Jibin daya fadi jibin akaje daukosu suka dawo da tsaraba sosai washe gari suka wuce Abuja.
Ummi kusan mutuwan tsaye tayi ganin durmemen gidan dasuka koma manya manyan flat daban daban guda uku ne komi iri daya, saida yafara shiga da ita ko'ina sannan yakaita second flat din inda yazuba mata furnitures naban mamaki a akwati saiti 16 jere a tsakiyan babban falon sai kawai Ummi tahau kuka dasauri yaran sukahau tambayanta menene shima Nura ma haka dago rinanun idanunta tayi takalleshi tace "ko amafarki bantaba tunanin zanyi rayuwa a irin wannan gidanba, kamin komi kuma, ga akwatina kaman wata yar sarki" murmushi yamata yace "kına kuka agaban su Amali, Amalili look at Anty Ummi is crying let's make her smile" sai kawai yama Ummi chakulkuli suma yaran sukahau mata tahau dariya sosai daganan suka wuce sama 4rooms ne asama ga masters bedroom nashi ga nata ga wasu dakuna biyu dayace anan su Amal zasu zauna daganan shida Aman suka wuce mosque dudda baya nuna mata komi but shigowanta gidan nan yakara tabbatar mata da Anty batanan duksai taji tadamu hankalinta yaki natsuwa sauka tayi itada Amali suka tafi kitchen kunga kitchen Ummi kawai tasaki baki suka kara fitowa waje wow gidan yahadu babban gaske yayi wani karamin kauye girma.

Damuwa tama Hadiza yawa taki kwaso kayanta daga Abuja tasake dagewa da addu'a da sallan dare, tanason taje tasami Hajiya but batasan taya zata mata magana ba yau ne the second time datake kara nadaman rashin shirinta da kannen mijinta, ijiyan zuciya ta sauke ta dauki wayanta tareda dialing number Ya Aisha amman harya katse bata daga ba sauran biyu takira basu dagaba, saikuma kaman bazata iyaba taciro number Meena tai dialing shima harya katse bata dagaba kawai saitaji hawaye sun zubomata dasauri ta sharesu ta ijiye wayan ta buga tagumi tai shiruuuu tafara tunani zaka iya kai downgrading yan uwan mijinka kana ganinsu kaman bakomi ba sabida mijinki na sonka but the truth is kowa nada rananshi arayuwan nan always respect kowa ijiyan zuciya ta sauke kafin ahankali ta kwanta akasa kaman marainiya Mama tadade tsaye agaban dakin tasaga labule tana kallonta amman bata sani ba, tsakanin uwa da d'a sai Allah, Uwace aduniyan nan duk lalacewan danta tanason abinta haka, tafi kowa tausayin Hadiza da damuwa da damuwanta, shigowa dakin tayi ahankali ta zauna gece ta hakan yasa Hadiza ta dan dago kanta saikuma ta tashi zaune da wuri takalli Mama, hannu Mama takai takama kuncinta tace "Hadiza na kin ganki kuwa? Kaman bake ba kashe kanki zakiyi ne dukkin rame saikace wacce kanjamau ki kama kinyi duhu, baki iyacin abinci, menene Hadiza? Ki hakura da Nura mana tunda shi ya hakura dake? Allah zai baki wani mijin daya fi zama miki

Alkhairi” dan lumshe idanu Hadiza tayi cikin sansanyan murya tace “Mamaa” saikuma kawai tafashe da kuka Mama tadade tana kallonta kafin kawai ta mike hijabin Hadizan ta dauka da car key dinta da aka kawo mata daga abujan dan dama a plazan shagonta tai parking motan tadauki wayanta duka tamika mata dasauri Hadiza dake kallon Mama tana kuka tace “Mama mezanyi dasu?” Ahankali Mama tace “tashi kije wajen Hajiya go and amend mistakes naki Hadiza” Shiru Hadiza tayi tana kallon Mama saikuma cikin wani kalan muryan ban tausayi tace “idan takoreni fa” ahankali Mama tace “tashi kije kozata koreki bakomi ta isa ne but ki sauke nauyin dakikejin nan azuciyanki and asked her for sincere forgiveness ba irin wanda kikayi a asibiti ba, kinji don’t be scared tashi kije Allah zai dauraki akanta zan miki addu’a” Hadiza kaman tayi mutuwan zaune saikuma ta tashi ta karbi Hijabin tasaka ta karbi wayanta tawuce tafita.
Parking Hadiza tayi awajen gidan tadade zaune cikin mota sannan tabude kofa tafito jikinta duk yay sanyi kaman kankara dan batasan mezataje ta tarar ba tawuce tashiga gidan, matan datagani tsakar gida ta gaida tana tambayan ko Hajiya na nan aka cemata eh tawuce ciki sallama tayi agaban dakin daga ciki muryan wata mata ta amsa tace “shigo” ahankali Hadiza tacire takalmi tashiga ciki Hajiya tagani zaune kan kujera tareda wata mata wacce ita ta amsa sallaman tana nunama Hajiya wasu kaya da aka kawo ido cikin ido Hadiza tayi da Hajiya da sauri ta sauke kanta kasa matan tace “bismillah zoki zauna” wucewa Hadiza tayi tasami waje ta sauna akasa matan tace “bari naje Hajiya” Hajiya tace “to Salamatu ayi amfanida rabi kada ki manta” matan tace “to” tawuce tafita dakin yarage daga Hadiza sai Hajiya, ahankali Hadiza da kanta ke kasa tace “ina yini Hajiya” Kai tsaye Hajiya tace “lafiya lau Hadiza ya jikin naki? Naso zuwa dubaki amman kinsan kafan nawa maneji ne saisa, Allah yasa mai ceton ku ne sannu sannu”.

💫MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE3️⃣8️⃣

Why are you cheating on your husband?? “Sabida baya gamsar dani! Sabida yanada karamin gaba! Sabida he’s not romantic! Sabida baya bani kudi am suffering to feed our kids!”.

Why are you cheating on your wife?? “Sabida tabude dayawa! Sabida bata iya kwanciya agado ba! Sabida she’s local batasan wassup ba! Sabida bata gayu! Sabida auren hadi ne! Sabida bata daukan bukatu na!!!”
Kunsan this are the common reasons din da ma’aurata kebadawa na cheating???
Subscribe with 1k and read to learn chat me up now!!
wa.me/+2347012181461

38
Dan kallonta Hajiya tayi ganin yanda kanta ke kasa yasa tace “tashi ki dauko ruwa da drink a fridge ki debo duk abinda kikeso a kitchen ni kadaine Meena batanan” girgizama Hajiya kai Hadiza tayi baki tabude zatai magana saita kasa Hajiya duk tana lurada ita amman tai shiru ta maida kanta kan tv, cikin wata kalan murya dake breaking Hadiza tace “Hajiya bansan ta ina zan faraba, yau kalamai sunyi karanci abakina dazan hada nabaki hakuri bisa kuskuren danamiki abaya” yadanyi shiru sabida muryanta was shaking sosai tace “Hajiya nasan nayi abubuwa da dama dasukasa kika tsaneni harda su Ya Aisha ma I called all of them dan nabasu hakuri harda Meena babu wanda yadauki wayana I understand no one wants me, Hajiya dan girman Allah dan darajan Allah Hajiya kiyakuri ki yafemin kuyafemin dukanku gabaki daya Haji…….” Sai kawai kuka ya kufcemata Hajiya tai shiru tazuba mata idanu dukta lalace kaman ba Hadiza ba, tabama Hajiya tausayi dan she’s a mother babu abinda kecin mutum kaman guilt din yama wasu laifi basu yafemai ba dan gyaran murya tayi anatse dan ba kwana kwana tace “stop crying Hadiza ya isa Allah ya yafemana Hadiza gabaki daya wlh har raina nayafe miki, su Aisha baki musu komi ba wayan nan, Nura ma inamai tabbatar miki shima ya yafemiki” Hajiya tadanyi shiru tana kallonta har ranta din tayafemata tace “amman Hadiza bazan miki karyaba banma d’ana sha’awan aurenki har abada!” Dasauri Hadiza yadago rinannyn idanunta tana kallon Hajiya data gyadamata kai tace “Mun yafe miki kuma bamu rikeki araiba, an riga an zama daya yanzu Hadiza kin haifamana yara so har lahira ana tare, amman dai babu zancen aure tsakaninki da d’ana yanda kikeson Aman da Amal yanda kikasan darajan su ki kasan zafin haihuwansu haka nasan na nawa dan, koda kin chanza hali Hadiza wasu tabon basa goguwa dan haka kitashi kije amman idan zancen yafiyane wlh tallahi mun yafemiki, yaranki kuma idan sukai Hutu zaa dinga kawo miki su idan kinason ki gansu call me ko wani cikinmu za’a kawo miki su” hade hannayenta Hadiza tayi dagudu zuciyanta har mata yakeyi kaman zai katse tazo gaban Hajiya tana kuka sosai tace “Hajiya ki rufamin asiri, Hajiya Nura kadai nakeso arayuwana dashi kadai zan iya zaman aure” Dasauri Hajiya tace “d’ana yahakura dake Hadiza, please mubar maganan nan tashi kitafi akwai mutane a tsakar gidan nan kar aji muryanshi a shigo adauka wani abune tashi kitafi” Hajiya tai maganan tana dafa kujera tana yunkurin tashi kama kafan Hajiya Hadiza tayi tace “Hajiya kiji tausayina ki kalleni amatsayin yarki” Dasauri Hajiya ta nuna Hadiza da hannu tace “kul! Karki sake ki kwatanta yarana dake sabida nabasu tarbiyan da sunsan banbancin matsayin namiji da mace! Kap yarana mata mazajensu ne jagororin su! Yarana bazasu taba yima mazajensu kazafi ba har abada wlh inaaaa! Basasu taba yima masajensu tabon dahar abada bazai bar sunan su ba! You have no idea kotun da shairin dakikama Nura yayi affecting nashi da business nashi kinsan investors nawa ya rasa? Sakenmini kafa!” Hajiya tamata tsawa dan batason tuna abubuwan da Nura yagayamata ya sameshi daya koma Abuja kwanakin baya, ahankali Hadiza tasaki kadan Hajiya idanunta sunyi jazur Hajiya tace “wallahi na yafe miki Hadiza kinji namiki rantsuwa hakama Nura ai ko darajan yaranki yakai mu yafemiki amman I will tell you this to your face dan bazan miki karyaba ko in yaudareki ko amafarki, ko amafarki Hadiza banama d’ana kwadayin ki kuma, sai anjima” Hajiya tawuce dakinta ahankali tareda maido kofa tarufe.
Hadiza tai kuka tai kuka awajen na. Harta godema Allah takai almost 30min sannan ta tashi da kyar tawuce ta tafi bata damu da mutanen dake tsakar gidan ba haka tawuce, Hajiya tadade gaban dakin tanajin kukan Hadiza dake tabata kafin ahankali takoma bakin gado ta zauna tai

shiru saida taji tafiyan Hadizan sannan tasauke ijiyan zuciya wayanta tadauka ahankali tai dialing number Nura.

Ringing daya ya katse yakirata back ya gaidata cikin tattausan muryan irin conversation na d'a da mahaifiyarsa Hajiya tace "yanzu Hadiza tabar gidan nan" dan shiru Nura yayi baice komiba, ahankali Hajiya tace "tazo tabani hakuri kan komi dayafaru tama kira su Aisha wai tabasu hakuri amman duk basu dauka ba, Nura duk ta lalace" "umm" was the only thing daya fito daga bakin Nura dan shiru Hajiya tayi sai chan tace "Son I know nidakai we had this conversation before, nasan abubuwan da Hadiza tamaka hurt me deeply, and I support you dakace bazaka kara zaman aure da ita ba but I looked into her eyes today Nura I saw sincere nadama, wlh danasani ne cike tap a idanunta, koda naji haushi ina fushi da ita the decision is still yours Nura, kanason Hadiza ko baka sonta yanzu tell me the truth Nurudeen" dan shiru Nura yayi tareda lumshe idanunshi ya jinginar da kanshi jikin kujeran office din, kaman bazaiyi magana ba ahankali yace "I will always love Hadiza Hajiya, but har cikin raina nahakura da ita kaman yanda na fadamiki ranan, nabude new chapter in my life, na yafemata, I've moved on, bazan iya cigaba da zama da itaba anytime na kalleta I will remember itane the first person data taba zagina kala kala aduniya, the first matan data chakumeni, tamin kazafi tamin kotu, akwai somethings aduniya dahar kamutu kanaso but u will never get them sabida wasu dalilai I think Hadiza is just one, Hajiya inason Hadiza sabida bani nadaurama kaina son ba Allah ne shi kadai zai iya cire mini, but nahakura da ita har abada, please Hajiya kada ki karamin maganan ta"
Ijiyan zuciya Hajiya tasauke tace "shikenan Nura, remember this kome kakeso I will always support you, all I want is inganka living peacefully and happily" anatse yace "Ummi is giving me that Hajiya, Ummi is the biggest gift in my life, yarinyar nan is just God sent, Hajiya she loves me unconditionally, duk abinda nakeso itama tanaso, she loves my children, zan biyamana aikin hajjin bana ma dukanmu mutafi harda ke Hajiya" murmushi tayi tace "Allah ya amsa, Allah yakaimu lokacin, Allah yabata yara itama" ahankali Nura yace "Ameen" cikeda so Hajiya tace "cigaba da aikin ka bari nadan kwanta" sallama sukayi daidai wayan Nuran na ringing yaga Baby dasauri ya dauka muryan Ummi yaji tana magana da kyar tana numfashi kaman wacce take kokawa tai numfashin da kyar tace "Da…….dyn Amal……" dip yaji shiru ga wayan na connecting dasauri ya mike yana "Baby, Ummi, Ummi" key mota kawai yadauka dasauri yashiga kiranta but ba'a dagawa 15mij yakaishi gidanshi yatafi side din Ummi aguje, yana bude kofa wani kamshin turaren wuta ya daki hancinshi, falon fess fess an gyara, sama yawuce yabude dakinta bata ciki shima agyare dakinshi yawuce kwance yaganta akan tile ga mop ga roban mop dudda ba ruwa akasa amman kaman zamiyewa tayi tafadi, tana nishi da kyar a sandare, dawani kalan gudu yayi wajen yadagota kadan kadan idanunta ke budewa arude yace "Ummi, what happen to you my baby?" Kallonshi takeyi but takasa magana sai hawaye dake bin gefen idanunta arude yashiga duddubata ganin kafafunta basa moving harta yatsunta ma, kawai ta sassandare kaman ice block yasa yaji gabanshi yadan fadi sai kawai yadauketa da sauri yakai mota yaja sai hospital aka shiga da ita ciki kusan 1hr yayi zaune Dr yafito suka wuce office nashi, Dr yabama Nura hannu yace "let's start da good news your wife is 3month pregnant" dasauri Nura ya kalli Dr jikinshi har rawa rawa yake da mugun mugun mamaki yace "Dr wasa kakemin ne ko da gaske kake Ummi is pregnant"? Dr ya gyadamai kai yana murmushi hannu biyu Nura yadaura kan fuskanshi yace "Alhamdulillah, Alhamdulilah, Ya Allah thank you, Ya

Allah nagode maka” he is seriously happy kaman zaiyi kuka, chan ya kalli Dr dake kallonshi yace “what’s the bad news Dr”? yayi maganan gabanshi na faduwa dum dum dum, ijiyan zuciya Dr yasauke yace “matarka is suffering from a very very rare disease, though bansan past medical history nata ba kota taba haihuwa” dasauri Nura yace “ta tabayi sort of sha she lost the baby at 6month hartai fama da yoyon fitsari” Dr yace “wow this information will go a long way it will help with investigation din dazamu mata” Dasauri Nura kirjinshi na dukan uku uku yace “to what’s wrong with my wife Dr? Lafiyanta kalau fa natafi office kaman faduwa tayi tana moping” ahankali Dr yace “I don’t think faduwa tayi datana moping, I mean she slipped and fall due to the watery ground I don’t think that’s the case here, your wife is suffering from HYPOKALEMIC PARALYSIS!” Wani kalan mikewa tsaye Nura yayi the only abinda ya gane a kalman is paralysis wato paralyze shiba science student bane amman kawai jikinshi saiyahau rawa kaman ba namiji ba da sauri Dr yatashi tareda kamashi yace “Alhaji Nura calm down is not abinda kake tunani zauna dan Allah calm down” idan kaga idanun Nura zaka tsorata yace “tell me Dr meya sami Ummi banni kawai ahakan am fine, tell me” yafadi maganan a hargitse, ahankali Dr yace “hypokalemic paralysis during pregnancy condition ne da bai cıka kama mata masu ciki ba, ba lallai nata yazama genetic ba sabida ciki yakawo mata halan, saimun gama investigation zamuyi ruling out”

but amman condition din dake sanya numbness, weakness na muscles, nata akafane yanzu haka two legs dinta are paralyze which zamu fara treatment immediately once result are out, yawancin abinda ke jawowa mata masu ciki condition din nan is low pottasuim level, paralysis ba abu mai kyau bane gabaki dayanta wajen mai ciki, so just pray for her to get through this inba hakaba gabaki dayan 9month pregnancy dinnan a wheelchair zata yishi dan she will not be able to use her legs, sabida ko zatai amfani da kafan maybe tafara tafiya bazatasan lokacin da kawai kafafun zasuyi sanyi su daina aiki ba, hopefully bazaiyi spreading zuwa hannuwanta ba for now she can’t feel her legs, maybe kuma ciwon is related to abinda yasameta a first child nata so contact the hospital din dasukai managing nata lokacin su bamu medical history nata, it will help alot sabida musan menene complications datai having a first pregnancy dinta” baya Nura yayi dasauri Dr ya tareshi, ijiyan zuciya yasauke yashiga tattaba kujera kaman makaho yazauna akai da nata ya buga tagumi, ahankali yace “agida ta haihu, magungunan datasha ma alokacin na gida ne bana hospital ba, ba’a kaita hospital ba alokacin, Dr kall…….” Nura yayi shiru idanunshi sun cika da hawaye saikuma yakai duka hannayenshi biyu yakama hannun Dr yace “Dr you see that woman Ummi, my Ummi” yanuna kanshi yace “she’s all I got, she takes care of me, my mother, my kids my entire family, Ummi is just like my back born” yayi shiruuu saikuma yasaki hannun Dr yaki hannayenshi kan idanunshi yace “bantaba ganin a selfless human like Ummi ba, her heart is filled with love, peace and harmony, she loves kowa da zuciya daya, she don’t have a Mom nor Dad, itane first born, tanada 2 sisters, her grandmother look up to her, her sisters look up to her, my kids look up to her, my Mom and even me, ko sauro banso ya ciji Ummi sabida mutumce ita mai kashemana sauro idan yazo zai cijemu, how can I be here ina kallon Ummi tana paralyze eh Doctor”? Nura yayi maganan yana zaro handky da sauri daga aljihun shi, yakai kan idanunshi dasauri ya goge yace “Dr please help me, I don’t know do everything, idanma akwai hospital that are specialize in managing condition nata ko a outside

Nigeria ne am willing to take her there I can’t stand watching Ummi na in pains, I can’t!” Nura yayi maganan gwanin ban tausayi.

💫 MATAN?? Ko MAZAN??💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE 3️⃣9️⃣

LABARIN FEMINIZM IS COMING TO AN END, CHAPTER2 IS AN ENTIRE DIFFERENT STORY ABOUT CHEATING🧡 KINDLY MAKE YOUR PAYMENT NA 1k and chat me up by clicking on this link;
wa.me/+2347012181461

You can make payment 1k here 👇🏼

3107021073 Aisha Muhammad first bank
KO

6353995766 M Shakur world Moniepoint
Send evidence of payment I will add you to chapter 2 group.

39

Dafa kafadanshi Dr yayi yadan matse anatse yace “you have to be strong for her Nura, Ummi will be fine trust me, pray ciki yakawo mata ciwon idan shine tana haihuwa she will be fine just that dole ayi monitoring nata sosai da special kulawa, you can’t breakdown like this you have to be strong kanajina” Dr yadan jijiga kafadan Nura dake kallonshi kaman hoto, ahankali Dr yace “pull yourself together katashi muje” Nura yadade zaune awaje kafin yayi taking wani long breathe saikuma yahada hannayenshi yayi addu’a da kawai saiyaji yasami natsuwa wato Allah is just the best comforter, tashi yayi tsaye yakalli Dr yace “am ready” gyadamai kai Dr yayi yace “let’s go” wucewa sukayi suka fice tare zuwa private room da akai admiting Ummi tana kwance an mata fixing drip tana bacci, sosai Nura ke kallon fuskanta gaban gadon Dr yaje inda kafafun Ummi suke yasa hannunshi gaban riganshi ya cire pen dinshi yakai tafin kafan Ummi ya sosa but batai motsi ba tattaba kafafun yayi duk Nura na kallo batai motsi ba sannan yazo inda Nura yake yana kallonshi kaman gunki murya chan kasa yace “I assure you everything is gonna be fine okay, bari naje naji how far da lab investigation danace ayi” gyadamai kai Nura yayi yawuce yafita daga dakin ahankali Nura yaja kujeran gaban gadon ya zauna tareda kai hannunshi

yakama hannun Ummi ahankali yadaga yana kallon fuskanta yakai kan bakinshi ya manna ma kiss saikuma ya kwantar da fuskanshi kan hannun nata yana kallonta ahankali yace “you are not alone Ummi, we will get through this together, you have to fight for me, for our baby” yakai dayan hannunshi yadaura kan cikinta yace “for our baby” yadan lumshe idanu yace “for Aman and Amali, for Gwaggo and su Shatu, for Hajiya and all my family Ummi, you are a strong girl fight kinji” yay maganan yana mammanna ma hannunta kiss kaman zai hadiye, ahankali Ummi ke bude idanunta kanta yamata nauyi tana kokarin tuna abinda yasameta tasan tagama gyaran falo tazo sama ta gyagyara tana dakin Baban Amali shima ta gyara tana cikin moping taji kafafunta sun rike sai chan sukai sanyi kaman kankara kawai taji tazube dudda tai kokarin tafadi kan hadi but takasa motsi da kafafun at all tadau waya daganan batasan meya faruba tasss tabude idanunta takalli saman dakin, dumi dataji da lema lema a hannunta yasa tadan juyoda kanta gefe Nura tagani zaune yakama hannunta ya rungume gamgam a fuskanshi ya lumshe idanunshi hawaye suna gangarowa ahankali suna zuba saman hannunta faduwa gabanta yayi dasauri tabude bakinta gabaki daya batada karfi takeji kaman an kashe mata jiki tace “Baban Amali” dasauri Nura yabude idanunshi yakai hannunshi dasauri yana share fuskanshi yakalleta tareda mikewa yana shafa mata fuska cikeda so yace “Baby na kin farka” gabanta na faduwa sosai ita bawai ciwon ko asibitin dataganta viki ke damunta ba no kukan dataga yanayi cikin saryin murya tace “meya sameka kake kuka”? Dan zaro idanu yayi ganin yanda take kallonshi hankalinta tashe kuma yasan dan raga hawaye a idanunshi ne yasa yadanja hancinta yace “common da girmana zanyi kuka saikace ke, I think idanuna ke ciwo nagama da nan zanje office na likitan idanu yadubani” bata taba karyata shi ba so she believe cikeda so tace “sannu muga idanun wani abu ya shiga cikine” tai maganan tana daura hannayenta and kan fuskanshi zata budemai idanu dasauri yakama hannayen yace “I am fine, meya sameki ya akayi kika fadi?” Dan kallonshi tayi ahankali tace “ina moping daki shine kawai naji kafafuna sun daina aiki sun dawo kaman kankara daya daskare gabaki daya ina kokarin najasu naje kan gadoma nakasa shine na zube, kaman nakiraka ko?” Gyadamata kai yayi ya manna mata kiss a goshi yace “don’t worry kafanshi will be fine okay” gyadamai kai tayi takalli kafan sannan takalleshi tace “har yanzu kaman daskararren kankara sukemin” tashi yayi saiyazo wajen kafan ya nunasu da yatsa yana daure fuska yace “ku kafafun Ummi me kuka damun mini mata”? Wani kalan murmushi Ummi tayi tana kallonshi, ganin tai murmushi yace “idan baku barta ba zaku gamu da fushin Noor din Ummi tom” for the first time ta kyalkyace da dariya tace “kafafu kuce munji Dadyn Amali” Dan dariya shima Nura yayi yadawo gadon yazo gefenta ya zauna yana kallon fuskanta yace “nabaki good news”? Dasauri ta gyadamai kai tace “eh” murmushi yamata hannunshi ahankali yakai yadaga riganta sama yakalli flat tummy dinta ahankali yasa hannunshi yakamo nata yadaura akan cikin kafin yasa nashi akai yakalli fuskanta yanda take zaro idanu tana kallonshi takosa yafadi abinda zai fadi ahankali yace “nan da wata shidda Babyn mu zaizo duniya” dasauri Ummi takara zaro idanu tana kallonshi bakinta na rawa sosai, tanason tai magana ma takasa Nura yace “kina dauke da cikin 3months Ummi, my baby na cikin cikinki” fashewa Ummi tayi da kuka tana dariya arayuwan ta tana son yara kodan babynta na farko yakutu ne oho but tanason yara cikin yakara kankamewa da hannun Nura tace “babyn ka, Babyna, babyn mu?” Gyadamata kai yayi yace “yes Ummi” dariya tafashe da shi sosai hawaye na fitowa daga idanunta suna ahaka akai knocking dakin hakan yasa yazare hannunshi tareda rufe mata cikin daidai Dr na bude kofa yakalli Nura yace “come with me Nura” ganin Ummi ta

farka yasa yashigo yace “Madam kin tashi ya jikin?” Ummi na murmushi sosai tace “lpy lau” Nura Dr yakala alamun yabiyoshi Nura yakalleta yace “bari naje nazo” gyadamai kai tayi kaman yar baby, Office suka shiga Dr yace “some of her lab results are out” dan faduwa gaban Nura yayi yakalli Dr dake dube dube, sai chan yayi shiru tareda ijiye file din yashiga typing a computer shi yayi printing wani paper yadauka tareda bawa Nura dake kallonshi yace “Nura we have to start treatment na matan ka immediately, zamu riketa a hospital for as long as needed ni karan kaina bazan iya gayamaka ga randa zamu sallameta ba, paralysis nata is spreading yanzu yakai cinyanta, before dakika shigo it was below knees nata, kaje pharmacy get all this including pampers na manya” dasauri Nura yakalli Dr, ahankali Dr yace “yes, we will not risk tana tashi for anything ba, Nura anything dazaisa Ummi tafadi can kill Babyn datake dauke dashi so she needs good management, the good news is I don’t think is genetic though munakan bincike har yanzu but ciki ne yasamata abin zai iya tafiya any moment idan kuma bai bartaba dazaran ta haihu zai saketa” Dr yadan sauke ijiyan zuciya ahankali yace “do you want me to tell her abinda ke damunta ko na barka kayi?” Kasa magana Nura yayi Dr yace “bamason anything dazaisa BP ta yayi raising dazaran hakan yafaru zai bata mana komi it will worsen this paralysis wlh, she needs kwanciyan hankali, zaka iya ka sanar da ita batare daka dagamata hankali ba ko ni namaka?” Ijiyan zuciya Nura yasauke kafin ahankali yace “zan sanar da ita” gyadamai kai Dr yayi yace “get everything ka sanar da ita nabaka 1hr, calm her down everything zamuzo mufara treatment” gyadamai kai Nura yayi yatashi yaje pharmacy yasayo komi kasa karban kayan yayi yace “su rikemai yana zuwa yawuce motanshi ya şairi ya shiga ya zauna tareda kunna motan ya kunna ma kanshi AC” wayanshi yaciro dasauri yaciro number Hajiya he just needs energy shima ringing daya Hajiya tadaga tace “Nura” cikin wani kalan weak voice yace “Hajiya” muryanshi kadai taji tasan ba lafiya ahankali tace “menene Nura why do you sound down” Dan lumshe idanu yayi ahankali yace “Ummi” faduwa gaban Hajiya yayi dasauri tace “what happen to Ummi”? Da kyar Nura ya iya ya gayama Hajiya komi, cikeda hikima irin na manya Hajiya tace “it’s okay Nura calm down ciki babu kalan abinda baya sanya ma mace, you have to be strong for her kaji, kaje ka sanar da ita kadena bata lokaci anjima zamuyi magana da kyau, tashi kaje yarona Allah maka Albarak, Allah bama Ummi lpy” katse wayan yayi yawuce ciki komi yawuce dakin dashi nesa da Ummi ya ijiye kayan daketa kallonshi kawai jitayi gabanta na faduwa dudda he’s smiling but body language nashi na gayamata wani abu, tanada this connection da Nura whenever he’s happy she senses it hakama whenever he’s sad, dawowa yayi bakin gadon ya zauna yace “yammata na” murmushi tamai takama hannunshi tarike anatse tace “meke damuna?” Kaman daga sama yaji tambayan sai kawai yaksa magana kaman an rikemai baki, Ummi na kallon kwayan idanunshi tace “banda Babyn mu inada wata cuta ajiki ko?” Kasa magana still Nura yayi, hawaye ne masu dumi suka sauko daga idanunta ganin yaki magana, dan lumshe idanunta tayi sannan tabudesu tareda sauke ijiyan zuciya takai hannunta ta share fuskanta tass sannan tai murmushi takai hannyenshi data rike tadaura kan kumatunta taji wani sanyi har ranta takalli fuskanshi ahankali tace “mutuwa zanyi ko Baban Amali!” Dawani kalan sauri Nura ya fizge hannunshi daga kan fuskanta yasauka daga gado yamike tsaye yace “noooo!” Fashewa da kuka Ummi tayi mai tsuma zuciya tace “ni naji ajikina mutuwa zanyi, alamomin zare rai daga jikin dan adam shine akashe wanan gaban akashe wancen gaban har a idasa zare ran, dafarko ai kafafuna ne sukai sanyi yanzu har cinyana bana jinsu kwata kwata kaman ba’a hallici wajen ba ajikina haka nikeji, mutuwa zanyi

